[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: https://chat.whatsapp.com/FJaq7XfYWaNBTOmSzv7tqa

TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

001.

*Dukkan Godiya da yabo sun tabbata ga Allah maɗaukakin sarki. Tsira da amincin ALLAH su ƙara tabbata ga Shugabanmu Annabi Muhammad {S.A.W} ina godiya ga ALLAH maɗaukakin sarki da ya bani ikon rubuta wannan littafi, mai suna TAREEQ IMAM ubangiji ya sanya ƴan uwa musulmi su amfana da faɗakarwa da ke cikinsa, kuskuren da ke ciki kuma ubangiji ya yafe min*

Matasan samari ne su uku ke tafiya kowanne su yana sanye da kayan ƙwallo sky blue in colour ga baki ɗayansu jikinsu jiƙe yake da gumi, alamar da ke nuna daga filin ƙwallon ƙafa suka fito. Shekarun su na haihuwa ba za su gaza 14-15 ba. Tun daga nesa kake ji tashin muryoyin su suna tafe suna firar yadda team ɗinsu yai nasarar lashe gasar da suka yi a yammacin yau. Ɗaya daga cikinsu wanda ya kasance a tsakiya kuma shine gajere a cikinsu ya kalli na gefen hagunsa ya ce.

"Slugger ga fa mutuniyarka can ta dawo daga islamiyya da alama hango mu da tayi ne yasaka ta ƙara sauri."

Ya ƙarasa magana tare da pointing inda ya hango ƴar matashiyar budurwa ke tafiya cikin sauri jikinta sanye da uniform ɗin Islamiyya.

Murmushin mugunta wanda aka kira da suna Slugger ya yi har yana haɗawa da shafa sumar kansa wacce ya yiwa wani irin kalar ɗan iskan haircut, da ƙarfi ya shiga kwalla mata kira.

"Ke Nana zo nan! kina jina fa ki tsaya nace."

Ko juyowa Nana bata yi ba balle yasa ran za ta amsa mai sai ma ƙara saurin da tayi wanda har da ɗan gudu-gudu ta haɗa.

Gani haka yasa ya bi ta da mugun gudu dama shi gudu ba wuya yake mai ba tana gaf da isa gate ɗin gidansu ya cimmata, da ƙarfi ya cafko purple hijab ɗinta ya yi mugun jawo wuyanta da ƙarfi ya yi baya yayin da wuyan hijab ɗin ya yage a ƙoƙarin kwatar kanta da take yi. Hannunta na

hagu ya damƙe cikin nasa shiyasa ya saki yagagge hijabinta.Ya shiga ja ta da ƙarfi ita kuma tana tirjewa a fusace ta ce

"Wai me na tare maka ne a rayuwa Tareeq da duk sanda muka hadu sai ka ci zarafina?"

Tai magana cikin rawar murya wacce ke nuna kowanne lokaci za ta iya fashewa da kuka.

"Ubanki kika yi min shegiya baƙar munafuka wato ke har kin manta abin da kika yi min ɗazu a school kina zaton kin ci bulus ko?"

"Ni fa ba wani mummunan abu nace akanka ba kawai dai na faɗawa Uncle Joel ne ya shiga tsakanina da kai kadaina taɓa min jiki saboda ni ba 'yar iska bace..

"Dallah rufewa mutane shegen bakinki mai mugun ɗoyi tsiya to da kika kai faɗawa Uncle Joel uba na ne shi da zai sa na fasa yi miki abin da zuciyata ta raya min?"

"Ba ubanka bane ba amma ai kana tsoronsa."

Nana ta faɗa cikin tsiwa, har tana murguda baki.

"Iyeee! lallai slugger ka yi sake yarinyar nan ta gama rena ka. Na rantse da Allah da nine ta ke gayawa haka da tuni na gaggaurawa shegiya maruka, da bakinta zai juye ya koma keya."

Cewar Fahad wanda suke wa laƙabi da suna Rooney kuma shi ne wanda ya fara hango Nana.

"Kam bala'in nan! Nana ni kike kira ɗan iska?"

"Ban faɗa ba amma Tareeq abin da kake min miye bambanci ka da ɗan iska?"

Tana rufe baki yana ɗauke ta da mahaukaci mari a kumatunta na dama tana ɗagowa cikin ruɗewa ya sake dallawa ɗayan kumatunta, na hagu ga baki ɗaya Nana ruɗewa tai ta rasa inda za ta tsoma ranta saboda maruka sun ratsa ta ba kaɗan ba. Da ƙarfi ya finciko ta ya haɗa ta da jikin bangon gidansu yasa gwiwar hannunsa a maƙogwaronta ya danne yayin da yasa ɗayan hannunsa ya yiwa 'yan matasan boobs ɗinta baƙar damƙa ya dinga matsa su, da iyakaci ƙarfinsa yana luguiguita su wani irin tsananin azaba da ya ratsa ƙwaƙwalwar Nana yasa ta tsandara ihu sai dai ihu nata bai fita sosai ba, saboda maƙoshinta da ya dafe Rooney da Lil-prince sai kyalkyalar dariya suke yi su na kashewa.

"Ci mana ubanta ka matsi 'yan biyunta son ranka gobe ko gani wata tayi za ta kai ƙararka gun Uncle Joel da gudu za ta hana."

Lil-prince ya faɗa yana sheƙewa da dariyar mugunta.

Rooney ne ya karɓe zance ta hanyar cewa.

"Bar Shegiya yau zata koyi darasi, ba dai taƙamarta kai ƙarar BBT ba {Bad boys team} yau za ki yaba wa aya zaƙinta, shegiya mai idanuwa kamar na mujiya."

Wata mota ce baƙa wulik ƙirar Corolla new model 2023 tazo ta wuce su har tayi nisa sai gashi direban motar ya yi reverse ya dawo, hakan ne ya jawo hankalinsu har suka kalle mamallakin motar cikin sauri Lil-prince ya furta.

"Slugger sake ta zo mu tafi ga tsohon munafuki can na gidanku mai siffar ƴan daudu ya tsaya yana kallanmu...

Tun kafin Lil-prince ya dasa aya suka ji muryar Uncle Hamza yana faɗin

"Kai Tareeq uban me kake aikatawa ƴar mutane a jikin bango?"

Sakinta Tareeq ya yi ta durƙushe ƙasa tare da rushewa da matsanancin kuka, da sauri uncle Hamza ya ɓalle murfin mota ya fito.

"Me kayi wa ƴar mutane Tareeq?"

"Abin da idonka ya gane ma?"

Tareeq ya yi magana yana gallawa Uncle Hamza harara.

"Kai dai anyi mugun ɗan iskan yaro kai kenan kullum cikin ɗaukowa iyayenka magana.

Uncle Hamza ya faɗa tare da ɗago Nana wacce har yanzu take gunshaƙin kuka.

"Daɗin abin Iyayena na ɗaukowa ba na wani ƙato ɗa shan miyar gidanmu ba,kuma ubana yana da arzikin da komai girman laifin da na aikata zai tare min dan haka ka fita sabgata babu ruwanka dani."

Sosai furucin Tareeq ya ɓatawa Uncle Hamza rai wato shine ƙato ɗa shan miyar gidansu, lallai me hana yau ya cin uban yaro nan sai ALLAH. A fusace Uncle Hamza ya yi kan Tareeq ya shaƙe masa wuyan jersey har sai da idanunsa suka firfito, Nana tana gani haka ta kwasa da gudu ta shiga gida.

Da ƙarfi Lil-prince da Ronney suka shiga ɓamɓare hannun Uncle Hamza daga wuyan rigar Tareeq wanda dakyar yake iya numfashi. Yana sakinshi ya dinga tari idanunsa suka yi jajir sai dai bakinshi bai mutu ba sai maganganu banza yake fadawa uncle Hamza ɗin

"Da ku bar shi ya dake ni yau kwano tuwonshi ya ƙare a gidanmu, dama na gaji da gani wannan mummunar fuskar tasa mai saka min tashin zuciya."

Tareeq ya yi magana cikin fitsara da zallan rashin kunya.

Ronney da Lil-prince suka sheƙe da dariya tare da kashewa, cikin ƙonar zuciya Uncle Hamza ya zuba musu ido sai huci yake tsananin ɓacin rai yasa ya kasa magana kamar ba zai daina kallonsu ba. Sai kurum ya yi kwafa tare da girgiza kai ya juya da sauri ya shiga motarsa.

Cikin ɗaga murya Tareeq ya ce.

"Banza kawai ɗan maula lokaci na zuwa da zan kakkaɓe ka daga gidanmu wawa kawai mai warin bunsuru."

Duk abin da yake faɗa a kunne Uncle Hamza bai mayar mishi da martani ba ya ja motarsa ya nufi gida.

"Gaskiya slugger idan ba ka tashi tsaye akan guy ɗinan ba ka ci ubansa cin goriba, ba zai sakar ma mara kayi fitsari ba."

"Bar shi kawai Lil-prince lokaci nake jira wallahi-azim sai nai masa mummunan wulaƙancin da ko kare ba zai ci ba."

"Da kyau na wajena ni nasan BBT basa ɗaukar reni."

Ronney ya faɗa yana wani bubbuɗawa.

Tareeq ya cire rigar jikinshi ya ɗora a shoulder yana faɗar "Ba don jersey ɗinan favorite ɗina bace ALLAH da sai na cina mata wuta saboda kawai hannu ɗan shegiya nan ya taɓa ta."

Ya ƙarasa magana yana wani yatsine fuska, dariya su Lil-prince suka sa dai-dai sun iso gate ɗin gidansu Ronney shaking hands suka yi da wani salo mai nuna rashin jin su a fili tare da faɗar sai sun haɗu anjima. Gidanje huɗu ne tsakanin gidansu Ronney da na su Lil-prince gidansu Tareeq shine a ƙarshen layi, yana zuwa tangameme gate ɗin gidansu ya ja yai tsaye ya shiga knocking abin mamaki gate maigadi ya buɗe masa alhali ga ƙaramar ƙofa ya bi amma tsabar iskanci da ɗaukar magana irin nasa sai dai a buɗe masa gate a cewarshi ƙafafuwanshi sun fi kowa ce mota da ke gidan daraja da tsada, saboda haka dole maigadi ya dinga buɗe mai gate.

"Sannu da dawowa magajin Daddy."

"Yauwa Ɗan Bala kaima sannu da tsare mana ƙofar gida."

Tareeq ya faɗa yana ɗagawa Ɗan Bala hannu, yana zuwa ƙofar da za ta sada shi da main parlour kasancewar ƙofar ta gilashi ce wacce alburushi baya hudawa{bullet proof}da zarar an tura ta da ƙarfi ƙarar alarm zai karaɗe ilahirin gidan shiyasa ya fizge ta da ƙarfi ta yadda ƙararta zai isarwa da duk wanda ke cikin main parlour ɗin shigowar shi duk gidan shi kaɗai ne mai wannan ɗabi'a shi kuma yana yi ne saboda kowa ya kama kansa, gudun kada ka shiga gonarsa ya shuka ma rashin mutuncin.

Kyawawan 'yan mata su Uku ya tarar zaune cikin parlour ɗaya tana operating wayarta yayin da biyu ke kallon Big brother Naija yadda ya rufu ƙofar ne ya firgita su saboda kowacce ta shagala da abin da take yi kamar daga sama suka ji ƙarar duk dai in da sabo sun saba da iskancinsa kala daban-daban.

"Mtsss...!

Wacce ke operating ɗin waya tai tsaki.

"Innalillahi wa'inna illaihim raji'un."

Ɗaya daga cikin masu kallon big brother ta faɗa can ƙasan maƙoshinta.

"Annobar gida ya dawo."

Ɗayar ta faɗa tana mishi kallon sama da ƙasa tare da jan guntun tsaki.

Folding hannuwa ya yi yana sauraren abin da kowacce su ke faɗa.

Kwafa ya yi har ya ɗauki hanyar corridor da zai kai shi da ɗakinshi

Ya ji an sake ja mishi tsaki a fusace ya juyo ya sauke fusatattun idanuwanshi akan wacce yake kyautata zaton ita ce tai tsaki.

"Wacce Shegiya ce mai sha'awa kwanciyar gadon asibiti ke min tsaki?"

Ya tambaya yana wani zare idanuwa kamar yana yi da sa'anninshi.

"Wai nikam Tareeq har sai yaushe za ka fara girmama na gaba da kai ne?"

Daga bayan shi ya ji muryar Umminshi ta daki dodon kunnenshi.

Cikin kumbura baki ya ce.

"Ummi ko zan girmama na gaba dani bana tunani riɗa-riɗa ƴan matan gidanan za su sami haka daga gareni, kawai dai ina so ki shiga tsakanina da Ya Zainab ta daina shiga sabgata ina shigowa ta kira ni da annobar gida, ban tanka ta ba. Hakan bai ishe ta ba sai da ta sake yi min tsaki har sau biyu."

"Rufe min baki Tareeq kafin na tsinke ma mari Zainab ɗin ce zan shiga tsakaninka da ita ƴar uwarka ta jini kayi hauka ne Tareeq?"

Ya kwana da sani Ummi ba za ta taɓa bashi gaskiya koda shine da gaskiyar, shiyasa ya yi kwafa ya wuce zuwa ɗakinshi tun kafin ya ƙarasa shiga corridor ya ji Ummi tana ci gaba da masifa.

"Kai ma saboda ɗaukar magana yasa ka biyo ta cikin parlour nan bayan akwai ƙofar shiga ɗakinka ta waje fitinane yaro kawai da baya ƙaunar zaman lafiya."

Bai ce komai ba ya ƙarasa shigewa corridor ɗin tare da shan alwashin ko ba yau sai ya karyawa Ya Zainab ƙafa ko hannu tun lokaci da ya karyawa Ya Fadila hannu ta daina shiga sabgarsa tun da ya fahimci 'yan matan gidan nasu sai yana yi yana kakkarya su zasu daina shige mishi hanci.

Ummi ta juya ta koma kitchen dama tana cikin haɗa abincin dinner ta jiyo muryar Tareeq ɗin. Ko five minutes Ummi ba tayi ba da shiga kitchen ta ji Fadila tana kwalla mata kira, da sauri ta fito hannunta riƙe da ludayin miya. Nana da Mamarta ta gani tsakiyar parlour tsaye yayin da maman Nana sai cika take tana batsewa Nana kuma sai faman gunji kuka take.

"Subhanalillah! Nana Tareeq ne ko?"

Ummi ta faɗa sa'ili da ta iso kusa da Nana dan tasan duk duniya shi kadai ne za a kawo mata ƙarar sa, tasa hannu tana jujjuya fuskar Nana tana kallon shatin yatsun Tareeq dake shimfiɗe raɗau akan manyan kumatunta.

Cikin sanyi jiki Ummi ta ɗago ta dubi maman Nana ta ce.

"Dan ALLAH maman Nana kiyi haƙuri tabbas ɗan yau ne ka haife shi ba ka haifi halinshi ba...

"Dallah Maman Fadila ya isa haka maganar ta gaskiya nagaji da cin kashin da Tareeq ke wa Nana, fissibilillahi ace iskancin shi ya tashi daga tsagwama da dukanta da yake yi ya koma taɓa mata nonuwa to wallahi ki sani ba zan lamunci ya ɓata min tarbiyyar 'ya ba. muddin ya sake taɓa ta hukuma ce za ta shiga tsakaninsu ina dalili yaro ya fitine mutane unguwa."

"Innalillahi wa'inna illaihim raji'un! Nana Tareeq ne ya taɓa miki nono?"

Ummi ta faɗa cikin zallar firgici da tashin hankali.

"Eh! Ummi bama sau ɗaya ba ko yau a school ya ritsa ni a bathroom ya taɓa sai na kai ƙararshi wurin schoolteacher ɗinmu ya dake shi. Shine yanzu na dawo daga islamiyya su ka sake tare ni shi da abokanshi yai min mari biyu ya kuma sake taɓawa. ALLAH ya taimake ni sai ga Uncle Hamza na nan gidan ya kwace ni a hannunshi da ALLAH ne ƙadai yasan iya adadin abin da zai yi min."

Nana ta faɗa tare da rushewa da sabon kuka.

#Soyayya

#Nadama

#Makirci

#Kiyayya.

#07032566172

#Wed-jun-11-2025.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

002.

Cikin tashin Ummi ta buɗe baki da idanuwa tana kallon fuskar Nana. Da ka kalle cikin idanuwan ummi za ka gano irin tsananin tashin hankali da ta shiga. Tabbas tasan Tareeq ba ya jin magana ga tsokanar faɗa kamar me ko su dake zaune dashi ya fitine su, domin yaro ne mai kiriniya da taurin kai ga baƙar zuciya amma duk da wannan ko kusan ba taɓa kawowa zuciyarta rashin jinsa ya kai haka ba. Duka Tareeq guda nawa yake yaushe ma ya balaga da zai dinga ɗauko mata masifa irin wannan?"

Tuni idanuwan Ummi sun canza kala cikin yanayi na wanda ya shiga damuwa ta ce.

"Dan ALLAH ba don ni ba kiyi haƙuri maman Nana nai miki alƙawari ko hannun Nana Tareeq ba zai sake taɓawa bare nononta. Sai na hukunta shi hukunci mai tsanani bisa laifi da ya aikatawa ƴarki."

Kafin Maman Nana tai magana suka tsikayi sautin muryar Aayya daga bayansu tana faɗin

"Amma gaskiya Amina kin bani mamaki haka kawai wata banza bazara zata ɗauko gantalalliyar ƴarta, su shigo har cikin gidanmu tai wa jikana ƙazafi ke kuma ki yarda, wallahi da dani ku ka fara cin karo da tuni nasa securities sun watsa ku waje masu baƙar aniya."

Aayya ta ƙarasa magana tare da makawa Maman Nana da Ummi harara.

Tun sanda ta shigo parlour har ta ƙarasa magana Ummi tana kallonta, ko kusa ba ta ji mamakin fitowar waɗannan kalaman daga bakin surukarta ba. Saboda ta kwana da sani tana ɗaya daga cikin mutane da suka jagoranci taɓarɓarewar tarbiyyar Tareeq.

"Haba Aayya wannan wacce irin magana ce?" miyasa duk sanda aka kawo korafi akan Tareeq sai kin nemi kare shi alhali kinsan rashin jin shi duk abun da aka faɗa akansa bana kwakwato zai aikata?"

A fusace Aayya ta ce "To ai ni ba sakarya bace da zan amince da wannan shatin faɗe ba."

"Lallai yau na gasganta abin da ake faɗa akanki Aayya, yanzu ke ko kunya bakya ji a matsayin ki na uwa jikanki ya aikata mummuna laifi irin wannan sannan ki goyi bayan sa?"

"Na goyi bayan sa ɗin daga nan in kin fita ki zarce gidan alƙali dan ALLAH dan Annabi kafin wayewar safiya mu ga sammaci."

"Ai dole ki faɗi haka saboda kina taƙamar ɗanki mai ƙudi ne, amma ba komai ALLAH na nan shi zai bi mana haƙƙinmu da mahaifin Nana yana raye jikanki har isa ya taba masa ƴa wallahi da sai inda ƙarfinsa ya ƙare duk kuɗin ku ba zai zuba ido yana kallo ana cin zarafin 'yarsa ba."

Cewar Maman Nana tana watsawa Aayya mugun kallo.

"Dallah rufe min baki manufukar mata da alama ba nonon ƴarki aka taɓa ba kawai munafuci da tsugudidi ne ya kawo ki gidanan maza ja gantalalliyar ƴarki ku bar mana gida. Wa ma yasani ko da amincewar ta suke ƴan taɓe-taɓensu, na kuruciya kin zo kina so tayar mana da hankali a wofi."

Aayya ta karasa magana tare da nuna wa Maman Nana ƙofar fita

Sosai ran Ummi ya ɓaci da furucin Aayya sai dai ba ta da yadda zata yi, ci gaba da ba wa Maman Nana haƙuri tayi tare da rarrashin Nana.

"Ba komai Maman Fadila na haƙura amma ki tabbata ki ja masa kunne babu shi babu ƴata ya fita sabgarta, ki kuma ɗage da wa ɗanki addu'a shiriya tun kafin tafiya ba tai nisa ba ya fara shuka tsiya irin wannan ba a san me anan gaba zai aikata ba. Na barku lafiya"

Daga haka Maman Nana ta ja hannu Nana suka fice daga gidan, yayin da Aayya tabi Maman Nana da baƙaƙken maganganu.

Zazzafan numfashi Ummi ta sauke kafin cikin kwantar da murya ta ce.

"Haba Aayya miyasa za ki dinga goyon bayan Tareeq bayan kinsan ba shi da gaskiya musamman irin wannan mummunan

laifi da ya aikata?"

"Na sani Amina amma jinin kaine da baya taɓa tsallake wuya duk yadda Tareeq ya kai da lalacewa ba zan ji daɗi wata ta zo daga waje har cikin gidanmu ta aibanta shi."

"Amma Aayya abin da ki ka yiwa Maman Nana ba dai-dai bane. Tunda ita aka wa laifi kamata ya yi mu taru dukka mu bata haƙuri."

"Dallah ya isa Amina yawan maimaita zance shi ke kawo ɓacin rai, kawai mu ci gaba da bin Tareeq da addu'a.

"Ki fahimci ni Aayya...

"Nace ki rufe min baki wallahi Amina da Tareeq bai ɗebo kamaninki ba da nace ba ke kika haife shi ba."

Aayya ta katse Ummi cikin tsawa da fusata. Sannan ta cigaba da fadin "Amma ba abin mamaki bane kiyayyar da kike wa mahaifinsa ce kika tattaro kika dawo da ita kansa."

Jiki a mace Ummi ta juya ta koma kitchen dan bata da saura abin faɗa, Zainab ta miƙe tare da ja siriri tsaki, ta kalli Aayya rai ɓace ta ce "Wallahi-tallahi Tareeq ya fita zakka a gidanan, kullum da kalar masifar da zai jajibo mana yaro sai kace jinin fir'auna."

"Ahir! Zainabu kada na sake jin kin aibanta ɗan uwanki, abun da ya yi Tareeq ai shi ya yi ki idan shi jinin fir'auna ne kema jininsa ce dan kuwa jini irin ɗaya ne ke yawo a jikinku. Duk abin da kika

ga yana yi ƙuruciya ce idan mu ka bi shi da addu'a sai ki ga watarana ya natsu ya daina kowanne yaro da irin tashi kalar ƙuruciyar shi."

Fadila da Baby suka kalli junansu tare da taɓe baki, sun kan tuni suka daina shiga sabgar Tareeq duk da uwa ɗaya uba ɗaya ne ya haife su hakan bai sa ya raga musu ba.

Aayya ta maida ganinta akan su Fadila ta ce.

"Ku kuma tsofaffin munafukai naga sai wani tattaɓe baki ku ke gara ku fito fili ku faɗi abin da ke cikin zuciyoyin ku kada ya kashe ku."

Daga Fadila har Baby ba wanda ko kallon arziki yai mata, hakan ya ƙara tunzirata, ta koma ɗakinta rai ɓace.

Ummi tana shiga kitchen a fusace ta zari muciya kai tsaye ɗakin Tareeq tai wa tsinke tana shiga dai-dai ya fito daga wanka waist ɗin shi ɗaure da brown towel yana fito yana goge sumar kanshi da hand towel, a fusace Ummi ta nufe shi tana zuwa ta rufe shi da duka duk inda ta samu buga mai muciya kawai take  tana haɗawa da zagi

"Ɗan iska yaro kawai marar jin magana tsabar rashin jin naka har ya kai ka dinga taɓa wa yaran unguwa nono, to wallahi bari ka ji duk ranar da ka sake taɓa wa Nana nono sai na illata ka a gidanan. Sai dai ubanka ya tsinka igiyoyin aurensa dake kaina."

Tsaye kawai Tareeq ya yi yana kallonta da girar ido ɗage duk duka da take mai ko gizau bai yi ba. Tamkar tana dukan itace, Ummi sai haki take yi da kyar take jan numfashinta alamar da ke nuna ciwonta na Asthma ya tashi duk da haka bata fasa kai mishi duka ba gani ta fara galabaita Tareeq ya fizge muciyar hannunta ya jefar ya kama kafaɗunta ya zaunar da ita gefen gadonshi da gudu ya fita zuwa main parlour.

"Ya Baby ina inheler Ummi Asthma ta ya tashi."

Tareeq ya faɗa hankalinsa a mugun tashe.

Baby ta zabura da sauri ta nufe bedroom ɗin Ummi.

Fadila ta ɗago cike da takaicin Tareeq ji take kamar ta tashi ita ma ta rufe shi da ɗan banzan duka, cikin ɓacin rai tace.

"Wallahi Tareeq idan ka sake ka zama silar da hawan jini ya kashe Ummi ba za mu taɓa yafe ma ba. Idan kai Daddy shine gatanka mu kuma ita ce gatanmu."

Fadila ta ƙarasa magana mai tattare da karayar zuciya.

Shiru Tareeq ya yi yana sauraren abin da take faɗa, yayin da fusatattun idanuwanshi ke yawo akan fuskarta fitowar Baby daga bedroom ɗin Ummi riƙe da inheler yasa Tareeq ya bi ta da sauri, da taimakon inheler numfashin Ummi ya daidaita ta ɗago idanuwanta da suka canza launi ta watsa su akan fuskar Tareeq da ke jingine da bango, mugun kallo da take aika masa yasa

Tareeq yai saurin kauda fuskarsa.

"Ummi Dan ALLAH ki yi haƙuri ki daina biyewa fushin zuciya, kina dukan Tareeq da duka zai sa ya gyara halinsa da tun kafin ya kawo girman haka ya daina Ummi ki sani duka baya taɓa gyara tarbiyya face ya ƙara jagorantar taɓarɓarewar ta."

Hawaye da Ummi take ƙoƙarin dannewa ne suka silalo akan kumatunta, cikin rawar murya da karayar zuciya ta ce.

"Baby ba za ki gane hali da nake shiga a duk lokaci da aka kawo min ƙarar Tareeq gidanan ba. Lamarin Tareeq kullum gaba-gaba yake yi a maimakon yana girma ƙiriniyarsa ya ragu amma sai daɗa ƙaruwa take."

"Ummi addu'a za ki ci gaba da masa, ni wallahi a wasu lokuta idan naga Tareeq yana wani abu sai naga kamar ba shi ƙadai bane, kamar wani mai shafar aljanu."

Cike da takaicin furucin Baby na ƙarshe Ummi ta galla mata harara, don ba ƙaramin haushi ta bata ba sai kawai ta ture hannuwanta da ke jikinta ta fice daga ɗakin a daidai ƙofar fita taga Fadila jingine jikin bango.

Ummi ba ta tanka ta ba ta wuce zuwa bedroom ɗinta. Bin bayanta Fadila tai har Ummi ta nufi bathroom jin motsin Fadila a bayanta yasa ta tsayawa tare da waigowa.

Cikin rauni murya Fadila ta ce "Dan ALLAH Ummi ki daina saka damuwar Tareeq a zuciyarki kada hakan ya zo ya shafi lafiyarki mu shiga uku."

"Fadila iskanci Tareeq ya isheni duk wanda ya ga yadda yake tafiyar da rayuwarsa ni za a zarga da rashin bashi kyakkyawar tarbiyya, Kuma Ubangiji shine shaidata ina iya bakin ƙoƙarina."

"Haka ne Ummi amma kowanne ɗan adam da irin jarabawar da Ubangiji yake jarabtarsa da ita domin gwada ƙarfin imaninsa. Kar ki fasa ko nuna gajiyawa wajen yi masa addu'a ubangiji yana sane da halin da kike ciki."

Kyakkyawar ajiyar zuciya Ummi ta sauke a kodayaushe cikin godewa ALLAH take da ya bata, ƴaƴa mata masu hankali da natsuwa lokuta da dama suke kwatar mata da hankali a duk lokaci da irin wannan ta faru.

"ALLAH Ubangiji yai muku albarka Fadila ALLAH ya shirya min Tareeq ya ganar dashi illolin da ke tattare da abin da yake aikatawa.

"Amin ya Rabbil alamin."

Murmushi Ummi tai kafin ta buɗe ƙofar bathroom yayin da Fadila ta fice .

"Yanzu Tareeq jin daɗin ka ne ka dinga ƙunsawa mahaifiyar mu bakin ciki?"

Kauda fuska ya yi da bari kallon Baby yana gunguni ƙasa-ƙasa. Duk da Baby ta ga yadda ya yi hakan bai sanyaya mata gwiwa ba, ta ci gaba da faɗin.

"Na tabbata ba za ka so ka zama silar da hawan jini ko ciwon zuciya su kashe ummi ba, saboda haka ka saka kayanka ka je ka bata haƙuri kai mata alƙawarin ba za ka sake aikata kwatankwacin abin da ka aikata yau ɗinan."

Baby ta ƙarasa magana cikin tausasa murya tana kallon gefen da Tareeq ɗin yake jingine ya wani harɗe ƙafafuwanshi wurin ɗaya, yayin da ya yi folding hannuwanshi a ƙirji. A fusace Tareeq ya ce.

"Dan ALLAH Ya Baby ki fita ki bani wuri inaso na saka kayana kada ki ɓata min lokaci."

Waro idanuwa Baby tai tana kallon Tareeq kamar zata sake magana sai kuma ta haɗiye abarta, ta girgiza kai ta fice abinta.

"Mtsss! Haka kawai Ummi ta bi ta tsangwame ni, ta takurawa rayuwata sai kace ni ƙadai ne ɗa. Ita kuma Nana za mu gauraya da ita gobe a school sai naci uwarta wallahi."

Da wannan mita Tareeq ya shirya cikin blue jeans da white colour t-shirt ya ɗora blue p-cap a kansa ƙafafuwansa cikin white trainers, ya bi jikinsa da turaruka masu ƙamshin gaske, bedside drawer ya buɗe can ƙasan wani dictionary ya ɗaga ya ɗauko buddle na one-one thousand ya kirga 50k ya mayar da raguwar kuɗi inda ya ɗauko, kana ya soke wanda ya kirgo cikin aljihun wandonsa, har ya kusa fita daga ɗakin ya tuna da wristwatch ɗinsa da bai saka ba da sauri ya dawo ya janwo drawer mirror ya buɗe wani maidaidaci box ya dauki ɗaya daga cikin tarin agogayen shi. Yana tafe yana saka agogo daidai yana buɗe ƙofar main parlour yaci karo da wata farar yarinya wacce shekarunta na haihuwa ba za su wuce bakwai ba tana zuwa da gudu yayin da take kyalkyalar dariya duk yadda taso ta kauce masa hakan ya ci tura dan sai da ta bangaje shi agogon da yake ƙoƙarin sakawa ya faɗi ƙasa, cikin tsananin tashin hankali ta duƙa ta dauƙo mishi agogo daidai shi ma cikin azama ya duƙa tsoronshi ɗaya idan agogon nashi bai fashe ba. Bai lura da Lokacin da ta duƙa ba sai jin ya yi kanta ya buge bakinshi, sosai ya ji zafin buguwar shiyasa ya ɗago a fusace tuni cikinta ya murɗa ko bata yi mishi laifin komai ba ya dake ta balle yau ta shiga komarsa. Mai ceton ta hannunsa sai ALLAH.

#Tareeq

#Nana

#Ummi

#TeamTareeqImam.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@Jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB

003.

Tun daga yanayi da fizgota ta tabbatar yau duka da zai mata bana wasa bane. Tsanani firgita da tai ga kuma zafin da ya ratsa damtse hannunta sakamakon mugun riƙo da ya mata, tayin wuƙi-wuƙi da idanuwa tsoro ya bayyana ƙarara akan kyakkyawar farar fuskarta. Idanuwanta ta sauke akan murtuƙaƙƙiyar fuskarshi cikin sarƙewar harshe ta furta. "Da...All...ah..Ya...Tashh....

Tun kafin ta ƙarasa magana ta ji saukar rikitattacen mari, sai da ji da ganinta suka ɗauke na ɗan wani lokaci, bayan wuyanta ya riƙe ya dinga sakar mata naushi kamar yana dukan sa'ansa kafin ya ture ta da ƙarfin gaske gefen goshinta ya bugi glass door.

Ta fasa ihu da dukkan ƙarfinta cikin sauti mai ƙarar gaske gaba ɗaya illahirin gidan ya cika da amon sautin muryarta, duhu ya fara mamaye ganinta tun tana gani dishi-dishi har ta ji diff! komai ya tsaya mata cakk! numfashinta ya ɗauke tamkar ɗaukewar wutar lantarki kana ta zube ƙasa dai-dai securities ɗin gidan suna ƙarasowa da gudunsu da sauri Tareeq ya cire agogonshi da ke maƙale cikin tafin hannunta, sai da ya watsa musu mugun kallo tare da nuna su da yatsa yana cizan lips ɗinshi na ƙasa, ya yi ƙwafa alamar da ke nuna gargaɗi kana ya nufi gate cikin tafiyarshi ta ƙasaita, sai kace wanda ya aikata abin arziki da gudu ɗan Bala ya zo ya buɗe mai gate ya fice abinsa hankalinshi kwace zuciyarshi zaune.

Ummi tana fitowa daga bathroom ta ji ihun Tahreem nan take gabanta yai mummunan faɗuwa, da gudunta ta fito daga ɗakinta dai-dai Aayya, Fadila da Baby su ma suna fitowa a guje yadda ihunta ya karaɗe gidan za ka zaci a main parlour take.

Har ture juna suke wajen fita Ummi ce a gaba sai Fadila da ke take mata baya, ɗaya daga cikin securities ɗin ne ya ɗago ta gaba ɗaya jini ya wanke mata fuska.

"Innalillahi wa'inna illaihim raji'un....Bello me ya same ta?"

Ummi ta faɗa sa'ili da ta durƙusa gaban Tahreem tana tattaɓa ta.

"Hajiya nima ban sani ba muna bakin Gate ne muka jiyo ihunta."

Bello ya faɗa domin yana gudun aji mutuwar sarki a bakinshi.

Cike da zallar masifa Aayya ta ce.

"Amma kuwa Bello ba ku da amfani a gidanan taya yarinya za ta ji mummunan rauni irin wannan tsabar lalacewa ace ba ku san dalili ba. Bari Imamu ya dawo daga kai har tawagarka sai kun bar gidanan katti banza kattin wofi kuna cinye mana abinci a banza bakwa kula da aikinku yadda ya dace."

Kuka Ummi ta fashe dashi lokaci da ta fahimci babu numfashi a jikin Tahreem.

"To ko dai zamewa tai ta faɗi ne?"

Baby ta tambaya fuskarta shimfiɗe da mamaki.

"Kai Bello ɗauke ta kasa ta mota mu kai ta hospital kuna kallo ko numfashi ba ta yi kun tsaya ɓata lokaci."

Fadila ta faɗa a ɗan fusace domin ba ƙaramin haushi securities ɗin suka ɓata ba.

Da sauri Ummi ta koma ciki ta dauƙo hijab haɗi da ATM card ɗinta.

Tana dawowa ta ci karo da Baby ta dauƙowa Aayya nata hijab ga baki ɗaya suka ɗuguma zuwa asibiti.

Kasancewar asibitin da suke zuwa ce shiyasa aka karɓe su da gaggawa nan take aka shiga treating ɗinta, dukkansu tsa-tsaye suka yi a bakin ƙofar ɗakin da aka shigar da ita.

Har zuwa lokaci Aayya tana kumfar baki.

"Wannan lalacewar ta Tahreem tayi yawa duk girmanta ace batasan yadda ake tafiya ba, gashinan garin shan-shancinta ta jawo mana zuwa asibiti da magaribar fari."

A fusace Baby ta maida wa Aayya magana cikin ɓacin rai take cewa.

"Dan girman ALLAH Aayya ki barmu mu ji da abin da ke damun mu ko ke kin wuce ALLAH ya kawo miki tsau-tsayi ki zame ki karya hannu ko ƙafa?"

"La'ilaha'illahu......Maryama ni kike yi wa mummunan fatan In-sha-ALLAH akan ɗaya daga cikin ubanai ki karaya za ta ƙare ba dai ni Aayya ba, ƴar banza yarinya mai kambun baka."

Fitowar doctor Hafiz yasa ba wanda yasake bin ta kan Aayya balle ta sami mai bata amsa.

"Dr Hafiz ya jikin nata?"

Ummi ta faɗa muryarta na rawa.

"Al-hamdulillah! Ta farfaɗo ta ɗan bugu a gefen kanta har mun mata ɗimki nayi mata allurar bacci saboda tana buƙatar hutu, da zarar ta farka za a yi discharge ɗinku.

"Al-hamdulillah!

Kusan a tare suka faɗa kafin Fadila tai karaf ta ce "doctor za mu iya shiga mu ganta?"

"Kwarai kuwa amma Dan ALLAH banda hayaniya."

Cikin yatsine fuska Baby ta nuna Aayya da baki tare da furta

"Ita za ka faɗawa Dr domin tun ɗazu kwakwazonta ka ke ji, gara ka kashe mata gargaɗi tun wuri ta gane akwai bambanci tsakanin asibiti da gidan Imamu."

Baby ta ƙarasa magana cikin gatse.

"Na shiga uku ni Aayya Maryama ni kike faɗawa magana Kamar wata sa'arki, Amina a gaban ki ƴarki ke kwashe min albarka tsabar lalacewa kin zuba mata idanu taci karenta babu babbaka ko? To bari Imamu ya dawo wallahi daga ke har ita sai nasa yaci min mutumcin ku mutanen banza da wofi."

Ajiyar zuciya Ummi tayi tare da goge zufan goshinta da gefen hijabinta, kafin ta dallawa Baby harara rai ɓaci ta ce.

"Bana cike da iskanci Baby Aayya sa'arki ce da za ki dinga faɗa mata magana son ranki, maza bata haƙuri kafin na rufe ki da duka."

Turo baki Baby tayi cikin yatsina ta dubi Aayya ta ce.

"Allah ya ba ki haƙuri Aayyarmu."

Ta tare da tura ƙofar ɗakin da Tahreem take wanda tuni Fadila ta tsofa ciki.

"Aikin banza can ki nemo Aayyarku wannan Aayya ta Tareeq ce domin shi kaɗai ne duk a cikin ƴaƴa da Imamu ya haifa da ba ya min ɗibar albarka."

"Dan ALLAH Aayya ki daina biyewa yaranan su na saka ki kumfar baki."

Ummi ta faɗa tana mai tura ƙofar ɗakin ta shiga, mugun kallo Aayya ta bi ta dashi kafin tai ƙwafa ta bi bayanta.

A kwance suka tarar da Tahreem an mata fixing ɗin drip sai sharar bacci take kusa da ƙafafuwanta Ummi ta zauna, cike da alhini take kallon gefen goshinta da ke lulluɓe da bandeji.

Fadila da Baby suka jingina da bangon ɗakin zuciyarsu cike take fal da tausayin Tahreem,wata irin ƙauna suke mata kasancewarta marainiya kuma ƙarama a cikinsu shiyasa ko ciwon kai take gaba ɗaya sai sun shiga damuwa. Tareeq ne kaɗai bai damu da ita ba, ba dan baya ƙaunarta ba kawai dai yana cin zalinta ne dan ya fahimci duk gidan ita kaɗai ce zai taɓa ya saka su ɓacin rai shiyasa, duk lokaci da suka haɗu sai ya zalunce ta hanya rankwashi ko ya murɗe mata kunne, ko kuma ya ja mata gashi yana kiranta da mai red hair Kasancewar sumar kanta ba ɓaki bane

jajir yake sai tsantsi tsiya don ko kitso ba a  mata sai dai ayi mata parking da hairband ko ai mata kalaba.

Tareeq yana fita kai tsaye gidan su Roonie ya nufa yana zuwa gidan ya wuce ɗakin Ronnie da ke boys questers, koda ya shiga Ronnie yana zaune gefen gado yana ɗaure igiyoyin takalmin shi. Hannu Tareeq ya miƙa mai suka kashe ya nemi doguwar kujera guda ɗaya tal da ke ɗakin ya zauna.

"Dan ALLAH Roonie ka sa wa jikinka gishiri mu bar unguwar nan na rantse maka da ALLAH idan Ummi ta rutsani a gidanan yau kashina ya bushe ko ɗazu ta min duka, don kawai Maman Nana ta kai ƙarana.

Balle yau na ɗebo ta da zafi na kuma tabbata ko yanzu ba tsallake wa dukan nata zan yi ba."

Dariya Ronnie yasa har yana dukan gefen gado.

"Wai Slugger sai yaushe za ka wuce duka a wurin Ummi?"

"Ba rana Roonie saboda kullum ni mai laifi ne a wajenta. Musamman yau da na taɓo shalelenta red hair.

Zaro idanuwa Ronnie ya yi cikin ƙaduwa ya ce.

"Kutt! lallai yau abokina ka taɓo tsuliyar dodo ALLAH yasa ba dukanta ka yi ba?"

"Sai dai kar a sake abokina don har goshinta na fasa kai a takaice kwance na baro ta cikin jini, dukan da Ummi tai min na huce akanta."

"Saboda Ummi ba ta buguwa shine ka huce akan ƴarta wallahi ka ji tsoron ALLAH kada haƙkin marainiya ya kama ka."

Ronnie ya faɗa yana mai miƙewa tsaye.

"Kai dallah mu tafi ba wani haƙki da zai kama ni maraya nawa ne ake zalunta sai ni da na taɓa guda ɗaya shine haƙki zai kamani zance banza kawai in fact Ummi ce ta jawo mata ko gobe ta dake ni sai na rama akan red hair ai Roonie Ummi tayi sake da na gano mai jan gashi ita ne weakness ɗinta."

Sosai furucin shi ya ba wa Ronnie dariya, cikin dariya ya ce.

"Gaskiya abokina kai taƙadari ne na ƙarshe bangon littafi, na rantse da ALLAH ban taɓa gani tsagera irinka ba."

Tareeq yai murmushi yana shafa sumar kanshi, suna fitowa suka ci ƙaro da Lil-prince ya ɗauko motar Abbanshi saboda yau haka suka tsara da tsalelliya motar Alhaji Sa'id marafa za su fita Da gudu tsiya suka bar unguwar kai tsaye wani wurin hutawa suka nufa dama, anan suke zama a duk lokacin da suka haɗa joint.

Anan suka tarar da raguwar abokan rashin jinsu Hisham Yahaya ɗan kwangila da suke wa laƙabi da Dezzy sai Sadeeq A. Salis shi kuma su na kira shi da Sasco sai mace ɗaya kacal da ke team ɗinsu Rufaida Mustapha sodangi suna kira ta da Roofy Sodangi.

Dalilin shigar Roofy Sodangi gang ɗinsu Tareeq saboda tsananin ƙaunar da take mai duk da kasancewarsu classmate, kuma agemate soyayyar shan mitti suke zubawa abinsu tamkar ba ƴan secondary School ba ko kuma teenagers.

Suna zuwa Roofy ta taso da sauri jikinta har ɓari yake ta rungume Tareeq, ba kunya bare tsoron ALLAH ya ke lalluɓarta a bainar mutane.

Shisha pot aka kawo musu haɗi da champagne bottles, a gefe ɗaya ga ice cubes a cikin wani ɗan ƙaramin bowl, idan suka zuƙi shisha su yi sipping champagne.

Duk yawancin samari da ƴan matan da ke zaune a wuri matasa ne masu ƙaranci shekaru,kallo ɗaya za kai musu ka fahimci cewa ƴaƴa masu hannu da shuni ne wanda suka fi ƙarfin iyayensu, ko kuma wanda ba su da mafaɗi ko ana faɗa ba sa ɗauka.{ALLAH Ubangiji ya shirya mana yaran mu bisa hanya madaidaiciya, dole sai mu ɗage da yiwa ƴaƴanmu addu'a domin muna cikin wani irin zamani da tarbiyya tai ƙaranci, kuma mu dinga lura da irin abokanai da yaran mu ke hulɗa dasu}

A can asibiti kuma sai misali ƙarfe 11:20pm Tahreem ta farka tuni an daɗe da cire mata drip, da sauri Fadila ta fita ta kira doctor da ke on call ya sake duba jikin Tahreem ya ga komai normal ya cike masu discharge papers.

"Baby ki tashe da Aayya mu tafi gida naga kamar bacci ya ɗauke ta."

Ummi tai magana tana ƙoƙarin kama Tahreem ta sakko daga kan gado.

Baby ta nufi gun da Aayya take kwance akan sallaya da tai sallar isha'i.

"Aayya....Aayya! Ki tashi mu tafi gida an sallame mu.

Baby ta faɗa tana ɗan bubbuga kafaɗar Aayya, buɗe idanuwa Aayya tayi tare da jan guntun tsaki.

"Mtsss..!

Kana ta zarce da faɗar.

"Uhmm!... ALLAH shi kyauta yau lalacewa ta cika da mu a asibiti, shi kuma wannan lalatacce likita sai yanzu ya, damar sallamar mu, kai Allah dai wadan naka ya lalace."

Ta ƙarasa magana tana warware hijabinta wanda dashi tai matashi.

Fadila ta matso kusa da Ummi ta kama Tahreem suka fice Ummi da Baby suka biyo su a baya yayin da Aayya tana tafe tana mita, duk azababbiyar mita da take yi ba wanda ya ce mata ci kanki.

Sai da suka shiga mota sun ɗau hanyar gida Fadila ta kwantar da kan Tahreem a cibiyoyin ta tana shafa sumar kanta, cike da zallar damuwa tace.

"Gifty garin ya ya kika ji wa kanki mummunan rauni irin wannan?"

Baby da Fadila ke kiranta da suna gifty saboda kyauta ce wacce Allah ya basu, kuma sharp brain gareta bala'in kokari ne da ita gata da ɗan banza surutu.

Sai da Gifty ta lumshe idanuwanta kana ta buɗe su ta ɗago kanta ta yadda za ta iya gani fuskar Fadila da kyau, cikin 'yar muryarta mai cike da yarinta ta ce.

"Lokaci da na dawo daga islamiyya na shigo da gudu, shine muka ci karo da Ya Tashh by mistake na bangaje shi wristwatch ɗinshi ya fadi shine ya zabga min mari yana ta dukana ya ture ni goshina ya bugi glass door.

Jeeddah Aliyu

07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

004.

Ummi tai sauri runtse idanuwanta tana jin wani irin ɗaci a maƙogwaronta, wannan ɗaci haka take jinsa a duk lokaci da Tareeq ya aikata wani mummunan laifi. Kafin ta lallaɓo kalmar da za ta faɗa ta ji saukar murya Aayya a dodon kunnenta tana cewa da Gifty.

"Ke Tahreem yaushe kika fara koyon saƙa da mugun zare ina ruwan Tareeq dake da zai miki wannan ta'adi ina sane da ko kallon kirki baya hada shi da k....

Da sauri Fadila ta katse Aayya cikin fusata.

"Kar ma ki fara Aayya saboda kin fi kowa sani halin Tareeq yadda yake zaluntar Gifty, naga take-takenki ki ce tai masa ƙazafi sanin kanki ne tun sanda Gifty ta zo duniya Tareeq yake cin

zalinta, har kawo yau bai fasa cutar ta ba."

"Ya Fadila kenan kamar kin manta da wacece Aayya,ai indai akan Tareeq ne tana gani gaskiya baro-baro za tai fatali da ita ta shigo da son zuciya ita haka ALLAH ya yi ta da bala'in son zuciya a wurinta Tareeq baya laifi."

"Ya isa Baby!

Ummi ta katse Baby cikin tsawa, banaso nasake jin ɗaya daga cikinku ta sake magana a motar nan."

"Ai da kin barsu, su ci gaba da zagina iya son ransu haba ina dalili kowanne ɗan banza ya kwaso sharar sa sai akan Tareeq, baki yana neman ya yi masa yawa to ta ALLAH dai ba ta mutum ba masu kambun baka ƴan gadon butulci"

Tuƙuƙin da Ummi take ji a cikin zuciyarta ya hanata tankawa Aayya har suka iso gida Aayya tana ci gaba da masifa,tana yadawa Ummi magana a fakaice.

Kai tsaye Fadila ɗakinta ta wuce da Gifty, Yayin da Ummi ta wuce nata ɗaki tana zuwa ta ciro wayarta da ta bari tana charging kan bedside drawer, yadda take jin haushi da takaicin Tareeq kamar in ta rutsa shi baza ta bar shi da numfashi ba.

Dialling number Alhaji Imam wali tayi gani take wannan issue ba zai yu ta barshi zuwa wayewar gari ba, tabbas sai ta ɗauki mummunan mataki akan Tareeq ba zata zuba mai ido ya zo ya illata mata ƴa ba. Gara tun wuri shi da yake goya mai baya yake tsula rashin mutunci iri-iri yasan irin ta'asar da yai wa ƴar marainiyar ALLAH.

Ringing ɗaya zuwa biyu Alhaji Imam Wali yai picking cikin sanyi murya yai sallama, a daƙile Ummi ta amsa mai ya zarce da tambayar lafiyarta da ta yara ba ta amsa masa ba saboda ba shi ne maƙasudin kira da tai mai ba. Kai tsaye ta zarce da faɗar.

"Alhaji na kira ne domin ka san hali da ake ciki, ka yiwa tufka hanci idan ba haka ba wallahi-tallahi duk mataki da na ɗauka akan ɗanka kada ka ga zarge ni....

"Ɗan dakata mana Amina kin fi kowa sani na tsani rashin natsuwa a al'amurrana, duk tsiyarki da masifarki kya bari mu gaisa cikin mutunci da lumana har fa tambayarki lafiyar gidana nai amma tsabar masifa ta ciyoki ba ki amsa min ba."

"Idan har ka damu da sani lafiyar gidanka kira za ka yi ba wai sai na kira ka da tawa matsala ba ka zarce da faɗar taka."

"Shike nan Amina nima ina so ki gaggauta faɗar dalilin kira na domin bani da lokaci ɓatawa akanki, ina da ayyuka masu tarin muhimmanci a gabana."

"Ba laifi dama nasan har gaba da abada ba za ka yi lokacina ba....

"Amina Please just go straight to the point!

Alhaji Usman Wali ya katse mata numfashi cikin hasala.

Sosai ran Ummi ya ƙara ɓaci a dalili yadda ya daka mata tsawa kamar wata ƴarsa ko baiwa furucin da yake amfani dashi ko kusa bai yi kama da na wadda ke magana da matarsa ba, dakyar ta saita natsuwarta cikin muryar da ke bayyanar da tsanani fushi da ɓacin rai ta ce

"Inaso ka gargaɗi shalelen ɗanka kada ya kuskura hannunsa ya sake sauka akan Tahreem.

"Idan kuma naƙi fa?"

Alhaji Imam Wali yai sauri tarar numfashinta.

"To wallahi-tallahi duk abin da nai masa shi ya jawo.

"Idan kin fasa kin rena ALLAH Amina dan ALLAH dan ƙaunarki da Annabi kafin na dawo ki yi gunduwa-gunduwa da naman jikin Tareeq, hakan ne kawai zai ƙara gamsar da ni zallar ƙiyayyar da kike min. Tun-tuni na gama fahimtar ki Amina sanadin ƙiyayyar da ki ke min ce ta shafi Tareeq, saboda kin fahimci ta hakan ce kawai za ki ƙara ƙuntata min."

"Wannan kuma matsalarka ce Imam Wali amma ina mai tabbatar ma da cewa ko ban yi gunduwa-gunduwa da Tareeq ba, tabbas za ka dawo ka tarar da mummunan rauni a jikinsa tamkar dai yadda yai wa Tahreem, saboda ita ma ƴa ce kamar yadda yake ɗa ba kuma gata ya fi ta dashi ba."

Tana gama magana ta datse kiran, tare da saka wayarta Flight mode gudu kada ma ya sake kiranta.

Sororo Alhaji Imam Wali ya yi tare da ƙurawa wayar hannunshi ido, zuciyarsa na masa wani irin bugawa sau da dama sai zuciya ta ciyo shi ya ji tamkar ya datse igiyoyin aurensa da ke kan Ummi, sai kuma wani ɓangare na zuciyarsa ya hane shi. Yana matuƙar ƙaunar Amina ita ce jini da bargo jikinsa yana mata azababbiyar soyayya da fatar baki ba za ta iya misaltawa ba. Sanadin gundarin so da yake mata yasa ya shanye shekaru masu yawan gaske yana haƙuri da zazzafar ƙiyayyar da take masa.

An ce zuciyar mace rauni ne da ita bata zurfafa ƙiyayya, amma ban da ta Ummi shekaru 26 da yin aurensu kawo yanzu ba abin da ya sauya daga matsananciyar ƙiyayya da take mai, a takaice ma sai daɗa ƙaruwa take har abin yana ƙoƙarin shafar gudan jininsa.

Zuciyarsa ko kusa ta kasa jurewa bata yi la'akari da yawan shekarun shi ba, ko kuma babban matsayinsa sai da ta raunata masa zuciya ta haddasa masa sakin wasu irin zafafa hawaye suka tsiyayo daga kwarmin idonshi, zuwa ga kumatunsa yasa ɗan yatsa ya laƙato su.

Wani irin tausayin kanshi yake ji har ya fara tuhumar kanshi da kanshi ta hanyar furta.

"Miyasa na kasa haƙura da son da nake miki Amina, har ta kaini da cilasta miki aurena?"

Wannan tambayar duk da ya kwana da sani amsarta amma a kusan kodayaushe cikin yi wa

kansa ita yake. Sai yanzu ya ƙara tabbatar da so abin banza ne bai ga amfani da yai mai ba sai ma jefa shi da ya yi cikin ƙunci da takaici.

Da wani irin fushi Ummi ta jefar da wayarta akan gado, ta miƙe ta shiga bathroom ruwa ke sauka jikinta daga shower da ta kunna sanyi su na ratsa fatar jikinta hakan ne ya haddasa wa zuciyarta yin sanyi, har ta shiga backward ɗin abin da ya faru tsakaninta da mai gidanta, ta rasa dalili da yasa a kodayaushe cikin samun misunderstanding suke ta kuma rasa dalili da yasa a kodayaushe take zurfafa tsana da take masa wacce ita kanta a yanzu ta fara bata tsoro da firgici musamman da ta gano ƙiyayya da take wa Imam Wali bata da bambanci da wacce take wa ɗan ta jini jikinta Tareeq.

Sai dai ta lakanta tsanar da tai wa Tareeq a bisa yawan ƙiriniyarsa.

Fadila ta haɗa ruwan wanka, ta yiwa Gifty wanka Baby taje ɗakin Gifty ta ɗauko mata sleeping dress ta kawo mata, koda suka fito daga bathroom hatta da abinci Baby ta ɗebo mata sai da Fadila da Baby suka tabbatar duk wani abu na al'ada da suke wa Gifty kafin kwanciya bacci sai da suka yi mata kafin suka barta ta kwanta.

Sai around 1:30am su Tareeq suka baro joint kowanne a ƙofar gidansu Lil-prince ya sauke shi kafin ya juya akalar motar ya nufi nasu gida, can cikin bacci ɗan Bala maigadi tare da securities ɗin ke on duty a main gate suka ji ana bugun gate da ƙarfin bala'i tamkar za a ɓalla shi sun san aikin Tareeq ne, da mugun gudu ɗan Bala yazo ya buɗe mai.

Wani mugun kallo ya watsawa Dan Bala sa'ili da ya buɗe masa gate suka yi 2 eyes "Barka da dawowa maigida farin zaki magajin Daddy."

Ɗan Bala ya faɗa yana sosai ƙeya.

"Banaso kutumar b*... uba ɗan Bala tun yaushe nake tsaye anan ina bugun gate kayi banza da ni sai kace gidan mallakin tsohonka ne."

"Allah ya huci zuciyar magajin Daddy wallahi bacci ne ya ɗauke ni..

"I'll you shut up my friend, ko nan gidan ubanka ne da za ka kwanta bacci?"

Tareeq ya katse shi a tsawace duk da ran Ɗan Bala ya ɓaci da yadda Tareeq ya zage shi tare da buga masa tsawa amma haka ya danne cikin karya harshe ya shiga bashi haƙuri.

Tsaki kawai ya yi ya ture ɗan Bala a gefe ya shiga gida kusan securities huɗu ya gani suna kai da kawo lungu da saƙon gidan, domin ƙara tabbatar da tsaro duk gaisuwa da suke masa bai amsa ba ya nufi flat ɗin shi.

Tun daga parlour ya soma cire kayan jikinsa yana watsi dasu duk inda yaga dama. Daga shi sai boxer ya ƙarasa bedroom kafin ya kwanta saida ya yi wanka ya saka wayarshi charging wacce tun kafin ya fita ya saka ta a Flight mode.

Tun Asuba da Ummi ta tashi Sallah kawai tayi ta nufi ɗakin Fadila taga hali da Gifty take ciki saboda jiya da ita ta kwana a ranta.

Koda ta shiga ɗakin ta tarar da Fadila ta tashi tana zaune gun da tayi sallah tana azkar, Gifty kuma tana kan gado tana bacci, gefen kanta Ummi ta zauna cike da kulawa take shafar jar sumar kanta.

"Ina kwana Ummi?"

Fadila ta gaida Ummi tare da baro gun da take zaune ta dawo gefen gadon ta zauna.

"Lafiya ƙalau Fadila ya jikin Tahreem?" wallahi ko kaɗan ban runtse ba da yarinya nan na kwana araina."

"Al-hamdulillah Ummi ta ji sauƙi sosai naga kamar magani da tasha akwai na bacci shiyasa na barta ta ɗan ƙara hutawa zuwa 7 o'clock in tashe ta tai sallah."

"Shike nan Fadila ki barta amma ki tabbata ƙarfe 7 ɗin ki tashe ta."

"To Ummi."

Daga haka Ummi ta baro ɗakin.

Tareeq yasan, ya aikata babban laifi a wurin Ummi shiyasa yau ya yi shiri zuwa School da wuri, yana gudun kada Ummi ta rutsa shi.

Misali ƙarfe takwas Tareeq Imam Wali ya iso cikin makaranta ya hango ana assembly, cikin tafiyar shi ta kasaita da izza hannuwanshi zube ciki aljihun wandon uniform ɗinshi, ya wuce cikin tawagar ƴan ajinsu{SS2}, tsabar neman magana yasa hannu ya jawo Shariff Idris Kankia ya fito dashi daga cikin jerin ɗalibai ya kuma maye gurbinsa.

Kasancewar Shariff yaro ne da baya so fitina uffan bai ce dashi ba ya koma ƙarshe layi ya tsaya, tun tsayuwa Tareeq wuri yake neman faɗa ya tokari wannan ya ja kunnen wannan idan ka kalli shi ya ɗaga ma gira ko ya kashe idonshi ɗaya duk bayani da principal ke yi ba ko ɗaya da ya ji.

Can idanuwanshi suka sauka akan fuskar Nana wacce ke nesa dashi kaɗan, tun shigowarshi ta ganshi tasha jinin jikinta lokaci-lokaci take satar kallonshi. Da zarar ta ga zai kallo gefenta sai tai sauri kauda kai, a karo na ba adadi ta ɗago da zimmar satar kallonshi karaf suka haɗa ido sai lokaci ya lura da tana tsaye a wuri.

Mugun kallon da ya watsa mata sai da gabanta ya yi mummunan faɗuwa, tsoronsa ya bayyana ƙarara a cikin ƙwayar idonta.

Jeeddah Aliyu

07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeedddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

005.

Cikin sauri Nana ta kauda fuskarta jikinta na wani kalar rawa, kamar an mata dole haka ta sake waigawa ta kalli Tareeq

A karo na biyu idanuwansu suka sarƙewa karkaɗa mata yatsanshi ya yi tare da yi alama da wuyanshi da ke nuna sai na yanka ki. Wani sabon tsoronshi ne ya ƙara kamata ana kammala assembly Kowanne ɗalibi ya nufi class saɓani Tareeq da ya nemi gefen doguwar baranda class ɗinsu ya zauna, duka abokan rashin jinsa ba su zo ba saboda kullum a late suke zuwa shima sakamakon laifi da yai wa Ummi ya sanya shi sammako.

Nana tana hango shi jikinta ya shiga ɓari dole ta ja ta tsaya tana kallo ɗalibai ƴan uwanta suna shiga class da tayi yunkurin nufar class sai kuma ta ji bata da kwarin gwiwa yin hakan. Tsintar kanta tayi da zubda hawaye har ta shiga danasani faɗawa mamanta abin da Tareeq yake mata, da basu kai ƙarar shi gidansu wurin umminshi ba da yanzu bata cikin wannan halin.

Komawa tai ta jingina ga pillar da ke jikin baranda ɗin ta ɓoya ta yadda Tareeq ba zai ganta ba, inda ALLAH ya taimake ta, sai ta hango Uncle Joel zai shiga ajinsu, da gudun bala'i ta nufi class tana isowa dai-dai ƙofar shiga shima Tareeq yana shirin shiga duk iskancinshi yana tsoron Uncle Joel saboda ya kware da wulaƙanta mutum a gaban class shi kuma abin da ya tsana kenan.

Yadda ya nufi class da sauri kamar zai tashi sama ga kuma Nana da ta fallo da gudu idanuwanta sun rufe sam bata lura da Tareeq ba mummunan karo suka ci. Rai ɓace ya ɗago yaga wacece ko wanene ya siyawa kansa masifa da sanyi safiya, fusatattun idanuwanshi ya sauke akan fuskar Nana wacce saura ƙiriss ta saki fitsari a uniform skirt ɗin ta ta firfito da manyan idanunta. Tareeq bai yi wata-wata ba ya ɗauke ta da mugun mari yana ƙokarin sake ɗauke ta da wani Uncle Joel ya ƙaraso yai karaf ya riƙe mai hannun.

"Why are you slapping her?"

Cewar Uncle Joel yana kallon Tareeq yayin da Nana ta tsuguna tare da sunne fuskarta tsakanin gwuiwayinta tana rera kuka.

Cikin fusata Tareeq ya fincike hannun shi dake cikin tafin hannun Uncle Joel, cikin ƙara ji yace.

"Ask her the reason Uncle!"

Koƙarin sake magana Uncle Joel ya yi amma sai Tareeq ya bi ta gefenshi ya shiga class.

"Come back here Teeri I'm not finish yet with you, Teeri i say come back am warning you."

Uncle Joel bai iya fadar Tareeq ba shi ne yake kiransa da Teeri

Banza yai da uncle Joel tamkar ba dashi yake magana ba, cike da takaici Uncle Joel ya kama hannun Nana ya miƙar da ita tsaye ya shiga rarrashin ta kafin ya umarce ta da ta shiga class.

Tareeq ya zauna a permanent sit ɗin shi sai wani cin magani yake, Uncle Joel ya shigo shima fuskarsa babu rahama ko kaɗan ya yi pointing ɗin shi da yatsa cike da bada umarni ya ce.

"You stand up and leave my class right now."

Basarwa Tareeq ya yi tamkar bai fahimce dashi yake magana ba, hakan kuma sai ya ƙara harzuƙa Uncle Joel cikin kakkausar murya ya sake furta.

"I'm talking to you Teeri just get out of my class or else I'll report you to the principal."

Kasancewar yasan muddin maganar ta je kunnen principal, kashinsa ya bushe dan nan take yake rubuta wa student suspension letter ya tura ka gida idan aka yi suspending ɗinsa a wannan karo shine na bakwai a wannan term ɗin kuma gashi ya yiwa Daddynshi alkawari, ba zai sake laifin da za a suspending dinshi dan haka baya fatar faruwar hakan. Shiyasa ya miƙe cikin tafiyar ƙasaita mai cike da zallar izza da taƙama ya fice har ya kai ƙofar fita ya waiga ya kalli side ɗin da Nana take ya karkaɗa mata ɗan yatsanshi tare da nuna ke kuma taki ta ƙare.

"Mtsss...useless boy.

Uncle Joel ya faɗa haɗe da tsaki kana ya bi Tareeq da harara.

Tareeq yana fita ya nemi gaba da class kaɗan ya zauna, sai cika yake yana batsewa.

Har Lil-prince ya iso kusa dashi bai sani ba sai da ya dafa ƙafadarshi,sannan ya ɗago idanuwanshi da suka kaɗa suka yi jajir.

"Wane mai ƙarar kwana ne ya taɓowa kanshi our highness?"

Lil-prince ya faɗa tare da zaunawa gafda ƙugun Tareeq, shiru Tareeq ya yi sai musu-musu yake da baki tare da jan iska daga ƙofufin hancinsa. Lil-prince ya kai dubansa ta window ɗin class ɗinsu ya hango Uncle Joel yana rubutu akan whiteboard, sai kuma ya dawo da ganinsa akan Tareeq, ya ce "Ga dukkan alama ka yi halin naka shine bald head ya cillo ka waje {Suna da suke kiran Uncle Joel dashi kenan saboda yana da irin mugun sanƙo nan na tsakiyar kai}

"Lil na rantse da Allah sai naci uwar Nana sai nai mata tabo da ba zai taɓa gogewa nan kusa. Shi

ma bald head ɗin da take takama dashi in naga dama sai nai sanadin da za a kore shi a school ɗinan tun ba ta ubansa bace. Amma zan kyale shi sai ranar da na rubuta last final exam ɗina, wallahi sai na fasa masa sanƙonsa kuma daga rana ya bar makarantar nan shege mummunan."

Dariya Lil-prince ya shiga babbakawa tamkar wanda aka yiwa albishir mai daɗi, tun kafin Roonie ya ƙaraso kusa dasu cikin ɗaga murya ya fara jefawa Lil-prince tambaya.

"Kai ɗan iska dariya uba me ka ke yi haka kodai yau za ta fashe ne?"

"Kai dai ƙaraso mutumina yau bald head ya dauƙo dala ba gamo, don kutumar ubanshi da sanyi safiyar nan ya ɓatawa our highness rai."

Shima Roonie y yana zuwa ya nemi hagun Tareeq ya zauna suka saka shi tsakiya.

"Wai me kuma ya koma haɗa ka dashi ne Slugger?"

Roonie ya faɗa yana kallon murtuƙaƙƙiyar fuskar Tareeq, zazzafan numfashi Tareeq ya sauke kafin cikin hasala ya shiga basu labari abin da ya wakana tsakaninsa da Nana.

Ronnie ya dafa kafaɗar Tareeq cikin sanyi murya ya shiga faɗar

"Gaskiya slugger ka fita harkar yarinya nan kar ta sake zuwa gidanku ta haɗa ka da Ummi, banaso rashin jituwa yai ta shiga tsakaninka da mahaifiyarka."

Kafin Tareeq yai magana Roofy Sodangi ta fito daga cikin class, tun sanda Uncle Joel ya kora Tareeq waje hankalinta yake a tashe ga baki ɗaya ta rasa natsuwarta. Sai neman hanyar  da za ta fito tazo wajenshi take shine ta ɗauki excuse za tai fitsari. Tana fitowa dai-dai lokaci da Tareeq yake faɗar.

"Ni fa Roonie bana tsoro duk abin da Nana za ta faɗa a gidanmu, burina kawai na haɗu da ita a kaɓaɓɓe wuri nai mata wulaƙanci da za ta adana shi a shafi na tarihin rayuwarta banasan Nana ta manta dani cikin rayuwarta."

Roofy Sodangi tana zuwa ta rufe Tareeq da faɗa idanuwanta sun rufe ruff! Wani irin masifaffen kishi ke nuƙurƙusar zuciyarta, don gani take yi, kamar Tareeq yana son Nana ne shiyasa kodayaushe yake ƙiƙƙirar faɗa a tsakaninsu, cikin kaushin murya ta shiga faɗar

"Nana... Nana! For God sake I'm sick and tired of hearing her name coming out in to your mouth Tareeq

miyasa ba za ka iya rabuwa da yarinyar nan ba, sai yunkuri jefa kanka matsala kake. Kana da labari idan har maganar nan bald head ya kai ta a kunnen PC zai iya gayawa Daddynka, ka daina gani duk abun da kayi mahaifin ka baya gani laifin ka. Ka sani wannan karon laifinka zai iya taɓa ƙima da mutunci mahaifinka.

I swear to God na gaji da zance wannan banzar Nana ɗin, sai kace ita kaɗai ne mace a whole school ɗinan."

Maganganu Roofy Sodangi ba ƙaramin ƙara baƙatawa Tareeq rai suka yi, don ji yake yi kamar ya tashi ya rufe ta da bala'in duka.

Sauke fusatattun idanuwanshi yai akan fuskarta kafin yace.

"This is my first and last warning to you Rufaida ki daina yi min shisshigi da kutse a cikin almurrana ke wacece da za ki faɗa min abin da ya dace nayi?"

Gani yadda Tareeq ya harzuƙa yasa Lil-prince ya shiga bubbuga kafaɗarsa "calm down abokina kada ka dauki maganar Roofy da zafi saboda tana ƙaunarka ne shiyasa bataso ka sami matsala da mahaifinka."

"Dallah ya isa Lil! ka daina goyon bayan yarinya nan ta fiye shiga abin da bai shafe ta ba. Ni dan ALLAH Ku tashi ku shiga class kada mu taru duka mu yi hasarar darasin bald head."

Tareeq ya faɗa yana harara Roofy Sodangi da ke tsaye a gabanshi.

Sosai ta ji zafin abin da yai mata dama can ita ce ke binshi shiyasa kullum cikin wulaƙanta ta yake. Ba tare da tasake furta kalma ko ɗaya ba ta juya a fusace ta koma class, Roonie har ya yi niyar magana Tareeq ya dakatar dashi "Roonie please ku tafi kawai banaso damuwa."

Sani halinsa da suka yi da saurin hawa yanzu sai rashe ya juye da mujiya faɗa ya dawo kansu, shiyasa suka tashi salu-alu.

Saida period ɗin Uncle Joel ya ƙare bai wuce remain 11 minutes ya fita ba sannan ya kira Tareeq ya dawo class kuma don tsabar yana so yai masa mugunta yace "Any question students?"

Suka ce "No Sir!

"Okay get ready for snap test."

Kuma all questions da ya tambaya daga cikin topic ɗin da ya kammala koyar dasu ne, cikin abin da bai fi ten minutes ba ya fara faɗar "everybody drop off your pens and and get ready to submit yours papers."

Dama Tareeq a front desk yake zama saboda haka da gangan Uncle Joel ya fara ta kanshi, da ƙarfi ya finciko takarda Tareeq ya ƙurawa haɗaɗɗen handwriting ɗinshi idanu yana karanta abin da ya rubuta, yayin da Tareeq ya kauda fuskarshi yana kallon window.

Girgiza kai Uncle Joel ya yi cike da takaici ya kammala karanta test ɗin ya rasa wane irin brain ne da Tareeq ga shi da rashin ji da ƙiriniya amma kuma shine best student a school ɗin, shiyasa yawancin schoolteachers suke ɗaga mai ƙafa. Duk da baya cikin class aka yi darasin amma shegen gari gaba ɗaya ya rubuta amsa tambayoyin dai-dai. Duk yadda kaso ka ƙure shi sai dai shi ya ƙure ka yaron yana da baiwa sosai.

Uncle Joel yaga test ɗin Tareeq ya duƙulƙuleta ya cilla a dustbin, ya nufi ƙofar fita yana faɗar "see you next time students!"

Gaba ɗaya class ɗin ya hartsine da ihu saboda sun fahimci ya yi cancelling test ɗin, haka kuma ba ƙaramin daɗi yai musu ba.

During breakfast period Kowanne student ya fito domin cika cikinsa, suna nufar students dining room da aka tanadar masu domin yi breakfast.

Katon dining room ne mai dauke da ƙanana dining table masu four chairs, kowanne student da kalar breakfast food ɗin yake so shi zai ci saɓanin su Tareeq da tun lokaci da suka zama senior student suka daina taking breakfast a school, shiyasa ko kallo dining room ɗin bai ishe su ba.

Can bayan premises suka zauna har zuwa lokaci Tareeq yana cin kansa duk irin musu da ya kaure a tsakanin Roonie da Sasco bai furta uffan ba sai bin su kawai yake da ido.

Roofy Sodangi kasa jure shirun nasa tayi da kam har tayi fushi dashi sai kuma fushin nata ya kasa yin tasiri, ta taso daga wurin zamanta ta dawo kusa dashi. Hannunshi ta kama a hankali take massage ɗin palm ɗinshi idanuwanshi ya ɗago ya kalleta sau ɗaya ya kauda fuska.

"Are you still mad with me?"

"Who the hell think you're da zan yi fushi dake?"

"Haba slugger wai miyasa kake min haka ne, wallahi nakan shiga damuwa na rasa walwala ta a duk sanda ranka ya ɓaci, ka yi haƙuri kadaina fushi nan ka saki ranka Please."

"Mtsss! ke dai ƙaramar ƙwaƙwalwa ce dake Roofy, duk zama na da ke kin kasa fahimtar wanene, ni. Nan da ki ka ganni ko mutane masu muhimmanci a rayuwata bana da lokaci ɓatawa nai fushi dasu balle ke, saboda haka karki nemi ki takura min."

Sosai Roofy Sodangi ta ji haushi maganganun shi, ranta ɓace ta miƙe gaba ɗaya ta bar wuri ta nemi can nesa da su ta zauna tana jira breakfast period ya ƙare ta koma class.

Kamar daga sama Tareeq ya ji ta bayanshi an kira sunansa kuma, kamar muryar Nana, kamar wanda ya tsorata haka ya waigo idanuwanshi suka sarƙe cikin nata, tsoronshi ya hango shimfiɗe a cikin ƙwayar idanunta. Zubur ya miƙe tsaye.

"Ubanwa ya kawo ki wajena wa ya ce ki ambaci sunana?"

Tareeq ya ƙarashe magana yana wani dakawa Nana tsawa.

Tsananin tsorata da tayi yasa ta dafe kunnuwanta da hannuwanta biyu tare da runtse idanuwa.

#TareeqImam

#RoofySodangi

#NanaBashir

Jeeddah Aliyu

07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

006.

Yadda Tareeq ya dakawa Nana tsawa ya jawo hankali wasu tsirarun ɗalibai, sannu a hankali Nana ta shiga buɗe idanuwanta don ta zaci wani mari zai sake kifa mata. Da ta fahimci kallo ya dawo kansu tai sauri bari wuri, ta nufi class da mugun kallo Tareeq ya bi bayanta dashi, can ƙasan zuciyarshi yana cike da mamakin dalili zuwan nata wajenshi.

Har aka koma class su Tareeq suna zaune, da yake mathematics ne dasu kuma teacher ɗin mace ce, ko kaɗan basa tsoronta basu girmama ta,sai sukai zamansu har ta cinye first period ɗinta, ta shiga second da yake double period ne. Suna zaune abin su kuma basu da niyar komawa class ɗin. Fitsari ne ya matse Nana ta dau excuse, tana cikin gyara skirt ɗinta, sai kurum taji an turo kofa da ƙarfi sai da ta zabura Tareeq ta gani tsaye fuskarshi a murtuke kamar bai taɓa sani me ake nufi da dariya a rayuwarsa ba, nan take cikinta murɗa ya bada wani sauti mai ƙarfi kamar zatai gudawa sai zarar ido take, cikin kaduwa da sarkewar harshe ta haɗa haruffan sunansa  "Ta.ta.ree...q!"

Mugun kallo ya watsa mata kafin ya maida kofa ya rufe ruff! Har da murza key, wasu yawun tsoro Nana ta hadiya, ta shiga ja da baya fizga ɗaya yai mata ya kaita jikin wall tiles ya yi pinning ɗinta rikitattun idanunshi ya zuba mata, ai kuwa jikinta ya dau kakkarwa Nana tana ji tana gani Tareeq ya cire mata mini hijab ɗin jikinta, ga rigar uniform ɗinsu white ce tsautsayi yasa ta cire jacket saukar hannunshi ta ji akan ƙirjinta tai sauri runtse ido abun da yake mata ne ya haifar mata da daukewar numfashi na wancan gadi,tun sanda ya fara taɓa mata kirji bai taɓa yimata in a gentle way ba sai a wannan karo shiyasa ta rikice ta rasa wacce duniya take ciki. Nana tana da tsananin sha'awa wadda a karancin shekarunta bata gama fahimtar me hakan yake nufi ba amma sometimes idan tana kallon movies aka haska romantic scene saurayi da budurwa suna shafe-shafe sai ta dinga ji wani abu yana tsirga mata, har wani ruwa take ji yana fita a gabanta. Motsi taɓa kofa suka ji da sauri Tareeq ya janye daga jikinta, tare da yimata wani shu'umin kallo dakyar Nana ta iya jan kafafunta ta buɗe kofa ta fice, jikinta sai rawa yake.

Special breakfast food Ummi ta haɗawa Gifty duk abin da tasan tana so saida ta girka mata, sai wanda ranta keso za ta zaɓa. Karfe bakwai dai-dai Fadila ta tashe Gifty ta haɗa mata ruwa tai mata wanka kana tasa tayi sallah.

Bayan ta Kammala sallah Fadila ta jawo stool ta zaunar da ita gaban dressing mirror, tasan halin Gifty bataso gyaran gashi kusan kodayaushe sai an yi fama da ita kafin ta bari a taɓa gashinta musamman da yawaicin mutane suke tsokanar suman ta, kasancewar shi dark red hair gashi da matuƙar tsantsi gaske comb tasa a hankali ta taje mata ta yadda ba za ta ji zafi ba.

Ta raba mata shi gida biyu ta ɗaure mata da pink hairband mai hoton teddy bear a jiki, hairstyle ɗin ya ƙara ƙawa ta fuskarta tai matuƙar kyau, white colour Australia gown Fadila ta dauƙo mata mai watse Pink flowers a jiki ta mikar da ita tsaye tasa mata rigar ya tsaya iya guiwayoyinta kafin ta Kama hannunta suka fito main parlour kai tsaye dining room suka nufa inda suka hango Ummi da Baby na arranging table gani yadda Fadila ta shirya Gifty yai matuƙar faranta ran Ummi har ta kasa ɓoye farin cikinta tai sauri ajiye plate ɗin hannunta tana murmushi ta rungumo Gifty "ma-sha-ALLAH autar Ummi jiki ya warware zo maza ki ci abinci duk abin da ki ke so yau shi na girka miki."

Cikin sigar shagwaɓa Gifty tace "Thank you umminmu."

Baby ta ja mata kujera ta zauna kana ta shiga bubbuɗa warmers tana nuna mata kaloli abincin.

"Ya Baby zan sha kunu gyaɗa da ƙosai kuma inasan na ci waina."

Gifty tai magana cikin shagwaɓabɓiyar muryarta.

Nan take Baby ta zuzzuba mata abubuwan da ta lissafa. Fadila ta karɓi mug ɗin kunu ta shiga bata a baki sai shagwaɓa take zubawa.

Aayya da fitowar ta kenan daga ɗakinta tai tsaye tana kallon yadda Ummi da ƴaƴanta suka taru akan Tahreem sai nuna mata kulawa da ƙaunar ta musamman suke. Hakan ba ƙaramin baƙanta mata rai ya yi ba, tsanar da tai wa mahaifiyar Tahreem har yanzu da bata duniya da raguwar ta a ƙasan zuciyarta, a fusace tasoma tattaki zuwa dining room ɗin tana tafe tana zazzaga masifa "Oh ni Aayya yau naga abin da yafi zare tsayi tsabar lalacewa Amina ku taru ayari guda ke da zugar ƴaƴanki duk akan cin abinci rai guda. Ni kuma tsabar ba ku damu da ni ba, ba ɗan bante uban da ya kira ni na zo na karya kumallo. To daɗin abin ɗa da na haifa ne ya kawo abinci ba Usmanu ba.

Aayya ta ƙarasa magana sa'ili da ta iso cikin dining room ɗin, cikin sanyi murya Ummi ta furta "ina kwana Aayya?"

"Ka ji wani rashin ɗa'a Amina sai yanzu za ki gaida ni halan ba ki san ɗakina ba?"

"Haba Aayya! ko kin manta da asuba ni ce na tashe ki?"

Cewar Ummi tana murmushi takaici.

"To tun da kinsan da haka miye na wani tambayana kwana, idan ma kwana kike so tambaya je ki ɗakina yana nan kan gado na baro shi."

Kafin Ummi tai magana Baby ta riga ta, ta hanyar ballawa Aayya harara tana faɗin

"To Bismillahi...Al-masifatu minal azabatu safiyarki ta waye kenan, za ki fara halinki in za kiyi breakfast ki zo ga kujera ki zauna, tun da sassafe za ki fara addabar mu da ruwan masifa...

Cikin tsawa Ummi ta takawa Baby birki.

"Ya isa Baby wallahi ki kiyayye ni banaso rashin kunya Aayya ba sa'arki bace ki san irin maganganun da za ki dinga furta mata."

"Allah ya ba ki haƙuri Ummi."

Baby ta faɗa tare da ajiye serving spoon rai ɓace ta nufi cikin parlour, kujera Ummi ta jawa Aayya tare da kwantar da murya ta ce "Dan Allah Aayya ki yi haƙuri wallahi ina da niyyar na je na kira ki sai gashi kin fito, amma In-sha-ALLAH daga yau hakan ba zai sake faruwa ba."

Taɓe baki Aayya tayi tare da zaunawa Ummi ta zuba mata kunu gyaɗa, da ƙosai ɗayan plate kuma ta zuba mata waina saboda tasan tana so waina sosai. Fuskar Aayya babu walwala alamun har yanzu bata gamawa hucewa ba, ta dubi Ummi a ɗage ta ce "ina fatar kafin Tareeq ya fita ya yi karin kumallo kinsan shi da son waina?"

Ita ma Ummi ɗaure fuskarta tayi cikin ɓacin rai ta shiga faɗin "kema Aayya kinsan halin Tareeq da rashin son cin abinci sau nawa za a yi waina a gidanan a ajiye masa ƙarshenta ya tsallake ya fi ce abinsa."

"Wannan kuma ai ba hujja bace Amina da kin yi niyar bashi yaci ki san hanyar da za ki bi kamar dai yadda ki ka saka shalelen ƴarki a gaba kina lallaba ta kamar kwai har da bata a baki sai kace kuturwa, kodai bata da yantsu ne?"

Da sauri Fadila ta ɗago ta kalli Aayya ta watsar wani shegen haushinta ya turnuƙe mata zuciya, ji take kamar ta taso ta rufe ta da shegen duka, sai dai ba halin yin hakan. Sau dama saboda halin masifar Aayya take fatar tayi aure ta bar mata gida.

Sai Ummi ta dube ta cikin danne ɓaci rai ta ce "Haba Aayya Dan ALLAH ki dinga faɗar abin da zai yiwuwa mana yanzu fissibilillahi Tareeq da girmansa zan zauna ina rarrashinsa dan yaci abinci sai kace wani yaron goye."

"Ita kuma wannan mai jan gashi ai naga yarinyar goye ce shiyasa ku ka taro ku na bata a baki."

Gifty naji Aayya ta kira ta da sunan da ta tsana, nan take ta ji abinci ya fi ce mata arai domin har idanuwanta sun cicciko da hawaye duk tsangwama da hantararta da Aayya ke mata baya damunta amma da ta kira ta da mai jan gashi sai ranta ya sosu wani lokaci har kuka take yi, Fadila tana gani yanayi Gifty ya sauya tai sauri kama hannunta ta ja ta suka bar dining area ɗin.

Duk da haka sai da Aayya ta bi su da zagi.

"Wawayen banza marar sa zuciya ku zauna kuna raino ƴar wani ku bar ƙaninku, an bi an koya muku mugun hali ai kuwa ga ku nan zube a gida ko kare bai taya ba."

Ummi kan tsabar takaici da baƙin ciki kasa furta uffan tayi sai kawai ta tattara abincin Gifty ta bi ta dashi ɗakin Fadila, ai kuwa Aayya ta sake buɗe sabon shafin masifa da gore-gore sai da ta gaji don kanta, sannan taci abincinta.

Ummi kuka ta tarar da Gifty tana yi Fadila tana rungume da ita sai faman rarrashinta take ran Ummi ya ƙara ɓaci ta tsani duk abin da zai ɓatawa Tahreem rai balle har ya kaita da zubda hawaye ita ɗin amana ce a gurin ta shiyasa take matuƙar kiyaye duk abin da zai iya saka ta damuwa ko ya ɓata mata rai.

Kusa da ita Ummi ta zauna ta ciro ta daga jikin Fadila ta mayar a nata jiki, ta rungume ta tsam...a hankali take shafar gadon bayanta.

"Bana so kukanki Tahreem yana saka ni cikin matsananciyar damuwa, har na kan ji na gaza maye miki gurbin uwa da kika rasa. Koda bana auren Daddyn Fadila Aayya uwa ce a gare ni ita da mahaifiyata uwa ɗaya uba ɗaya ne ya haife su, kuma lokaci da mahaifiyata ta bar duniya muna da ƙanana shekaru ni da mahaifinki kamar dai ke, ita ce ta raine mu cike da so da ƙauna tun tasowa ta har na kai muzalin aure bata taɓa nuna min bambancin da ƴaƴan da ta haifa ba. Asali ma zan iya ce miki tafi ƙaunata fiye dasu. Rashin jituwa tsakanin mu ya samo asali ne tun daga lokaci da na zaɓi mahaifin Yayanku Jabeer na ƙi ɗanta bayan mahaifin Jabeer ya rasu, suka aura min Daddyn Fadila batare da neman jin ra'ayina ba.....

"To ita kuma Gifty miye laifinta anan Ummi da Aayya ke hantararta?"

Fadila tai saurin katse Ummi da tambaya da alamun akwai raguwar ɓacin rai a tare da ita.

Sai da Ummi ta gyara zamanta ta tattara natsuwarta wuri guda kana ta ce "Saboda Usman ya bijirewa auren yakumbo Ku Maimunatu, ya aure mahaifyar Tahreem wacce ta kasance buzuwa."

Zaro idanuwa Fadila tayi tace "Cabdijam!... lallai tsangwamar da Aayya take wa Gifty ashe da walakin goro a miya."

Ajiyar zuciya Ummi tayi tare da kai dubanta ga Tahreem wacce taji jikinta ya saki alamun tayi barci, murmushi Ummi tasaki sakamakon gani yadda Tahreem ta jefa yatsan a baki tana tsotsa.

"Fadila bansan sai yaushe Tahreem za ta daina shan yatsa ba?"

Ummi ta faɗa tana jawo pillow ta ɗora kan Gifty akai kana ta gyara mata ƙafafuwanta ta yadda za ta ji daɗin kwanciya.

Dariya Fadila tayi tare da furta "Da yardar ALLAH zuwa gaba za ta daina Ummi. Nikam ummi zan so wata rana ki ba mu tarihin rayuwarki da dukkan alama kin sha gwagwarmaya."

Murmushi ummi tayi kafin ta ce "Fadila babu komai a cikin tarihina face takaici da tausayi amma tun da kina buƙatar ji nai miki alƙawari watarana zan sanar dake tun daga farko har izuwa ƙarshensa.

Misali ƙarfe uku aka

tashe su Tareeq daga school tun kafin lokacin direbanshi yake zaune yana jiranshi, ƙa'idarsa ce kafin wa'adin tashin su ya yi dole direbanshi ya kasance a school ɗin a cewar shi ba zai iya jira ba sai dai shi a jira shi, tsabar iskanci irin na Tareeq ba zai wuce gida ba har sai ya jira an zo ɗaukar friends ɗinshi.

Tsau-tsayi yasa wata rana direban ya gwada yi mai complain rufe idanuwa ya yi yai masa rashin mutunci har da su zagi, daga lokaci Malam Musa bai sake kwantata yi mai korafi ba. Saidai ya yi zamansa cikin mota yana jiranshi.

Sai da abokan rashin jin nashi suka wuce kafin ya nufo mota da sauri Malam Musa ya fito ya buɗe mai ƙofa ya shiga.

Tareeq yana gudun haɗuwa da Ummi shiyasa bai bi ta ƙofar main parlour ba, bayan ya cire school uniform yai watsi dasu kan gado wanka ya yi ya fito ɗaure da brown towel a gaggauce ya shirya cikin black colour crazy jeans trouser riga mai gajeren hannu yasa ta matse mishi ƙirji da damtse hannuwanshi dama sune ire-iren kayan shi da matuƙar wahala ka ganshi da shigar arziki saida ya gabatar da sallar la'asar kafin ya dauko wayarshi ya fito daga ɗakin. Kai tsaye ɓangaren Hajiya Jamila ya nufa wacce ta kasance uwar gidan Alhaji Imam Wali, yana shiga babban parlour ya tarar da Baby da Zainab tare da Uncle Hamza su na fira, sai famar kyalkyalar dariya suke yadda ya turo ƙofa da ƙarfi yasa su katse dariya da suke yi kusan a tare su duka suka kalle ƙofa kowanne su da irin kallon da yake mai, shi ma kallonsu yai ya watsar cikin tanke fuska ya kalli Zainab ya ce "Ya Zainab Mommy na ciki?"

"Mommy bata nan Tareeq ta tafi koyon sallama."

Zainab ta furta tare da ƙare masa kallon banza.

"Mtsss! aikin banza!"

Baby ta faɗa tana gallawa Tareeq harara.

Murmushin reni wayau yai kafin ya ce "Ya Zainab ni ki ke wa baƙa ke kuma Ya Baby da wa ki ke?"

"Da kai ake ko za ka dake ni ne?"

Baby ta faɗa tana mai sake balla mai harara wacce tafi ta farko. Zainab kuma sai cewa tayi

"An maka ɗin ko akwai abin da za ka yi?"

Wani irin mugun kallo yake bin su dashi kafin ya yi ƙwafa ya ce "dukkan ku biyu kun yi marmarin

kwanciya gado asibiti shiyasa bakunan ku basa tauna magana kafin su furta min. To amma ba komai dama can ni kwararre ne a karya ƙasusuwan mata, cikinku wacece na taɓa karya wa?"

Ke ce?

Ya nuna Zainab sai kuma ya sake nuna Baby yana wani zaro ido "Ko kuma ke ce? Gosh! Babu ita a cikin ku ya Fadila ce ko? Ku san ni ba wani tantance ku nake yi ba, adai dinga kiyaye harshe Muhammad Tareeq baya ɗaukar nonsense."

Yadda yake magana cikin izza da taƙama dole ko waye kai ya ba ka haushi shiyasa yana dasa aya Uncle Hamza ya miƙe a fusace ya nuna shi ɗan yatsa "Kai wane irin marar ɗa'a ne Tareeq?Daga Zainab har Baby babu sa'arka amma kake faɗar za ka karya su to bara ka ji duk wacce tsau-tsayi ya aike ka taɓa koda ɗan yatsanta ne da sunan duka, na rantse ma da ALLAH sai nayi kusan kashe ka a gidanan ɗan iska kawai marar mutunci, wanda bai san abun da yake yi ba."

Kowacce kalma da ke fitowa daga bakin Uncle Hamza tana sauka a dodon kunne Tareeq tana daɗa tunzira shi, yayin da ranshi yai bala'in ɓaci cikin fusata ya ce "Ka ga ɗan wada{kasancewar Uncle Hamza ba shi da tsayi gajere ne shiyasa Tareeq yake kiransa da ɗan Wada😅} a shawarce ka daina shiga sabgar da ba taka ba musamman idan ka ji ana magana ta ahali kai fa ba jinin Mamman Wali kusada bane da za ka wani zakalkale ka shigo zance ƴan uwa. Kuma kamar yanda ka faɗa ba mutunci ne dani ba in kayi wasa har kai ɗin zan iya kwantar wa a gadon asibiti."

"Iyeee Tareeq! Uncle Hamza ɗin?"

Kusan a tare Baby da Zainab suka haɗa baki wajen furta wa tare da zaro idanuwa haɗi da dafe ƙirji.

Tsaki Tareeq ya ja yana hararar su yake faɗin

"Mtsss! Uncle Hamza ɗin mana ko kuna kwankwato ne na gwada maku zahirin gaskiya, wadda ma yafi uncle Hamza na zubar dashi balle shi da nake kallan shi tamkar Tahreem."

A fusace Uncle Hamza ya taso ya nufi Tareeq ya ɗaga hannu da nufi wanke mai fuska da mari mommy tai sauri riƙe masa hannu wacce haniyarsu ce da taji tayi yawa yasa ta fitowa daga ƙaramin parlournta. "Subhanalillah! meke faru ne Hamza me Babana yai ma da za ka dake shi?"

Cikin irin mugun ɓaci rai nan Uncle Hamza ke magana

"wallahi-tallahi Aunty, Tareeq ya fara kaini bango matuƙar ba ki yi mai iyaka dani ba na rantse da ALLAH sai na kassara mishi rayuwa, yaro ya bi ya raina kowa a gidanan ba wanda yake ragawa ni ba zan jure wannan iskanci nashi ba."

"Waye kai Uncle Hamza me kake dashi? ka manta a karkashin dukiyar ubana kake rayuwa, duk wata izza da jiji da kanka da bazar mahaifina kake taka rawa. Idan ba za ka jure iskancina ba sai

ka tattara kayanka ka koma gidan ubanka. Kuma wallahi idan ba ka yi hankali ba sai nai maka korar ƙasƙanci a gidanan, kora irin wacce ake wa kare...

"Kai ya isa Tareeq banaso shirmen banza da rashin kunya Hamza tsarar wasanka ne da za ka dinga faɗa mai magana kamar kana yi da sa'anka?"

Mommy ce ta katse Tareeq cikin fushi.

Turo baki ya yi irin na sangartattun kuma tsageru yara yana wani ɗaure fuska.

"Babana ka natsu kasan me kake yi kullum ƙara girman kake,kuma kaine magajin wannan gidan, kai kaɗai ALLAH ya mallaka mana a matsayin ɗa namiji burinmu ka zame mana tamkar ɗa dubu ka zama abin alfaharin mu. Amma wannan halin naka na rashin girmama na gaba da kai yana faɗar min da gaba ka yiwa kanka karatun ta natsu."

Jikin Tareeq yai matuƙar sanyi shiyasa yake ƙaunar Hajiya Jamila saboda tasan yadda za tai mishi nasiha cikin ruwan sanyi saɓani umminshi da kullum cikin zagi da hantararshi take.

"Ki yi haƙuri Mommy In-sha-ALLAH ba zan sake ba."

Yadda Tareeq ya furta magana cikin tattausan lafazi da karya kai tamkar ba shi ba.

"Shi kenan yaron kirki maza ba Uncle Hamza haƙuri."

"Uhmm! mommy!."

Ya faɗa cikin muryar shagwaɓa har da bubbuga ƙafa a tiles alamar hakan fa da matuƙar wahala.

"What do you mean Babana ba za ka iya bada haƙuri bane?"

"No mommy ba haka nake nufi ba kawai dai ban yi laifi da zan bada haƙuri ba."

Kunne shi Mommy ta kama ta murɗe a hankali ta ce "Banaso gardama oya ka yi abin da nasa ka kafin na tuzge wannan kunne da ba ya jin magana, faɗi mana."

Mommy ta ƙarashe magana tana ƙara murɗe kunnen nashi da ɗan ƙarfi.

"Ouchhh! mommy zafi karki cire min zan faɗa i am sorry Uncle Hamza."

Wani irin mashahurin takaici ne ya kama Uncle Hamza, harara Mommy ta galla mai alamar kayi magana zuciyarsa tana masa tuƙuƙin ya furta "its okay. Daga haka ya sa kai ya fice daga parlour, yana mai jin haushi yadda kodayaushe yayarsa ke biyewa Tareeq su na ƙara sangarta shi yana yi wa mutane rashin kunya iri-iri.

"Saura Ya Zainab da Ya Baby suma kace su yi haƙuri."

Cewar mommy tana kallon Tareeq tana murmushi ɓata fuska ya yi tare da zubawa mommy manyan idanuwanshi masu kama da na mahaifin shi sakk.

"Su kuma Mommy miyasa?"

"Saboda su na gaba da kai kuma ka yi musu rashin kunya, a matsayinka na ƙaramin ƙaninsu dole ka bada haƙuri.

"Ku yi haƙuri."

Ya faɗa a takaice tare da kife kanshi a shoulder mommy ya runtse idanuwanshi duk duniya in da akwai abin da ke bashi haushi yake kuma yi masa matuƙar wahala furta wa shine kalmar ban haƙuri duk sanda ya aikata laifi, mommy da Daddy ne kaɗai mutane da suka isa su cilasta mai bada haƙuri.

Yana ɗagowa Zainab tai mai gwalo Baby kuma tai mai blowing kiss, sosai hakan ya ƙara harzuƙa shi kamar zai fashe da kuka ya ce "mommy kin gansu ko su na tsokanata wallahi ina karya ɗiya yanzu nan."

Dariya mommy tayi tare da watsa masu harara tana faɗin "Ku ɓace min da gani manyan Kwabo kawai shiyasa ya raina ku."

Ficewa suka yi suna ci-gaba da sheƙa dariya abinsu don kawai su ƙara tulawa mai haushi.

#Tareeq

#Uncle Hamza

#Mommy

#Zainab

#Baby

#team TareeqImam.

Aayya ta ce a gayamuku kada ku shagala da karanta Free page ku manta da na kuɗi ne😂

Ta ce ga masu buƙatar ci-gaba da karanta wannan littafi za su biya 700 kacal ta wannan asusun banki 7032566272 Hauwa Shehu opay. Aayya tayi arha ta hana bashi dan haka ku hanzarta ku nunawa shalelenku Tareeq ƙauna, duk da Tareeq yace a baku part one kyauta amma part two kun dai gane, kusan Tareeq ɗan albarka ne yana yin ku.

Jeeddah Aliyu

07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@Jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

007.

Nana tana kwance a ɗakinta tayi rub da ciki tun dawowarta daga school take kwance tamkar marar lafiya, ko wacce bata da lakka a jiki bata da kuzari da walwala ko kaɗan. Duk sanda tai yunkuri ta tashi ta cire school uniform ta watsa ruwa a jikinta sai ta ji wata irin kasala da mutuwar jiki ya lulluɓe ta, abun da Tareeq Imam yai mata a school shi kaɗai ke mata yawo a kwakwalwa. tsawon rayuwarta bata taɓa dawowa daga school ta zauna da uniform a jikinta ba koda na mintuna ɗaya ne. Balle har ta kasa wanka saboda ita ɗin mutum ce mai tsananin tsaftar gaske wannan horu ne daga mamanta.

Jin shirunta ya yi yawa bata fito ba parlour ba bare taci abinci yasa Mama ta nufo ɗakinta, ta ganta kwance ga kuma uniform bata cire ba. Hakan ya haifarwa Mama da faduwar gaba har ta shiga tunani ko Tareeq ya sake taɓa mata ƴa da kuwa a wannan karon ba zasu kwashe ta daɗi ba ita da iyayenshi. Ba zai yiwa ba ya hanawa ƴarta sakewa dole ta kai report a school authorities.

Kusa da ƙafafuwanta Mama ta zauna ta bubbuga ƙafafuwanta haɗi da kiran sunanta "Nana! Ke Nana!"

Mama ta kira sunanta da ɗan ƙarfi

firgigit Nana tayi tare da saurin tashi zaune ko ba ka tambaya ba fuskarta za ta bayyanar maka da damuwar da take ciki.

"Na'am Mama!.

Nana ta faɗa sa'ili da ta jinginar da bayanta ga kan gado.

"Nana ya kike kwance ko school uniform ba ki cire ba ko dai taƙadari yaranan Tareeq ya sake miki wani abu ne?"

Nana tsintar kanta tayi da wani irin mashahurin faduwar gaba ambatar sunan Tareeq kawai da

Mama tayi cikin sanyi murya ta shiga girgiza kai tare da faɗin "Ba abin da ya yi min Mama kawai dai bana jin daɗin jikina kamar zazzaɓi ne yake so kamani."

"Subhanalillah! shine ba za ki faɗa min ba kika ƙunshe a ɗaki yaushe kika fara koyon ɓoyemin halin da kike ciki Nana?"

Sadda kai ƙasa Nana tayi tana wasa da ƙaramin zoben zinari da ke maƙale a ɗan yatsanta na hagu "Ba ɓoye miki nayi ba Mama kasala ce ta rufe ni tun ɗazu nakeso na tashi na yi wanka ko na ji ƙarfi jikina amma na kasa tashi."

Nana ta ƙarasa magana tana ɓoye hawaye da ke ƙoƙarin zubo mata. Hannu Mama tasa a gefen wuyanta taji temperature ɗinta.

"Ikon ALLAH! Nana jikinki ba zafi ko kaɗan?"

Mama tai magana cikin mamaki "Eh... Mama kawai kaina ne ke ciwo sai kuma rashin kuzari da nake ji, amma bara nai wanka watakila gajiyar school ce ke ɗibana."

"Shike nan tashi maza ki watsa ruwa ina jiran ki a parlour ki ce abinci idan jikin bai warware mu je asibiti a duba ki banaso zama da ciwo kin ji ko?"

Gyaɗa kai Nana tayi saida ta shiga bathroom Mama ta ji saukar ruwa kafin ta fice daga ɗakin. Cikin ƙanƙani lokaci Nana ta fito ɗaure da blue towel, kaitsaye wardrobe ɗinta ta buɗe ta ciro plain gown na material mai ƙaranci nauyi ta ajje gefen gado kana shiga tsane raguwar ruwan da sukai saura a jikinta turare kawai ta shafa ta zura rigar ta fito parlour.

*******

Hannun Tareeq Hajiya Jamila ta riƙo ta ja shi zuwa cikin ƙaramin parlournta, cikin hikima da kwarewa take masa nasiha kafin ta kira ɗaya daga cikin masu aikinta tasa ta kawo mai abinci kaɗan ya tsakura, dan shi ba ma'aboci cin abinci bane barshi da kayan zaki, kamar shazumame.

"Babana me ya sami wayarka Daddy yace ko ya kira layin ka a kashe?"

"Lafiya ƙalau kawai dai wayar ce banaso kuma Ummi tace ba za a canza min ba shiyasa na rufe ta."

Murmushi Hajiya Jamila tai kafin ta shafi sumar kan Tareeq tare da faɗin "Babana Sarkin rigima yanzu saboda canjin waya zai sa ka haramtawa Daddynka jin muryarka almost a week rabo shi da yai magana da kai, ka kuwa san yadda ka ɗaga mai hankali?"

Zamburi baki ya yi yana gunguni ƙasa-ƙasa

Mommy ta kira Alhaji Imam Wali a wayarta bayan sun gaisa, ya ji lafiyar gidansa ta kara wa Tareeq wayar a kunne shi cikin shagwaɓa ya furta "Daddyna...!

Saukar muryar Tareeq a dodon kunnen Alhaji Imam Wali ya haddasa masa sakin ƙarfaffiya

ajiyar zuciya saboda ya yi kewar ɗa nashi ba kaɗan ba.

"My Heir!

"Na'am Daddyna ina wuni?

"Ba zan amsa gaisuwarka ba Tareeq har sai ka faɗa min laifin da nayi da ka kashe wayarka, kuma ka kasa nema na."

Tareeq yai wani ɓata rai tamkar yana gaban Daddy nashi, cikin shagwaɓaɓɓiyar murya ya amsa da cewa

"Daddy ba laifi da ka yi kawai dai banso wayar nan. So nake a canza min, kuma Ummi ta ce ba za a canza ba."

Dariya ya yi irin ta dattawa kafin cikin kwantar da murya ya ce "My Heir kai ma kasan waya ba matsala bace zan kira El-yaqub ya kawo maka wayoyi new version har gida ka zaɓi wacce ka ke so.

"Ni Iphone 7 nake so wannan 6 ce an gama yayin ta."

"Shikenan El-yaqub zai kawo ma har gida."

"To amma Daddy ya za ka yi da Ummi tun da ta ce ba za a canza wayar ba, ni gaskiya banaso faɗa nan nata na rashin dalili?"

Tareeq ya faɗa yana wani yatsine fuska tare da turo baki.

"Don't mind her ai ba kuɗinta bane, yanzu dai mu ajiye matsalar waya da ta Amina a gefe tun da na ri ga da na magance wannan matsalar."

Cewar Daddy yana ƙoƙarin kawar da zance Ummi saboda ko kaɗan bayaso ya ji an ambata mishi sunanta yanzu sai mood ɗinsa ya canza.

Fira suka shiga yi tamkar wasu Friends tsawon lokaci suka share akan waya kafin, suka yi sallama sai gafda magariba Tareeq ya baro ɓangaren Hajiya Jamila.

Misali ƙarfe 9:00pm Tareeq ya fito cikin shiri na fita gantalinshi na dare yana tafe yana wani taƙama ga ɗan uban ƙamshin designer perfume dake tashi a jikinshi, a compound ya haɗu da Ya Fadila jingine da motar Isma'eel saurayin ta da za ta aura, ko kallon gefen da suke Tareeq bai yi ba ya nufi parking lot Isma'eel ne ma ya yi ƙarfin hali yimasa magana "Muhammadu Tareeq yau ba ko gaisuwa?"

Banza ya yi dashi tamkar bai ji ba al'hali ya ji shi sarai lokaci amsa mai ne kawai baya dashi.

Ɗaya daga cikin tsadaddun motocin Daddy ya nufa tun da yamma yasa Isa ya wanke masa ita ya yi unlocking kofufin motar ta hanyar danna remote

Fadila ta ankara abin da yake shirin aikatawa ta kalli Isma'eel dake ta faman korafi akan yai wa Tareeq magana bai amsa ba. Cikin sauri ta ce "Kayi haƙuri Babe bani two minutes nai magana dashi da alamun akwai abin da ke damunshi."

Ta ƙarashe magana bata jira amsar da Isma'eel zai bata ba ta nufi parking lot da saurinta "Kai Tareeq ji mana tsaya zan yi magana da kai."

Ta faɗa tun kafin ta ƙarasa gun sa.

Cakk! ya tsaya tare da waigowa nan take annurin fuskarsa ya ɗauke.

"Me kake shirin yi ne in short ina za ka tafi da motar Daddy amma sato key ɗin ka yi ba tare da sani Ummi ba ko?"

Ta faɗa sa'ili da ta isa kusa da shi.

Wani irin mugun takaici ne ya lulluɓe shi ya shiga ƙare mata kallo from head to toe kafin ya shiga tata mata rashin mutunci tamkar yana yi da sa'arshi "Wai ke Ya Fadila ba ki da aiki ne sai na gulma? Ya kamata ki sauya hali wallahi."

Cikin matuƙar fusata Fadila ta nuna shi da yatsa "Watch your tongue Tareeq kasan irin maganar da za ka dinga furta min remember I'm your elder sister."

"To hell with you da zamanki elder sister, ke bara ki ji Ya Fadila kar ki ga ina raga miki ki ɗauka ina jin tsoronki ne kasancewar ki gaba da ni ba shi zai baki damar yimin abun da kika ga dama ba,don haka ki fita sabgata ba ruwanki da....

"Tareeq!

Fadila ta katse shi cikin tsawa da hargagi kana ta ci-gaba da cewa "Ka zage ni iya adadin da ranka keso amma ba zan taɓa bari ka fita gidanan da motar nan, domin ALLAH ne kaɗai yasan irin masifar da za ka je ka ɗauka mana a gari yaushe ma ka kware da driving da za ka fita da mota?"

"Kutumar ubanan wai kina nufi kece za ki hanani fita da motar da ubana ya zuba kuɗi ya siya?"

Tareeq ya faɗa yana dariya mai cike da reni.

"Kwarai kuwa ko kana mamaki ne?"

"Ba mamaki na ke ba Ya Fadila saboda na daɗe da sani ke ɗin cikakkiyar mahaukaciyar ce wacce bata damu da tattalin lafiyar jikinta ba."

"Duk abin da za ka faɗa go ahead ba zan hanaka ba, fita da mota nan ce dai ba za ka yi ba. Maza ka bani key ɗin hannunka kana ɓata min lokaci kuma ka ga ina da baƙo."

Ta ƙarashe magana tare da tara masa tafin hannunta, sosai Tareeq yake sheƙa dariya sai da ya

yi mai isarshi kafin ya ɗage gira sama tare da cizon gefen leɓɓen shi na ƙasa yana kallon Fadila tunani yake ta ina zai fara illata ta yayin da ta shamma ce shi da nufi ta wafce key cikin rashin sa'a yai sauri janye hannunshi, hakan da tayi ba ƙaramin ƙara fusata shi ya yi ba cikin zallar ɓaci rai ya dube ta da idanuwanshi da suka fara sauya launi gami da daka mata tsawa yana faɗin "Ya Fadila I'm warning you stay away from me tun muna sheda juna wallahi-azim idan ki ka yi yunkuri hana ni fita da motar da ubana ne ya zuba kuɗinsa ya siye bai kuma taɓa yi min shamaki da ita ba. To kuwa ba abin da zai hana ni bi ta kanki na taka ki ba abun da za a yi dan na taka banza gwara tun wuri ki yi ta kanki rashin mutuncina ya girmewa naki."

Zaro idanuwa Fadila tayi cikin kaɗuwa za ta yi magana ya ƙara daka mata tsawa yana zare mata manyan idanuwanshi "Don't ever tested my patience just get out of my way."

Wani kallon banza Fadila ta shiga yi masa kafin tayi ƙwafa tare da kyasta yatsunta ya bada sauti ƙasss....ƙasss! "Ka jira za ka ga abin da zai biyo baya kuma In-sha-ALLAH yadda ka yi min sai ALLAH ya ba ka ƴaƴa da za su ma fiye da abin da ka yi min ɗan iska yaro marar tarbiyya ALLAH ya haɗa ka da dai-dai da kai."

"Dallah bani hanya Malama ko uban waye ya faɗa miki zan yi aure balle har na haifi ƴaƴa, sai dai ke ki haifa min nai ta cin ubansu."

Ya ƙarasa magana tare da buɗe ƙofar mota ya shiga yai mata key da ƙarfi ya shiga yin reverse, kamar zai taka Fadila tai sauri yi tsalle ta koma gefe tai tsaye tana kallonshi da idanuwanta da suka fara tara ƙwalla saboda ta ji zafin rashin kunya da yai mata musamman da ta waiga wajen da Isma'eel yake tsaye ta ga hankalinsa ya tattara ne akansu.

A hankali Tareeq ya sauke gilashi yai ƙasa ya leƙo da kansa yai mata waving haɗe da gwalo, ya ƙara figar motar da gudu tuni aka wangale mai gate.

Yana fita kai tsaye ƙofar gidansu Roonie ya nufa horn ya shiga dannawa sai ga Roonie da Lil-prince sun fito cikin shigar english wears, ya kwashe su suka nufi wani farm house na mahaifin abokinsu Sasco can bayan gari wuri daji ne sosai anan za su gudanar da birthday party da Sasco ya shirya wa girl friend ɗinshi.

Fadila tasa gefen gyaleta ta goge fuskarta dashi kafin ta koma wajen da ta baro Isma'eel, tana wani murmushi yaƙe "Babe mike faruwa ne naga kamar kuna sa-in-sa da Tareeq?"

Isma'eel ya faɗa yana kallon cikin idanuwa Fadila tare da karantar yanayi da take ciki.

#Tareeq

#Fadila

#isma'eel

#Rooney

#Lil-prince

#team TareeqImam.

Aayya ta ce a gayamuku kada ku shagala da karanta Free page ku manta da na kuɗi ne😂

Ta ce ga masu buƙatar ci-gaba da karanta wannan littafi za su biya 700 kacal ta wannan asusun banki 7032566272 Hauwa Shehu opay. Aayya tayi arha ta hana bashi dan haka ku hanzarta ku nunawa shalelenku Tareeq ƙauna, duk da Tareeq yace a baku part one kyauta amma part two kun dai gane, kusan Tareeq ɗan albarka ne yana yin ku.

Jeeddah Aliyu

07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

008.

Wata irin mashahuriyar kunya ce ta lulluɓe Fadila ta shiga kame-kame ta rasa wacce irin karya za ta sharārawa Isma'eel da ba zai gano cin mutuncin da ƙaramin ƙaninta ya gama yi mata. Can kuma ta dake ta shiga faɗar "Sa-in-sa fa haba Tareeq ne zai tsaya yana musanya yawu dani sai kace wata sa'arshi kawai dai faɗa nake mai."

"Amma kuma Fadila sai naga kamar saura kaɗan ya bi ta kanki da mota wallahi ba ki ji yadda gabana ya shiga dukan uku-uku ba?"

"Uhmm... na gayama faɗa nai masa akan ya cire haircut ɗin kanshi shine fa ya ji haushi ya ja mota da ƙarfi."

"Gaskiya kam gwara da ki ka yi mai faɗa domin duk yaro mai cikakkiyar tarbiyya bai kamata a dinga bari shi yana irin wannan haircut ɗin ba,sam babu daraja a cikinsa sannan kuma Fadila sai nake gani rashin dacewar sakarwa da Tareeq manyan motoci, shekarunsa bai kai da zai dinga hawa tsadaddun motoci ba irin wannan.

Har yanzu fa Tareeq bai kammala makarantar sakandare ba. Hakan fa zai iya shafar karatu da tarbiyyarshi, uwa-uba ga surutun da mutane za su dinga yi akai hakan zai iya taɓa gobensa da ƙimar mahaifin ku saboda da yawa waƴansu mutane bakinsu bashida kyau, shiyasa ake so a dinga taka tsan-tsan.

Amma ki yi haƙuri da katsalandan da nai miki naga ni dake muna gaf da zama abu guda in fact ƙaninki nima ƙanina ne."

Jikin Fadila ya yi sanyi tabbas duk abin da Isma'eel ya faɗa babu karya a ciki, sai dai ita ɗin bata da power ɗin da za ta sa ko ta hana Tareeq hatta da ummi da ta tsuguna ta haife shi baya jin maganar ta balle ita karan kaɗa miya. Ta ja gwaron numfashi tare da saukewa kafin ta ce "Isma'eel kasan halin yaran zamani nan musanman Idan suna farko balaga sai sun yi Irin wannan rawar kan amma wallahi dukkan mu muna iya ƙoƙari akan inganta tarbiyyarshi kuma In-sha-ALLAHU zan yi magana da Daddy ba zai sake fita da mota ba."

"Madallah hakan zai fi gaskiya musamman yanzu da muke fuskantar insecurity a ƙasar nan, ɓata gari sun yi yawa duk wani shige da fice shi su na lura dashi. Fatan mu ALLAH ya kiyaye ya kawo mana saukin waɗannan masifun da muke ciki."

"Amin ya hayyu ya ƙayyum!

Fadila ta faɗa cikin sanyi murya da mutuwar jiki. Kana su ka ci-gaba da firar su. Sai around 10:30 Isma'eel ya wuce kai tsaye ɗakin Ummi Fadila tai wa tsinke koda ta shiga Ummi tana bathroom "Ummi.... Ummi...!

Ta shiga kwalla mata kira Ummi ta buɗe ƙofar bathroom ta fito, jikinta ɗaure da matsakaici towel.

"Kanki ɗaya kuwa Fadila me kike nema ne da ba za ki iya haƙuri na fito daga banɗaki ba?"

"Yi haƙuri Ummi abin da ke cina ne a zuciya na kasa jurewa."

Gefen gado Ummi ta nufa ta zauna kana ta dubi Fadila ta ce "Mene ne ke cin ki a zuciya da ya haddasa miki yi min kalar wannan kiran makafi?"

"Ummi Tareeq ne...

"Innalillahi wa'inna illahim raji'un!

Ummi tai saurin katse Fadila yayin da zuciyarta ke wani irin bugawa, fargabar ta ɗaya a wannan karo batasan me kuma Fadila za ta ce Tareeq ya aikata. Zuciyarta na ɗarr-ɗarr ta ce "Fadila me

Tareeq ya sake aikatawa kuma?"

"Ummi wannan new car ɗin na Daddy me mahaukacin tsadar nan Mercedes Benz G-class Tareeq ya ɗauka ya fita dashi...

"Kai Fadila Yanzu fissibilillahi saboda mota ne ki ka haifar min da wannan firgici?"

"Ummi ba ki san mahaukatan kuɗi da mota yake dashi bane."

"Ko nasani me zan yi Fadila kina sane da duk abin da Tareeq yake yi a gidanan mahaifinku ne ya bashi goyo baya da yanzu za ki ɗaga waya ki kira shi ki kai mishi korafi akan Tareeq ya fita da motarshi wallahi shakka babu sai ya yi miki zagin ƙare dangi. Saboda haka ki kauda idanuwanki akan duk abin da ya shafi motocin Daddynku ba ruwanki can ta matse musu ai sun fi kusa."

"Ni a ganina Ummi bai kamata ki biyewa fushin zuciya ba gwara ki taka mai birki saboda ba mu san abin da yake fita aikatawa da motar ba."

"Fadila don ALLAH tashi ki fita ina buƙatar privacy zan kimtsa jikina."

Ummi ta faɗa cike da kosawa da zancen Tareeq.

Jimm... Fadila tai tana kallon Ummi kafin ta gyaɗa kai ta fice.

Wani irin kiɗa ke tashi na fitar hankali a farm house ɗin samari da ƴan mata ne dukka teenagers ke cike a wuri wasu na dirkar rawa wasu kuma sun keɓance kansu a gefe su na taɓe-taɓe da tsotse-tsotse hankalinsu kwance yayin da ƙalilan ne daga cikinsu ke fira tare da zuƙar shisha.

Tareeq yana ɗaya daga cikin masu shan shisha cike da kwarewa yake zuƙa, hayaƙi ke fita ta baki da hancinshi.

Ɗaya daga cikin friends ɗin bithdaya girl mai suna Raheela ta baro filin rawa ta nufo wajen su Tareeq, jikinta sanye da wando jeans haɗe da rigar armless wacce da kaɗan ta wuce cibiyar ta sai ɗan wani yalolo veil da ta yane kanta dashi, Raheela kyakkyawa ce ajin farko tana da ƙirar jiki mai matuƙar jan hankali kujerar da ke kallon Tareeq ta zauna "Hi guys!

ta faɗa sa'ili da ta dosana duwawunta a kujera.

"Hi...!

Ɗaya daga cikin su Tareeq ya amsa mata a takaice, ta tsare Tareeq da idanuwanta jikinsa ya bashi ana kallonshi ya ɗago ya kai dubanshi wurinta ta sakar mai ƙayatatcen murmushi tana lumshe idanuwanta kana ta buɗe su a kansa. Da sauri Tareeq ya mayar da duban shi kan Lil-prince da ke bashi labari.

Cikin kwantar da murya Raheela ta furta "Slugger wurinka na zo idan ba damuwa inaso mu keɓe ina ɗauke da magana mai muhimmanci a bakina da fatar za ka bani dama?"

Ɗagowa ya yi a karo na biyu ya sake kallonta ya taɓe baki tare da yin kici-kici da fuska batare da ya ce komai ba ya ci-gaba da zuƙar shisha ɗinshi, Lil-prince ya ɗan zungure shi da ƙafarshi Tareeq ya kalleshi alama Lil-prince yai mai da ya saurare ta, sai da ya gama ja mata aji kafin ya miƙe cikin tafiyarshi ta ƙasaita ya nufi wajen da yai parking ya jingina jikinshi ga mota tare da harɗe ƙafafuwanshi wurin ɗaya ya kuma yi folding hannuwanshi a kirji, Raheela tai tsaye gabanshi tana kallansa tana murmushi.

"Ki gaggauta faɗar maganarki domin ina da abin yi ban cika son a ɓata min lokaci ba."

Cewar Tareeq yana ƙara tanke fuska.

Ajiyar zuciya Raheela tai kafin ta ce "ina so mu ƙula alaƙa ta soyayya domin tun ranar farko da idanuwana sukai tozali da kyakkyawar fuskarka a wurin birthday party ɗin Faruq Abdulwahab Bichi zuciyarta ta kamo da azababbiyar soyayyarka, Don ALLAH kada ka ce min a'a domin faɗar hakan daga bakinka zai iya haifar da mummunan illa ga lafiyata."

Murmushin gefen baki Tareeq ya yi wanda ya ƙara masa bala'i kyau tare da sake ƙarewa Raheela kallo cike da jan aji ya ce "Gaskiya ba zan ɓoye miki ba zuciyata tamkar dutse ce bata da muhalli na soyayya, zan dai iya ɗaurewa na karɓe ki a matsayin friend with benefits."

"Dan ALLAH Tareeq kada ka yi min haka wallahi-tallahi zuciyata ta kamo da matsananciyar ƙaunarka, Please kar ka watsa ƙasa a ido.

"Ashe kuwa kina cikin wahala don ni bana soyayya idan har ba ki amince da mu yi ƙawance ba,tare da samar wa junan mu da natsuwa za ki iya ƙara wa gaba, duk lokaci da ki ka ji kina sha'awar mu ragewa junan mu zafi I'm always there for you."

Ya ƙarashe magana tare da juyawa wa da sauri ta sha gabanshi, ta wani kalar langwaɓar da kai gami da haɗe tazarar da ke tsakaninsu, kana ta riƙo hannunsa ta matse cikin nata, tsikar jikin Tareeq ta tashi yarrr... cike da kwarewa da yaudara Tareeq ya ɗora hannunshi a ƙugunta ya jawo ta ya mannata a ƙirjinshi, Raheela bata hana shi ba saboda ta daɗe da tsunduma cikin ƙogin sonshi kuma wannan ba shine karonta na farko da namiji ya fara taɓa ta, a hankali ya cire hannunshi daga ƙugunta ya ɗago haɓarta ya yi connecting lips ɗin su ya shiga kissing ɗin ta passionately, ƙafafuwan Raheela kasa ɗaukar ta suka yi sakamakon yadda jikinta ke ɓari da baya-baya ya dinga tafiya yayin da yake ci-gaba da shanye mata baki har ya isa ga mota ya mannata, hannuwanshi duka biyu yasa yana squeezing kirjinta ta cikin rigar jikinta ba ka ji komai sai moaning ɗinsu sosai Raheela ke jin daɗi yadda yake murza mata kirji kasancewar rigar ta ta mai gajeren hannu ce ya bashi damar zura hannunshi ta armpit ɗinta ya riƙo matasan boobs ɗinta guda cikin sa'a bata saka bra ba, jin yadda tattausan tafin hannunshi ya sauka akan ƙirjinta yasa ta ɗimauce baki ɗaya sosai ya rikita mata lissafi sai ƙara ƙanƙame shi take yi tana turo masa ƙirji Tareeq ya kwadaitu da son ya tsotsi ƙirjin nata cikin kunnenta yai mata raɗa da rikitatciyar murya "Baby let enter the car and feed me with your sweetest twins."

Kafin ta lallaɓo amsar bashi har ya fito da car key daga aljihunshi yai using da remote ya buɗe

motar, ta backseat ya tura Raheela ya bi ta kana ya rufe ƙofar jikinshi na mugun rawa ya kama rigar jikinta ya cire kamar wani mayunwacin zaki ya kama kirjinta dukka biyu ya cika hannunshi ya matse su a tare suka ja gwaron numfashi, kafin ya kafa bakinsa a nipples ɗinta ya shiga zuƙa idan ya sha wannan ya koma kan wannan haka ya dinga yi tun Raheela tana jin daɗi har ta fara jin bala'in zogi abin ka da nonuwan budurwa kuma wannan shi ne karo na farko da aka taɓa shan su iyakancita a taɓa su amma ko kaɗan bata bari a sha yayin da Tareeq sai zuƙa abinsa yake ƙoƙarin ture shi take yi laɓɓanta na rawa ta ce "Slugger ya isa haka dan ALLAH ka bari wallahi zafi nake ji."

Tamkar ƙara zuga shi take don kuwa sai ƙara cika bakinshi yake matuƙar Tareeq ya ga nono haukacewa yake saboda bala'in mayensu ne, shi dai idan zai sami su sun wadatar dashi.

Raheela ido ya rena fata sai gata ta dawo tana magiya "wayyo ALLAH zafi Slugger za ka tsinka min su don ALLAH ka yi a hankali... Tareeq Please ka bari haka nan, ni gida zan tafi idan nayi dare sosai wallahi mom dukana za ta yi."

Ta ƙarashe magana hawaye azaba na bin kumatunta, Tareeq bai bi ta kanta ba shagalinsa kawai yake sai da ya ji ya sami gamsuwa ya fitar da abin da ke maƙale a mararshi sannan ya ji natsuwa ta zo masa, ya daidaita numfashinsa ya langwaɓar da kai yana kallonta ta hasken light ɗin da ya kunna na mota "Ya sunan ki?"

Ya faɗa yana wani shegen blushing, kallo Raheela ta bi shi da shi kafin ta furta "tun farko ya kamata kai min wannan tambaya ba sai da ka gama biyan bukatar dani ba."

Ta ƙarasa magana tare da murguɗa baki tana ƙoƙarin mayar da rigar ta, murmushi Tareeq ya yi cike da shaƙiyanci ya ce "To ai Baby ke ɗin zazzafa ce tsananin zafin naki ne ya hanani tambayar sunanki ki ɗaure ki faɗa min kada ki tsaya jan aji, domin ko kin ja baya tasiri akaina."

Sai da ta fice daga motar kafin ta ce "Raheela Ibrahim mai iyali.

"Wow what a nice name, please can I get your phone number?"

Tareeq yai magana yana wani lumshe idanuwa sha'awar sake shan kirjinta na sake ratsa dukkanin jikinshi ji yake tamkar ya sake cafko ta duk da ba wannan ne karon shi na farko da ya fara shanye nonuwan ƴan mata ba, dan ya saba da shan na Roofy Sodangi da Afrah Abdallah har sai ma ya gaji don kanshi ya daina amma na Raheela daban suke ga su suna da girma ba kamar na Roofy da suke ƙananuwa sosai ba.

Karɓa wayarta ya yi ya saka mata digit ɗin shi tare da furta "Na ji daɗin haɗuwa da ke Raheela ina fatar haɗuwa mu ta gaba ta fi wannan daɗi da armashi."

Murmushi tayi tana wani rangwadar da kai "kar ka damu my slugger zuciyata da gangar jikina dukka naka ne sai yanda ka yi dasu na mallaka maka su kai kaɗai."

"A'a Baby kyautar ta yi min yawa ni kaɗai ki bar zuciyarki kawai gangar jikin ta wadatar da ni,

idan zan ci-gaba da mallakar jikinki bana jin ina da buƙatar zuciyarki."

Ɗora hannu Raheela tai akan laɓɓanta tana kallon Tareeq dake kishingiɗe yanayin da yai magana yai bala'in sanyayya mata jiki, kasa furta uffan tai ta juya ta nufi ainihin idan ake gudanar da party ɗin.

Ya yi murmushi tare da maida bottoms ɗin rigar shi, basu baro wurin ba sai misalin ƙarfe 12:30 na dare akan hanyar su ta zuwa gida Tareeq yake basu Rooney labari yadda ya kwashe gara a wajen Raheela gaba ɗaya suka ɗauki sowa suna tafawa tare da jinjina mishi "our highness kace yau kashe daɗin ka ba kai fitowar banza ba abokina."

Cewar Lil-prince yana dariya rashin ɗa'a.

"Bari kawai Lil daɗin har baya misaltuwa, jin nai kamar na kwana ina shagalina ko in cinyesu baki ɗaya kai Raheela ta haɗu abubuwan ta ba dai laushi da garɗi ba."

Dukkansu suka kwashe da dariya da haka ya sake kowanne su a ƙofar gidansu sannan ya nufo gida, horn ɗaya zuwa biyu security ɗan Bala ya buɗe mai gate ya nufi parking lot ya yi parking ya fito tare da rufe motar ya nufi entrance yana fito bai bi ta main parlour ba ya bi ta ainihin ƙofar shiga part ɗinshi, firstly wanka ya fara yi har zai bi lafiyar gado ya ji wata irin yunwa ta taso mai sai nuƙurƙusar hanjinsa take ba zai iya jure kwana ba tare da ya saka wani abu a cikinsa ba, ya cire towel ya maye gurbin sa da boxer ya fice. Ya bi ta corridor dake kai shi da part ɗin Ummi direct kitchen ya wuce ya kunna ruwan zafi a kettle da ya tafasa ya haɗa tea mai kaurin gaske ya buɗe fridge ya ga cup cakes ya fito dashi ya saka a microwave ya ɗumama.

Fadila ta fito daga ɗakinta ta nufo kitchen za ta sha ruwa saboda na fridge ɗin ɗakinta ya yi ƙanƙara, tun kafin ta ƙarasa kitchen ɗin ta hango Tareeq gaban microwave dai-dai ƙofar kitchen ta tsaya tare da tokare bakin ƙofar da hannuwanta biyu jin motsi daga bayanshi yasa shi juyawa da sauri a zato shi ko Ummi ce dake dakonsa, ya haɗa ya idanu da Ya Fadila da ke mishi kallo mai cike da zallar tuhuma "mtsss....!

Ya ja guntun tsaki kana ya buɗe microwave ya ciro container da zuba cake, ya juye a plate ya riƙo mug ɗin tea ɗinsa a hannu ɗaya yayin da ɗayan hannu ke ɗauke da plate ɗin cake.

"Daga ina kake Tareeq kasan kuwa ko ƙarfe nawa yanzu?"

Ya Fadila ta tambaya tare da shigowa cikin kitchen ɗin tai tsaya gabansa tare da tsare shi da idanuwanta.

Mugun kallo ya watsa mata yana faɗin "Ina ruwanki da ni wai miyasa ki ke saka min ido da yawa a al'amurrana Ya Fadila?"

"Saboda kai ɗin ƙanina ne ba zan ji daɗi ba idan wani mummunan abu ya same ka."

"Uhmm....!

Tareeq ya faɗa yana bin ta da kallon reni wayau, "look Ya Fadila Kar ki renawa kanki hankali ki nemi ki rena min tun wuri ki daina nuna wannan kulawar taki ta munafuci akaina."

Ya yi magana tare da raɓawa ta gefen ta zai wuce cikin zafin nama ta danƙo damtse hannunshi ta dawo dashi gabanta.

"Dawo nan ɗan Iska yaro I'm not finish yet with you tun da na fahimce hanyar lalama bata bi da kai to ka buɗe kunnenka da kyau ba zai yiwu ka ɓata mana sunan gida ba, kai ɗin guda nawa ne Tareeq da za mu kasa bi da kai?"

Ya ɗage girar ido yana kallon namijin ƙoƙarin da tai na riƙe mai damtse hannu, kafin cikin gatsali ya ce "To naji my second mom sai ki sake min hannu yunwa nake ji."

"Ba wai ka ji za ka ce ba ka tabbatar abin da na faɗa ya shiga cikin kunnuwanka."

Ta ƙarasa magana tare da sakin hannunshi, murmushi gefen baki ya yi ya fice daga kitchen ya wuce dining room ya zauna yana cin cake tare da sipping tea ɗinsa. Ya Fadila ta fito daga kitchen riƙe da water bottle ta dube shi tai ƙwafa kana ta nufi ɗakinta, ya bi ta da mushirikin murmushi sai da cikinsa ya cika ya koma ɗakinshi.

Washegari da wuri ya yi shirin tafiya school kamar dai yadda ya yi jiya, yana fitowa dai-dai kofar entrance ya haɗu da Ummi kunshe dariya dake ƙoƙarin subuce masa ya yi domin yadda Ummi ta haɗe fuska ta tsare hanya kamar wata dogari yai masifar bashi dariya, hannunsa ta damƙa ta jawo shi zuwa ɓangaren ta.

"Ummi Dan Allah ki yi haƙuri ba zan sake ba dan Allah Ummi kar ki dake ni wallahi ba zan ƙara aikata abin da bakyso ba. Ummi Please am sorry...

Sauran kalaman shi suka ƙargame a maƙoshinsa sakamakon cilla shi da Ummi tayi cikin bedroom ɗinta ta kuma rufe kofa haɗe da murza key.

Ba wai yana jin tsoron dukanshi da za tai ba kawai dai a can ƙasan zuciyarshi baya jin daɗin yadda kullum yake sa ta cikin ɓaci rai.

"Ummi ki yi haƙur....

Saukar mahaukacin mari ya ji a kamatunsa shine ya hana shi ƙarasa fadar abin da yake ƙoƙarin cewa.

"Yimin shiru ɗan Iska kawai mai kunne ƙashi uban me Tahreem tai ma da ka fasa mata goshi?"

Ummi tai tambaya ciki daka mai tsawa.

Tareeq yana dafe da kumatunshi da ta mara ya kasa magana sai shafar gun yake yi.

"Tambayar ka nake ka bani amsa dan ubanka!

Ta faɗa gami da sake daka masa tsawa wacce ta fi ta farko razanarwa.

Still dai bai ce komai ba sai tsare ta yai da idanuwanshi.

"Daina kallona da shegun idanuwanka masu kama da na ubanka, kuma bari ka ji duk ranar da ka sake sauke hannunka akan Tahreem sai na raunata ka wallahi."

Ya ja da baya da sauri yana kallon Ummi da fuskantar da ta bayyanar da gaskiya abin da ta faɗa tana nufi hakan har cikin zuciyarta.

"Ummi miyasa bakya sona miyasa a duk lokaci da na ɓata miki ba za ki yi min nasiha ki lurar da ni cikin tausasawa, sai dai ki ta zagina kina dukana?"

"Rufe min baki ɗan iska yaro kai ɗin ne ka ke jin nasiha ai tun da duka bai yi tasiri hanaka aikata tsageranci ba bana tunani nasiha za ta yi tasiri akanka Tareeq."

"Don ALLAH ki yi min addu'a Ummi wallahi idan kina min addu'a watarana zan daina."

Ya ƙarasa magana cikin karyewar zuciya hawaye na bin kumatunshi.

Harara ummi ta watsa mai tare da nuna ƙofar "maza fice ka bani wuri ai ba kai kaɗai na haifa ba da zan tsaya ɓatawa kaina lokaci ina ma addu'a ka je can ubanka da ya fifita ka da sauran ƴaƴanshi yai ma addu'a ba dai ni Amina ba."

Jikin Tareeq yai mugun sanyi ya ji wani irin ƙololo ya tokare mai maƙogwaronshi, ya soma tafiya cikin wani irin yanayi mai wuyar fassara wa ya murɗa key ya fice daga ɗakin. Duk abin da ya faru a kunne Fadila domin tun lokaci da ummi ta jawo Tareeq ta fito daga kitchen ta biyo su kafin ta ƙaraso ummi ta ƙargame kofa shine tai tsaye jikin ƙofar ɗakin tana sauraren su, Tareeq yana fitowa yai tozali da ita kallon da ya ga tana bin sa dashi ya kasa jurewa yai saurin nufar ɓangaren Aayya, yana zuwa ya faɗa jikin Aayya ya fasa kuka tamkar ƙaramin yaro.

"Innalillahi wa'inna illahim raji'un....! Tareeq me kake wa kuka ba dai Imamu ne ya riga mu gidan gaskiya ba?"

#TareeqImam

#Soyayya#Rikicin#zumunci

#Nadama#son maso wani#

#Butulci#BoyayyenSirri.

Aayya ta ce a gayamuku kada ku shagala da karanta Free page ku manta da na kuɗi ne😂

Ta ce ga masu buƙatar ci-gaba da karanta wannan littafi za su biya 700 kacal ta wannan asusun banki 7032566272 Hauwa Shehu opay. Aayya tayi arha ta hana bashi dan haka ku hanzarta ku nunawa shalelenku Tareeq ƙauna, duk da Tareeq yace a baku part one kyauta amma part two kun dai gane, kusan Tareeq ɗan albarka ne yana yin ku.

Jeeddah Aliyu

07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

009.

Duk tarin tambayoyin da Aayya take mai ya kasa amsa ko ɗaya gani haka yasa ta ture shi daga jikinta ta miƙe tsaye tare da ɗora hannuwanta aka ta zunduma ihu mai ƙarar gaske tare da fashewa da matsanancin kuka ta shiga sambatu "wayyo ALLAH na shiga uku shi kenan na rasa ka Imamu miyasa mutuwa za tai min haka miyasa ba za ki fara ɗauka na ba kafin ki ɗauke min ɗan kirki Imamuna shi kaɗai ne mai jinƙai na shikenan ni da kai Tareeq mun zama marayu."

Jin irin maganganun da ke fitowa daga bakin Aayya ya saka Tareeq miƙewa tare da cire ƙatuwar backpack ɗinshi dake goye a gadon bayanshi, ya sauke ta ƙasa kana ya nufe wajenta fuskarsa ɗauke da ɗimbin mamaki. Tuni ihunta ya karaɗe illahirin gidan. Ummi, Fadila, Baby har ma da Gifty da gudu suka shigo ɗakin nata yadda take kuka bil-haƙƙi da gaskiya yasa hanta cikinsu kaɗawa, sai komawa gefe Tareeq yai tare da harɗe hannuwanshi a ƙirji yana kallon ikon ALLAH.

"Subhanalillah!Aayya kukan me kike yi don Allah ki faɗa mana me yasa kike wannan kukan na fitar hankali?"

Cewar Ummi tana riƙo hannun Aayya kafin Aayya tai magana Fadila tayi karaf ta ce

"Wai kai Tareeq ba ka da baki ne da ba za ka faɗa mana takamaiman wannan uban ihu da kururuwa da ta cika mana gida dashi?"

Ko kallon gefen da Fadila take Tareeq bai yi ba sai ma wani kalar ɓata fuska da yake.

Sake fashe wa da sabon kuka Aayya tai cikin gunji kuka ta taƙarƙare tana faɗar "Yanzu nan wasu mutane da basan ko su waye ba suka kira wayar Tareeq suka faɗa masa mummunan labari....

Ta kasa ƙarasawa saboda kukan da yaci ƙarfi ta.

"Kai Tareeq wane iri mummunan labari ne aka faɗa maka da ba za ka iya buɗe baki ka faɗa mana ba ka bar mu da Aayya sai ƙara tadda mana hankali take kayi mana bayani duk fargaba da tashin hankali ya cika mu?"

Cewar Baby yayin da ƙirjinta ke wani irin bugawa.

Taɓe baƙi Tareeq ya yi tare da kallonsu ɗaya bayan ɗaya da idanuwanshi da suka fara canza launi a dalili kukan da ya yi.

Karaf Aayya ta karɓe zance ta hanyar cewa "dukkanmu mu taru mu rungume ta Annabawa duk mai rai dai mamaci ne wanda ya ba mu Imamu jiya da dare ya karɓi abinsa.

"Innalillahi wa'inna illahim raji'un...!

"Hasbunallahu wal-imal wakil!

"La'ilaha illallahu Muhammadur Rasulullah Sallallahu alaihi Wasallam!"

Kusan kowanne su da abin da yake faɗa har ba ka iya tantance muryoyin su, tuni su Fadila su ka fara ɓaɓɓaka kuka. Hatta da Ummi da ke jin ƙiyayyar Alhaji Imam Wali a zuciyarta sai da ta ji wani irin tashin hankalin bazata ya ziyarce ta, wani mashi ya daki ƙahon zuciyarta batasan lokaci da ta dafe ƙirjinta da dukkan hannuwanta saboda tsananin firgici sai da idanuwanta suka firfito.

"Mtsssss! Tareeq ya ja dogon tsaki ya wafce backpack ɗinshi cike da takaici ya kalli su ummi ya sake kallan Aayya, jin yadda ya ja tsaki yasa suka tsagaita kukan da suke su kayi tsittt tamkar an yi ruwa an ɗauke sai kawai suka kakkafe shi da idanuwa alamar suna jiran ƙarin bayani daga bakinshi, dan sun tabbatar abin da Aayya ta faɗa ba gaskiya bane don da gaskiya ne da sai Tareeq ya fi kowa shiga tashin hankali a gidan sai gashi kuma ya bige da bin su da tsaki gami da kallon banza.

"Gaskiya dukkan ku ba ku da hankali haka kawai wannan ruɗaɗɗiyar tsohuwa memory lost za ta tsira haukanta ku kuma sai ku biye mata ni ko kusa ban faɗa mata Daddy ya rasu ba. Ba tare da kwakwaran bincike ba kun bi kun cikawa mutane gida da kukan ku na banza da wofi."

Ya yi magana cike da rashin kunya yana mai galla musu harara.

takaici ya rufe Fadila ta kalle Aayya da take ji kamar ta rufe ta duka ta ce

"Haba! Aayya wannan wane irin ɗaukar al'hakki ne? Gaskiya ki dinga tantance magana kafin ki yaɗa ta kalli yadda kika tashe hankulan mu."

"Miye laifin Aayya anan kika san abin da wannan taƙadarin ya faɗa mata, kina ma jin abin da ya faɗa dukkan mu mahaukata ne har ni bai cire ba."

Ummi tai magana cike da zallar takaicin rashin kunyar Tareeq.

A fusace ya dau backpack ɗinshi ya nufi ƙofar fita da ƙarfi Fadila ta jawo collar rigar uniform ɗinshi ta baya "Dawo nan don ubanka rashin mutuncin da za ka shuka mana da sanyin safiyar nan ko? wato ka yi mahaukata da mu to kuwa za ka ga aikin hauka gani idonka wallahi, don taro dangi zamuyi maka mu lakaɗa ma shegen duka da sai ka manta da sunanka."

Fadila ta ƙarasa magana tana huci..

Kallon mai cike da reni ya fara aika mata kafin ya fincike daga riƙo da tai mai "Dallah!malama cikani tun kafin na darza miki rashin mutunci, ke har kina da zarrar duka irina ni da kodayaushe cikin neman fitina nake ido buɗe duk shegiyar da take gani ta cika ta gwada dukana na rantse da ALLAH agaban uwarta zai shemi ta."

"Cika shi Fadila bar shi kawai duniya ce tafi bagaruwa iya jima."

Ummi ta faɗa da rai ɓace don ta tabbatar abin da ya faɗa ba makawa zai aikata.

"Mtsss...!

Tareeq ya ja dogon tsaki ya nufi ƙofar fita yana gunguni da ƙarfi ta yadda za su iya jin sa.

"Aikin banza da kar ta sake ni da na nuna mata ko ban da uwa a gidanan na fi ƙarfi a ci min collar, Kuma wallahi duk ƴar iska da ta sake gigin shiga sabgata sai na ɓalla ƙashin wuyanta shegu ƴaƴa magge."

Da kallo Ummi ta bishi dashi yayin da zuciyarta ke wani irin bugawa da ƙarfi tamkar za ta ɓalla ƙirjinta ta faɗo ƙasa, sosai take ƙara jin tsanar ɗan nata. Musamman da ta ji ya sheganta mata ƴaƴa ya kuma kira ta da suna magge.

Aayya wacce tun lokaci da ta ji amsar da Tareeq ya ba wa su Ummi, ta share hawayenta. Cikin fusata ta daka musu tsawa ta tana faɗin "Wai nikam uban me ya shigo min da ku zoga guda a ɗaki, sai kace na aika muku da katin gayyata, ni shikenan banida sirri."

Cike da zallar takaici kowanne su yake kallonta, Baby ta ce "Ni dai wallahi an ɗauki haƙƙina kuma ALLAH ya isa ban yafe ba, haka kawai don salon zalunci ki dinga kururuwa da sassafe duk ki bin kin daga mana hankali....

"Ke Baby!

Ummi ta tarin numfashinta cikin tsawa gami da nuna musu ƙofar fita "Ku fita.

Baby ta ri ga Fadila da Gifty fita a dalilin yadda taga ran Ummi ya yi masifar ɓaci, tana gudun kada ta sauke fushinta akanta.

"Aayya Dan ALLAH ki dinga lissafi da ƙwaƙwalwa yanzu ina amfani irin wannan ki bin ki mayar da kanki tamkar wata ƙaramar yarinya fissibilillahi abin da kika aikata ko Tahreem dake ƙarama a gidanan ba za ta aikata kwatankwacin shi ba."

Aayya ta murtuƙe fuska tana faɗi "Ba shakka reni ya shiga tsakanina da ke Amina har ni za ki kalli tsabar idona ki danganta ni da Tahreem ba komai Allah ya dawo da Imamu gidanan duk ɗibar albarka da ki ke yi min ke da marar kunya ƴaƴanki tass a kunnenshi."

Zazzafar numfashi Ummi ta sauke tsananin takaici yasa ta juya ta bar ɗakin ba tare da ta sake tankawa ba.

Tareeq yana fita ya tadda direbanshi yana zaman jiran fitowar shi, tun kafin ya isa wajen mota Attahiru dake zaune a bakin gate ya rugu ya buɗe mai ƙofa dan Dan Bala ya shiga banɗaki fuska a murtuƙe Tareeq ya raba shi ya shiga motar yayin da Attahiru sai zuba masa kirari ya ke Tareeq kam ko kallo bai isheshi ba sai faman cin rai yake malam Musa ya ja motar gami da gaida Tareeq shima banza ya yi dashi 8:33am dai-dai ya iso cikin makaranta a maimakon ya shiga class sai kawai ya nufi wani waje da aka tanada domin hutawar ɗalibai ya zauna ya ajiye backpack ɗinsa akan kujerar da ke kusa dashi, sai rarraba idanuwa yake a harabar makarantar can ya hango direban Ummi ya sauke Gifty wacce ta kwana biyu bata zo ba a dalilin rauni da yai mata direban ne ya fito ya buɗe mata ƙofa ta fito kana ya miƙa mata schoolbag da lunch pack ɗinta, ya koma mota ya yi reverse ya nufi gate ɗin fita. Da kallo Tareeq ya bi ta dashi yadda ya ga tana tafiya cikin natsuwa sai zabga murmushi take bai ɗauke idanuwanshi akan ta ba har sai da ta shige ajinsu primary 2 a da tare suke zuwa Malam Musa ke kawo su tsananin cin zalunta da yake da mugun duka da yake mata ba laifin zaune balle na tsaye yasa Ummi ta raba musu mota shi ya bi direbanshi Gifty kuma direban Ummi kawo ta, tun lokaci da aka raba musu mota ya rage zaluntar ta duk da ba daina wa ya yi gaba ɗaya ba. sauke numfashi ya yi gami da ƙara tallabe kumatunshi ya ƙara nusawa a tunani a rayuwarshi duk abin da yake aikatawa nishaɗi yake haifar mai ba kaɗan ba a wasu lokuta da dama yana shiga tunani kwatankwacin wannan ko da zai yi katari da dalilin da yasa Ummi da ƴan uwansa suka tsane shi.

Jikinshi ya bashi cewa ana kallonshi a hankali ya bi da idanuwanshi gun da yake tunani mai kallon nashi yake, Nana ya gani ta kafe shi da idanuwanta masu matuƙar jan hankali tayi folding hannuwanta yadda tai mishi ƙurrr da idanuwa zai tabbatar maka ba ƙaramin enjoying take na kallonshi. Tareeq yai saurin kawar da kanshi wani gun daban. Still yana ci-gaba da jin idanuwanta na yawo a jikinsa after few seconds ya sake waigawa gefen da take tsaye sosai ya haɗe rai wani mugun haushinta yake ji musamman da ya rasa dalilinta na tsare shi da mayyen kallo "mtsss....ya ja ɗan siririn tsaki gami da miƙewa tsaye yai miƙa haɗe da doguwar hamma

yayi amfani da tafin hannunshi ya kare hamma ɗin, cikinsa yai masifar murɗa mai yasan yunwa ce ke damunshi saboda ko ɗan ruwan tea da ya saba sha kafin ya fito yau bai sami damar sha ba. Backpack ɗinshi ya dauka ya rataya a ƙafadarshi, walking majestically ya nufi class har zuwa lokaci Nana na aikin kallonshi a nufi shi da ya iso gun da take sai ya wanke mata fuskarta da mari amma yana isowa wurinta idanuwansa suka sarƙe da nata take ya ji ya kasa aiwatar da nufinsa tun daga tsakiyar kanshi har izuwa ga tafin ƙafarshi ya ji wani irin yarrr! jikinsa tamkar an ɗauɗɗaure mai shi da igiya ya yi jimm kafin ya yi ƙarfin halin yin ƙwafa ya soma tattaka stairs ɗin da zai ka shi class ɗinsu kasancewar class ɗinsu a saman bene yake bai wuce haura two to three stairs ba ya tsince muryarta tana faɗin "Ka yi haƙuri Tareeq."

Sosai yaso ya hanawa kanshi juyowa ya kalleta sai dai zuciya da gangar jikinshi ba su bashi haɗin kai ba don sai da ya juya ɗin, gani haka yasa Nana tasaki mishi tattausan murmushi tare da sake furta "I'm so sorry! Ba tare da ta bari sautin ya fita ba yadda lips ɗinta ya motsa ne zai sanya ka fahimci abinda ta faɗa. Gani da yanayin da yake kallonta dashi yasa tai saurin kawar da kai gefe ɗaya alamun ba za ta jure kallon tsanar da yake mata ba. Gudu-gudu Tareeq ya shiga haura bene step by step ya shige class Nana ta bi shi da kallo tare da dafe saitin da zuciyarta take.

Kwata-kwata daren jiya bata samu runtsawa ba da suna bacci gaba ɗaya ta raya dare ne da tunanin abun da Tareeq yai mata,ta rasa wacce irin masifa ce take shirin kunno wa rayuwarta. Tasan waye Tareeq sani ba na wasa ba sai dai ta ba wani labarinshi amma sai gashi cikin ƙanƙani lokaci tunaninshi yana neman ya birkita mata ƙwaƙwalwa. Ta nufi aji kamar wacce bata da lakka a jiki, ta so ta hanawa kanta kallon seat ɗinshi amma abin yaci tura sai da ta kalle shi kansa a duƙe yana duba text book wanda bata gane ko na wane subject bane, kasancewar seat ɗinta yana gefen hagunshi hakan ya ƙara mata ƙaimi wurin ci-gaba da kallon kyakkyawar fuskarshi.

First period English ke gare su har malamin da ke ɗaukar su darasin ya shigo ya fita Nana ta kasa concentrating gaba ɗaya hankalinta ya tattara ne akan Tareeq shi ma kusan haka abin yake a wurinshi dalilin yawan kallonshi da take ya haifar mai da rashin natsuwa.

Lokacin fita breakfast ya yi kasa fita ya yi ba don baya da buƙatar fita ba sai don yadda yake ji rashin kuzari, ba yadda su Lil-prince ba su yi ba akan ya faɗa musu mike damunshi domin gaba ɗaya ya sauya musu tamkar ba slugger ɗinsu ba, kafewa ya yi lallai ba abin da ke damunshi, yayin da Roonie ya kasa tafiya ya bar shi sai kawai ya matsa masa da tambaya a fusace ya taso masa kamar zai dake shi, gani haka yasa ran Roonie ya ɓaci ya nufi ƙofar fita a dining room ya tadda su Lil-prince wanda tuni suka fice daga aji.

Roofy Sodangi ita ma kasa bin su tayi ta nemi kusa da shi ta zauna sosai ƙugunta ke gugar nashi, sakamakon yadda seat ɗin yai musu kaɗan, saboda na zaman mutum ɗaya ne.

"Basan ni ba ko ina da muhimmanci da ni za ka faɗa min damuwarka, duk da akan idanuna saura kaɗan ka kai wa Roonie duka don kawai ya nuna damuwarshi akanka."

Yadda tai magana ƙasa-ƙasa tamkar mai raɗa yasa ya kalleta a fakaice, ya kawar da kanshi gefen da window yake karaff idanuwanshi suka faɗa cikin na Nana wacce ke tsaye jikin window tana kallonsu, jin ya yi a wannan lokaci ba zai kyale ta ba dole ta faɗa mishi dalilin da yasa tsakanin jiya da yau take neman takurawa rayuwarshi, ya tashi a fusace ya nufi ƙofar fita da sauri Roofy Sodangi ta bi shi a baya tana kiran sunanshi a zato ta ya ji haushin tambayar da tai masa ne. Koda ya fito ya nemi Nana sama da ƙasa ya rasa sosai hakan ya ɗaure mai kai, sai da aka dawo class ya hango ta zaune akan seat ɗinta ya yi ƙwafa gami da cizan leɓɓen shi.

Kamar Nana tasan Tareeq yana haƙonta ana tashi ita ce first da fita class, kafin ya fito har an zo ɗaukar ta yai ta nemanta bai gannta ba sosai ya ji haushin hakan.

Karfe 4:30pm ya iso gida direct ɓangaren shi ya nufa ya yi wanka ya shirya cikin black colour three quarter crazy jeans wanda gaba ɗaya gwuiwayin wando a farfeshe suke yasa sky blue t-shirt mai gajeren hannu ya gyara tulin sumarsa da ya tara wacce aka aske gefe da gefen har izuwa ga ƙeyarsa tsakiyar kawai ke da gashi ya taje suman sai ya sauko gaban goshinsa ba ƙaramin kyau haircut ɗin yai mishi ba. Sai dai babu tarbiyya a tattare da askin mostly celebrities ko 'yan kwallon ƙafa ke yin shi sai kuma iri-iri su Tareeq da suka fi ƙarfin Iyayensu.

Tsadaddun turaruka Daddy da ya ɗebo ɗakinshi ba da sani Daddy ba ya dinga bi jikin kayanshi yana fesawa ta entrance ɗin main parlour ya bi Aayya ƙadai ya tadda ta kafe idanuwanta ga akwatin talabijin sai dai yana jiyo muryoyin su Ya Fadila a kitchen.

"Sannu da hutawa memory lost yau ke kaɗai ki ka ci gadon parlour nan?"

Tareeq ya yi magana gami da faɗawa kan kujerar da Aayya take zaune, sosai ya shige jikinta ture kafaɗarshi tayi daga jikinta "matsa min kada ka karya ni ɗan banza yaro mai ƙiriniyar tsiya kai komai ba ka yi sa cikin natsuwa kalli yadda ka faɗo min aka.

"Da gaske faɗo miki nayi?"

Tareeq ya tambaya yana kunshe dariya doke mishi hannu Aayya tai gami da faɗin "ka ji min ja'irin yaro wato tambaya ta ma kake yi.

Hannunshi ya kai kan kumatunta yana tattaɓawa cike da shaƙiyanci yake faɗin "Gaskiya Aayya kin rame sosai kalli yadda kumatunki suka zurma idanuwanki duk sun faɗa anya kuwa gidanan ana ba ki abinci?"

Kamar jira Aayya take yi ya dasa aya ta shiga zazzaga masifa dama abin da yake so kenan ya haɗa husuma.

"Ubanwa ya damu da ni a gidanan Tareeq balle har a damu da naci abinci ko ban ci ba, gaba ɗaya mutane gidanan ban cire kowa ba manyansu da yaransu ban da mugun hali ba abinda suka iya, jira kawai nake Imamu ya dawo ya maida ni Katsina gidan Abubakari kada yunwa tai min illa cutar sugar da hawan jini ba su kashe ni ba ina daɗi idan cutar yunwa ta zama ajalina."

Yadda ta ƙarasa magana tana ya motsa fuska yasa Tareeq ya sheƙe da dariya ya ƙara rungume ta yana faɗin "Aayya rigima uwar Imamu kakar Tareeq sarka faɗi ki rikice a rasa ganin bakinki.

Dariya mai sauti Aayya tayi tana faɗin "hoo ja'iri yau har da kirari ake min da dukkan alama yau ƴan mutunci na bisa kai, to tashi maza ga abinci can munafukai can sun taru sun girkawa ɗan banza yaro nan Jabeeru mai baƙin yawo kamar wanda yaci ƙafar kare, yoo..... ALLAH na tuba tsakani shi da Imamu na rasa tantance wanda yafi wani taɓarɓarewa su kam rayuwar su gaba ɗaya a tanɓele za ta ƙare."

Sosai Tareeq ya dinga kyalkyalar dariya kafin ya gintse dariya ya kafa bakinsa a damtse hannun Aayya yana faɗin "Duk ranar da tijirarki ta motsa ki ka sake danganta Daddyna da Ya Jabeer sai na cinye damtse nan naki."

Da kyar Aayya ta yakice bakinshi daga damtseta ta kai mai rankwashi tana faɗin "Ka ji min ɗan banza yaro garin gantalinka a gari ka ɗebo maita nikam damtsena ɗaci gare shi sai dai ka ci uwarka Amina ko na Yakumbon ka Maimunatu."

Tareeq ya murmusa ya ce "ai duk kin fi su kitse sosai namanki Aayya zai yi daɗi ba sai an sha wahala wurin gasawa ba."

Throw pillow Aayya ta dauka tana dukanshi dashi "Tashi ka bani wuri kar ka sake dawowa inda nake ja'iri yaro da baya ƙaunar zaman lafiya."

Miƙewa ya yi yana ci-gaba da dariya kitchen ya nufa yana faɗin "huta da tadda jijiyoyin wuya koda ace ni mayye ne ba abinda zan yi da ke yunwa duk ta bi ta naɗe miki hanji mi zan ci da ke."

"Karya ka ke yi ja'iri duk cikin uwayenka ba ɗan banzan da yafi ni ƙoshi, za ka gasganta zancena duk sanda ka ƙare musu kallo kowane su da wuya zololo kamar talo-talo ya shiga gaba su na bin shi."

Da dariya ɗauke a fuskarshi ya nufi dining room ya ga ba abinci akan dining table sai kawai shiga kitchen ya tarar da Ya Fadila tana kwaɓa fulawa za ta yi scotch egg, Baby Kuma tana gyara fruits za ta haɗa special fruits combo Zainab kuma tana tsame naman kaza daga mai ba wacce ya tankawa ya raba su ya wuce Idan ya hango Manyan Warmers tun kafin ya kai hannunshi da nufi buɗewa, Ya Fadila ta daka mishi tsawa gami da faɗin "kar ka sake ka taɓa warmer ko ɗaya a wuri domin abinci da ke ciki ba wanda aka girka da sunanka.

Aayya ta ce a gayamuku kada ku shagala da karanta Free page ku manta da na kuɗi ne😂

Ta ce ga masu bukatar ci-gaba da karanta wannan littafi za su biya 700 kacal ta wannan asusun banki 7032566272 Hauwa Shehu opay. Aayya tayi arha ta hana bashi dan haka ku hanzarta ku

nunawa shalelenku Tareeq ƙauna, duk da Tareeq yace a baku part one kyauta amma part two kun dai gane, kusan Tareeq ɗan albarka ne yana yin ku.

Jeeddah Aliyu

07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

010.

Cike da mamaki ya ɗauke hannunshi daga murfi warmer ɗin ya kalli Ya Fadila wacce ko kallo bai isheta ba aikin gabanta kawai take yi. Ya ciza leɓɓen shi kafin ya yi ƙwafa ya juya zai fice sai kawai ya ga koren apples cikin wani matsakaicin bowl za su ka shidda zuwa bakwai ya biya mai a rai yasaka hannu ya ɗau guda.

"Kai waye ya ba ka izinin ɗaukar apple ɗinan?"

Ya Baby tai magana tana galla masa harara. Cakk! Ya tsaya tare da juyowa da mugun sauri zuwa yanzu ranshi ya kai maƙura da ɓaci.

Tsawa Baby ta daka mishi gami da faɗin

"Wai kai kurma ne ko tsabar reni wayau ne yasa ka kafe ni da shegun idanuwanka masu kama da na agolan nufawa."

Zainab ta tofa albarkacin bakinta ta hanyar cewa "Ba duk kurma bane tsabar iskanci ne da rena mu da ya yi shi kowa gani yake bai isa ba ɗan Iska kawai fitsararre da wasu dakwa-dakwa idanunshi kamar idon mayu."

Banda ƙwafa ba abinda Tareeq yake domin ji yake yi tamkar ya babbakawa kitchen ɗin wuta kowa ya ƙone ƙurmuss, a yadda yake jin zuciyarshi na tafarfasa bai ƙi a mutu har liman ba kowa yai wa kanshi sallah.

"Ki bar shi kawai Ya Zainab ya ri ga da ya gama rena mu a gidanan, kuma wallahi duk Daddy ne ya ja mana ya wani fiffita shi akanmu sai kace ba mu ya fara gani kafin shi ba. Ana magana yana kallan mutane a wulaƙance."

Cewar Ya Fadila tana taɓe baki.

"Mtsss! Ai kuwa ga illar fiffita shi nan ya fara gani irin su Tareeq ne ake wa lakabi da haihuwar ku gara barinku. Wannan taƙadari da kike gani in ya ƙara girma ba ƙaramin criminal za a yi ba."

Zainab tai magana cikin baƙin ciki da takaici.

"Dallah malam! ajiye mana apple ɗinmu ka ɓace mana da gani ɗan Iska da bai san darajar na gaba dashi ba."

Baby ta faɗa gami da sake daka masa tsawa.

Baki buɗe Tareeq yake kallansu kafin ya kaɗa kai ya nufi ƙofar fita daga kitchen ɗin, sai kuma ya juyo a fusace ya ce "Ga apple ɗinku nan ku ne matsiyata ni na fi ƙarfi a ci min zarafi akan kwarar apple guda ɗaya, ƴan ba***uba da suka yi kwatai kun tabbata gidanan kuna mana girke."

Ya ƙarashe magana gami da jefawa Ya Baby apple ɗin da ƙarfi, cikin sa'a apple bai sauka a ko ina ba sai ga ƙirjinta ya daki nononta na dama gashi dama bata saka bra ba soft short cotton gown ce a jikinta Irin mai bi ta lafe a jiki nan yadda apple ɗin ya buge nononta sai da taga wasu mitsi-mitsi jajayen taurari sun lulluɓe ganinta sai shawagi suke mata kamar dai yadda butterfly ke flying a cikin haske. Apple ɗin ya yi tsalle ya daki kitchen island ya tsage gida biyu kana ya faɗo ƙasan tiles kusan a tare ita da apple ɗin suka zube ƙasa, duka hannuwanta biyu tasa ta dafe kirjinta har da wanda jifan bai sama ba. Saboda tsananin azaba ta buɗe murya da ƙarfin gaske ta ce "wayyo ALLAH na ya fasa min nono wayyo na shiga uku nonona!

Yadda ta barka ihun da amo mai sauti sai da Tareeq ya toshe kunnuwanshi, a gigice Zainab da Fadila suka yi kan Baby da ke zube ƙasa wanwar! Koƙarin ɗago ta suke, yayin da Baby ta ke gunji kuka kamar ranta zai fita ita kaɗai ce za ta iya misalta Irin azababben ciwon da radadin take ji a nononta.

Tareeq ya kalle su yana sakin murmushin mugunta, cikin fitsara ya ce "Aikin banza kawai shi wannan ɗan bugun da apple yai miki a nono kike wa kuka to ke ina da an luguiguita miki su an tsotsa watakila suma za ki yi...mtsss.... I hate lazy woman!"

Ya ƙarasa magana yana jan tsaki ya juya gami da zuba hannuwanshi a cikin pocket ɗin wandonshi yana wata tafiya ta taƙama, hatta da Baby da ke gunji kuka sai da furucin Tareeq ya girgiza mata ƙwaƙwalwa bare su Fadila da sai da suka zabura kowacce su ta waro idanuwa suka bi shi da kallo baki buɗe, kasa haƙuri Fadila tai tasakin shoulder Baby ta rugu da mugun gudu ta nufi parlourn Ummi gami da kwalla mata kira na fitar hankali tana faɗin "Ummi....ummi!....zo ki ga abinda Tareeq yai wa Baby."

Tun kafin ta shiga parlourn ta fara kwaro zance, Ummi da ke kishigiɗe akan sofa ta tashi tsaye a tsoroce don kamar daga sama ta ji saukar muryar Fadila a dodon ƙunneta.

"Hasbunallahu wal-imal wakil! Fadila me kuma ya faru me Tareeq ya aikatawa Baby?"

"ummh! apple ya dauƙa ba tare da ya tambaya ba Baby ta ce ya ajiye shine ya rasa inda zai jefe ta dashi sai ga nononta, ga ta can kwance a kitchen cikin mayauwaci hali da wuya idan ma bai fasa mata nono ba."

Ba wannan ba Ummi wallahi Tareeq ya zama tantirin ɗan iska mata yake bi kin ji zance batsa da ke fita daga bakinshi abin ba ko daɗin ji."

Wani Irin jiri ne ya kwashi Ummi dole ta dafa hannu kujera, da tuni ta zube ƙasa numfashi Ummi ke fizga da ƙarfi da sauri Fadila ta riƙo hannunta "Innalillahi wa'inna illahim raji'un! Ummu ba dai Asthma ki ne ya tashi ba?"

Fadila tai magana cikin rawar murya.

"Fadila wacce irin masifa ce Tareeq yake so ɗauko min dukka guda nawa yake da zai fara bin mata zina fa Fadila?'

"Ni ma Ummi na tsorata matuƙa da na ji zance ya fita daga bakinshi, sai kuma na ƙara gasganta zance Maman Nana da ta ce ya taɓawa Nana nono wallahi Ummi azahirin gaskiya koda Tareeq bai fara aikata zina ba amma tabbas yana taɓa jikin mata nikam Ummi Tareeq ya fara bani tsoro."

"Innalillahi wa'inna illahim raji'un! wane zunubi na aikata Fadila da ALLAH zai jarabce ni da haifar ɗa irin Tareeq?"

Ummi tai magana gami da rushewa da matsanancin kuka mai taɓa zuciya.

"Haba! Ummi daina fadar haka Dan ALLAH ki tuna ke musulma ce ba dole sai kin saɓawa ubangiji zai jarabce ki ba, Ummi ki cire lamarin Tareeq daga ranki ko don gudun abin da zai taɓa lafiyar ki. Ki ɗauki abin da yake yi a matsayin jarabawar babban takaicina bai wuce goyon baya da yake samu daga wurin Daddy ya bi ya ɓata shi ya sangarta shi duk muni laifi da ya yi baki isa ki tsawata masa ba yanzu sai Daddy ya rufe ki da ruwan masifa saboda haka duk bala'i da masifar da Tareeq ya ɗauko kanshi da Daddy zai ƙare."

Fadila ta ƙarasa magana cike da jin haushin Daddynsu don shine ummul'haba'isi lalata Tareeq.

Share hawaye ummi tai da gefen rigar ta kafin ta ce "wallahi Fadila Imam Wali ya cuce ni ya zama silar haifar min da ƙunci ki duba ki gani a shekarun Tareeq har ya fara tsalle-tsalle ina da ya ƙara girma ALLAH ne kaɗai yasan kalolin tsiyar da zai tsula."

"Ni ma shine fargaba na ummi gashi kullum Daddy ba shi da zance da ya wuce ya tura shi karatu abroad. Ba baki nai masa ba amma da matuƙar wahala Tareeq ya dawo Nigeria ba tare

da guzirin tulin ƴaƴan shegu ba."

Waro idanuwa Ummi tayi tare dafe saitin da zuciyarta take sakamakon bugawar da tai mata da ƙarfi, jawo hannunta Fadila ta yi tare da faɗin "Taho mu je kitchen ki ganewa idanuwanki mugun ta'adin da ya yi wa Baby."

Kasa magana Ummi tayi batasan inda take taka ƙafafuwanta ba ita dai biye kawai take da Fadila a main parlour suka tadda Baby kwance aka rug Zainab ta taimaka mata ta kawo ta parlour har zuwa lokaci Baby bata cire hannuwanta daga kirjinta ba, kuma bata fasa gunjin kuka ba gaba ɗaya fuskarta ta caɓe da hawaye da majina.

"Tashi zaune Baby tashi kin ji naga wuri."

Ummi ta faɗa sa'ili da ta isa wajen Baby.

"Ba zan iya tashi ba Ummi can cikin nake ji azababben ciwo, Dan ALLAH ummi ki kira doctor ya duba ni banaso na rasa nonona, Ummi Tareeq ya kashe ni wallahi azaba nake ji."

Baby tai magana cikin raunanniyar murya.

Rigar jikinta Ummi ta janye sai da gabanta ya faɗi rass! A dalilin yadda taga nono Baby ya yi kumbure ya yi jajir

#Tareeq

#Fadila

#Baby

#Zainab

#Ummi

#team TareeqImam.

Aayya ta ce a gayamuku kada ku shagala da karanta Free page ku manta da na kuɗi ne😂

Ta ce ga masu buƙatar ci-gaba da karanta wannan littafi za su biya 700 kacal ta wannan asusun banki 7032566272 Hauwa Shehu opay. Aayya tayi arha ta hana bashi dan haka ku hanzarta ku nunawa shalelenku Tareeq ƙauna, duk da Tareeq yace a baku part one kyauta amma part two kun dai gane, kusan Tareeq ɗan albarka ne yana yin ku.

Jeeddah Aliyu

07032566172.

Jeeddah Aliyu

07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

011.

"Innalillahi wa'inna illahim raji'um! Gari ya Tareeq yai miki wannan aika-aikar?"

"Ummi na gayamiki fa saboda ya ɗauki apple ta mishi magana kinsan shi da baƙar zuciya da zafin rai shi ne ya jefe ta dashi. Kuma wallahi Ummi da gangan ya jefe mata a ƙirji."

In ji Fadila dake tsaye kusa da Ummi.

Sosai ran Ummi ya ɓaci dan har wani kalar ɗaci-ɗaci take ji a maƙogwaronta. Yayin da Baby sai gunji kuka take ita kaɗai ce za ta iya misalta tsanani raɗaɗi gami da zogi da nononta yake mata. Babban tashin hankalinta kada ta wannan sanadi Tareeq ya jawo mata matsala musamman da yanzu da breast cancer ta yi yawa ga mata. Da kyar Ummi ta danne tuƙuƙi da take ji a zuciyarta ta dubi Fadila ta ce "Fadila dauko key ɗin mota mu kaita asibiti.

Da sauri Fadila ta je ta dauko key da hijabin ummi.

Kafin su isa asibiti nonon Baby sai daɗa kumburi yake Dr Hadiza suka gani ta duba ta tare da rubuta mata magunguna ta kwatar mata da hankali "Daina kuka Baby In-shaa-Allah ba abinda zai same ki buguwa ce da zaran kina shan magani da zan rubuta miki ciki lokaci nan da kwana biyu kumburin zai sace.

Baby ta share hawaye da bayan hannunta tare miƙewa suka fice ita da Fadila. Yayin da Ummi ta tsaya yiwa Dr Hadiza godiya. Suna dawowa gida kai tsaye Ummi ta nufi ɗakin Tareeq da zimmar yi mai dukan akawo wuƙa. Sai dai tana tura ƙofar ɗakinshi ta ji ta a rufe a fusace ta dawo main parlor sai faman huci take yi, wata irin tsanar Tareeq ce ke huda mata zuciya ji take idan ta rutsa shi ko kashe shi za ta iya. Tsanani faɗa da zagi da take masa ya fito da Aayya daga ɗakinta.

"A duniya nan ta maliki yaumindini ban taɓa gani hatsabibiya uwa irinki ba Amina. Yanzu tsabar lalacewar taki har ta kai ki dinga zagi da aibanta ɗa da ki ka yi kayan cikinsa na tsawon watanni goma. Da ki ka zo haifarsa sai da likitoci suka yanka ki sannan suka ciro miki shi. Shine ki ke yiwa irin wannan ƙazamin zagi?"

Ummi ta waiga bayanta a mugun hasale tana kallon Aayya cikin wani irin fushi ta ce "Aayya na haɗa ki da girman Allah da manzonsa ki fita daga wannan magana saboda nayi rantsuwa yau ko ni ko Tareeq a gidanan."

"Ke arrr! Kin ji kunya Amina ɗa da ki ka haifa da cikinki, ki ke wannan tada jijjiyoyin wuya akanshi, wannan kayan takaici har ina? Kin mayar da ɗanki maƙiyin ki duk don ki kuntata wa ubanshi to ki sani Amina kanki ki ka yiwa domin ke uwa ce bakinki tamkar lalle yake."

"Shikenan Aayya ai ni kodayaushe mai laifi ce a wurin ki bana taɓa fari indai a gunki ne. To wallahi idan har Alhaji bai ɗau matakin tsawata wa Tareeq ya yadaina ɗora hannunshi akan yarana ba, sai na dau mummuna mataki kanshi. Akan me Tareeq zai bi ya fitine yara sai kace ba gidan ubansu ba. Yau ya daki wannan gobe ya bugi wancan jibi ya karya wannan akan idonki ya fasa wa Tahreem goshi ƙaryata wa ki ka yi, shi ma ubanshi da na gayawa masa wanne mataki ki ka ga ya dauka? Daga karshe ma sai ɗora min laifi ya yi. Don haka na gaji tun da har iskancinsa ya fara kai wa ya jefi nonuwa yarana."

"Ba tun yau ba nasan da cewa Amina bakya ƙaunar Imamu tun da har ki ka iya tsallake shi ki ka zaɓe ɗan makiyiyata dan ina faɗa kina faɗa ai ba komai bane idan aka yi duba da butulci da ki ka yi min a shekaru baya."

"Innalillahi wa'inna illahim raji'um! Haba Aayya wai miyasa duk sanda za ki buɗe baki sai ki yi min wannan gori shin miye laifina don na bi zaɓin zuciyata? Ni a wurina marigayi Abdallah da Imam duk ɗaya ne basu da bambanci domin duk abinda ya yi Imam shi ya yi Abdallah...

"Karya ki ke Amina ɗa kishiyata ba zai taɓa zama ɗaya da Imamu ba."

Cike da baƙin ciki mai haɗe da zallar takaici ummi take furzar da numfashi ba tare da ta sake tankawa Aayya ba ta bi ta gefenta jiri na ɗibar ta tai sauri shigewa bedroom ɗinta zuciyarta na mata raɗaɗi da zogi har sai zuwa yaushe Aayya za ta daina goranta mata wannan al'amari? Abinda ya faru tsayi shekaru 20 amma har kawo yau ɗinan ta kasa manta wa dashi.

Ummi ta nemi gefen gado ta zauna tare da rafka tagumi ita kaɗai tasan irin haƙuri da danne zuciyarta da take yi a yayin zamanta da Imam Wali bata taɓa ji ƙaunarshi ko misƙala-zarrati amma a haka take zaune dashi duk da haka bata wuce gori a wurin Aayya ba.

Ummi tana shigewa bedroom Fadila ta maka wa Aayya danƙarerriyar harara tana faɗin "Ke dai Aayya lamarin ki sai addu'a babu ranar da za ta zo ta wuce ba tare da kin baƙantawa Ummi rai ba. Kullum ciki nuƙurƙusar baƙin cikinku take. Ke ki kunsa mata Daddy ya yi mata ga kuma na wannan ɗan iska gantalalle wofi. To ki sani idan wani abu ya sami mahaifiyarmu ba za mu taɓa yafe muku ba."

"Ban yi mamaki ba Fadila dan ki dubi tsabar idanuwa na kin gaya min magana amma ki sani uwarki darajar ƴar uwata da muka fito ciki ɗaya take ci da tuni nasaka Imamu ya tsika igiyar aurensa dake kanta koda kuwa igiyar takai dubu, ina dalili wannan zazzafar ƙiyayya da take nuna masa gashi nan har ta shafi gudan jininsa."

Baby dake fama da zogi nononta ta ɗago daga kwance da take akan kujera ciki dusasshiyar murya ta ce "Dan Allah Ya Fadila ki yi shiru ki daina tanka mata ita dama kullum jireye take da Ummi kuskure kaɗan ta hau mata gori."

Tsaki Fadila ta ja ta wuce a fusace ta shiga bedroom ɗin Ummi Aayya ta dawo kan Baby ta dinga ƙare mata tanadi da Baby tagaji da surutun ta, ta bar mata falon duk da haka Aayya bata fasa zagin ummi ba.

Sosai tausayi Ummi ya lulluɓe Fadila musamman da ta hango ta tallaɓe da kumatunta ta takure kanta wuri guda, tun bata da wayau Aayya take wa Ummi wannan gori har kawo yanzu da ta girma ta mallaki hankali kanta bata canza zani ba.

A hankali Fadila ta tako ta zauna kusa da Ummi sai da ta cire mata tagumin da tayi kafin cikin kwatar da murya ta shiga kwatar mata da hankali "Ummi ki yi haƙuri ki daina damuwa da abinda Aayya take miki, in da sabo ya ci ace kin saba Ummi."

Sai da Ummi ta sake furzar da numfashi kafin ciki raunatacciya murya ta ce "Fadila na gaji da haƙuri domin na fahimci yana cutar dani idan na ci-gaba da yin sa watarana za ku riske gawa ta. Domin ni kaɗai nasan irin ƙunci da baƙin ciki da nake ciki wallahi Fadila na gaji da zama da Daddynku a halin yanzu na fi buƙata rabu wa dashi fiye da komai."

"Innalillahi wa'inna illahim raji'um! Hasbunallahu wal-imaal wakil! Ummi Dan ALLAH ki daina faɗar haka duk mai hankali ba zai koma kan Aayya ba rigima tsofa ke damunta abubuwan da take yi ke da gani kinsan akwai ruɗewar tsofa. Idan akan Tareeq ne Ummi addu'a za mu ci-gaba da masa In-sha-ALLAHU watarana za ki ga ya daina."

"Yaushe hakan za ta faru Fadila?

"Ummi Allah aka ce duk abinda aka ce Allah babu saura wata magana Ubangiji bashi da dole."

Girgiza kai Ummi tayi zuciyarta cike  da damuwa.

"Ki yi haƙuri Ummi da tambayar da zan miki har ga Allah ban so yi miki ita a irin wannan yanayi da ki ke ciki ba. Ummi miye musanbabbin faruwa rashin jituwa tsakaninki da Daddynmu da mahaifiyarsa (Aayya) duk da kasancewar Aayya na yayar mahaifiyarki suka fito ciki ɗaya uwa ɗaya uba ɗaya kuma wacce ta raini ki tun kina da shekaru shidda a duniya har ki kai muzali aure? Ummi dan ALLAH ki ɗaure ki bani amsar waɗannan tambayoyi nawa.

Sai da Ummi ta sauke naunnayar numfashi kafin ta tattara natsuwarta wuri ɗaya.

(Flash back)

Waiwaye!"

Alhaji Mamman Wali kusada haifaffen garin Katsina ne a ƙaramar hukumar kusada kuma shahararren ɗan kasuwa da yai shura a garin katsina har da wasu jihohin Nigeria, Duk wanda yasan kusada yasan gari ne na malaman addini shiyasa ma ake wa garin lakabi da

kusada garin malamai. Jama'ar garin su haɗa ƙabila Hausa/Fulani, babbar sana'ar su noma da kiwo. Alhaji Wali kamar yadda mutane suka fi kira shi dashi wanda hakan yasa ainihin sunansa na Mamman ya ɓata. Ya mallaki matan aure guda biyu uwargidansa Hadiza wacce ake kira da Aayya sai kuma Karimatu. Aayya tana da ƴaƴa shidda biyar maza macce ɗaya, Bello, Ibrahim, Abubakar, Imam da Hashim sai auta maimunatu.

Karimatu ita ce mai ƴaƴa takwas. Abdallah shi ne babba kuma shine sa'an Abubakar duk da Abdallah ya ba wa Abubakar watanni bakwai da haihuwa, sai Farouk, Sakina, Fatima, Kabir, Hafsah, Salisu shine ƙaramin su. Tun daga lokacin da Alhaji Wali ya auro karimatu zaman lafiya ya ƙare a gidanshi sakamakon Allah ya yi Aayya wata irin macce ce mai tsananin zafin kishi gata mafaɗaciyar gaske bata da haƙuri ko kaɗan. Abu ɗan ƙanƙani sai ta mayar dashi babba tun karimatu tana haƙuri da kauda kai akan iri-irin abubuwa marasa daɗi da take mata har ta dawo ta fara tanka mata. Hakan ya haifar da wata kalar ƙiyayya a tsakaninsu wacce har ta kai da shafar ƴaƴansu. Ƴan ubanci suke nuna wa junan su kamar me. Duk yadda Alhaji Wali yaso su haɗe kansu su zauna lafiya abin yaci tura. Yana ji yana gani ƴaƴansa suka dawo maƙiyan juna. Aayya tana da ƙanwa mai suna Fatima dake aure a garin Baurawa Fatima sun yi aure da mijinta mai suna Yusufu ta haifi yara biyu dashi Amina(Ummi) sai Usman a wurin haihuwar ta uku ne ALLAH ya karbi ranta a lokaci Amina(ummi) tana da shekaru shidda a duniya Usman yana da uku. Kasancewar su masu ƙananu shekaru shiyasa Aayya ta nemi Yusufu ya bata su ta riƙe bai yi gardama ba daga nan reƙo su ya dawo hannun Aayya. Da suka isa shiga makarantar boko Alhaji Wali da kanshi ya saka su duk abinda yai wa ƴaƴan cikinsa shi yake musu bai taɓa bambanta su ba. Tun daga sanda Amina ta zama cikkakiyar budurwa Allah ya ɗorawa Imam wani kalar azababben sonta yayin da ita kuma ko kaɗan bata sonsa a dalili Imam irin mutane nan masu izza da girman kai gashi da sauri fushi da baƙar zuciya Kwata-kwata halayensa da dabi'unsa ba su yi daidai da ra'ayin ta ba. Kwatsam! suka ƙula alaƙar soyayya ita da Abdallah ba tare da la'akari da abinda hakan zai haifar ba. Dukkan su biyu idanuwansu sun rufe akan junan su. Yayin da Aayya ke ta faman doki jiran Amina ta kammala karatun sakandare ayi shagali bikinsu da Imam. Sai ga Amina ta bullo da wani babban al'amari wanda sai da aka yi ɗan ƙaramin yaƙi. Aayya tana ji tana gani Alhaji wali da Yusufu suka nuna mata fin ƙarfi suka aurar da Amina ga Abdallah. Sauƙi Amina ɗaya Karimatu tana ƙaunar ta, rashin jituwa da ke tsakaninta da Aayya bai shafe ta ba a cewar karimatu duk wanda ya ce yana ƙaunar jininka ya gama maka komai, ta karbi Amina domin ta kara tulawa Aayya haushi. Ana kammala biki Abdallah ya ɗauki amaryarsa suka wuce cikin garin Katsina anan yake aiki koyarwa a makarantar sakandare.

A lokaci Imam sai da ya kwanta jinya bayan ya warke ya tattara kayanshi ya koma Kano da zama dama a Buk yake karatu. Cikin hukunci Ubangiji yana kammala degree ɗinsa a fannin

political science Allah ya haɗa shi da Alhaji Tareeq mu'az wanda ya kasance jam'i custom ne, da taimakon shi Imam Wali ya sami aiki da hukumar fasa gwari ta ƙasa (Nigerian custom service) cikin ƙanƙani lokaci Allah ya daukaka Imam ƙofufin samu suka buɗe masa. Ya zo ciki gari Katsina ya siye ƙaton fili ya gina wa Alhaji Wali katafaren gida a lokaci girma ya fara kama shi, gashi ya haɗu da kariyar arziki kasuwanci da yake karye komai ya tsaya. Wannan shi ne dalili da yasa Alhaji Wali ya baro garin kusada ya dawo ciki garin Katsina tare da iyalinsa. Wata irin ƙiyayya Aayya take nuna wa Amina ciki ma Alhaji Wali yana tsawata mata. A haka Amina ta zo ta sami ciki ta haifi lafiyayyen ɗanta ya ci suna Jabeer a haka rayuwar su ta ci-gaba da tafiya, arziki Imam sai daɗa bunƙasa yake sai dai wani abin mamaki ko zance aure baya so ayi masa, sai da Alhaji Wali ya tashi tsaye akanshi kafin ya gabatar da Jamila a matsayin wacce zai aura anan Kano ya haɗu da Jamila ɗiyar maigidan sa ce Alhaji Tareeq da fari Jamila ce ta fara nuna masa ƙauna gani yadda Malam ya kunno masa wuta babu shiri ya karɓi soyayyarta. Babu bata lokaci aka sha bikinsu. Rayuwa ta miƙa shekaru kuma sai daɗa tafiya suke kwatsam! suka waye gari da rasuwar Alhaji wali daga gajeriyar jinya Allah ya karɓi abinsa iyalansa sun yi kukan rashinsa daga ƙarshe dole suka dangana domin Ubangiji da ya basu shi yafi su ƙaunarsa.

Sannu a hankali Abdallah yake ji canji a jikinsa yau lafiya gobe ciwo sai uban kumburi da jikinsa ke yi kullum ciki shan maganganu gargajiya yake a cewar sa sanyi ƙashi ne ke damun sa, Abdallah irin mutane nan ne da basu cika son zuwa asibiti ba. Har sai ciwo yaci ya cinye su watarana ya faɗi a makarantar da yake koyarwa aka kwashe shi sai asibiti binciken farko da likitoci suka yi masa suka gano yana ɗauke da ciwon ƙoda rashin kulawa yasa har ƙodarsa guda ta fara lalace wa yayin da ɗayar ke barazanar kamuwa da cutar. Saboda haka babu ɓata lokaci aka soma yi masa dialysis ranar Amina tasha kuka kamar ba gobe ga baki ɗaya ta bi ta ɗaga hankalinta gani take yi kamar shikenan ta rasa mijinta. Kusan lamari idan aka ce na asibiti ne dole ana buƙata kuɗi gashi kuma Abdallah ƙaramin ƙarfi ne dashi, duk ciki ƴaƴan Alhaji Wali duk Imam yafi su rufin asiri, wasa-wasa ciwon Abdallah sai gaba-gaba yake yi babu wani sauki daga karshe aka tura su abuja za ai masa aiki a national hospital Abuja.

#Abdallah

#Amina

#Imam

#JeeddahAliyu.

[7/6, 7:24 AM] Jiddah Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

012.

National hospital Abuja.

{Dialysis unit}

Tsaye Amina take akan Abdallah bambancin shi da matacce ƙalilan ne hatta da numfashinsa sai ta jikin respiratory monitor take gani bugawarshi,ga jijiyoyin jikinsa an manna masa wayoyi dake haɗe da Hemodialysis machine{machine ɗin wankin koda} dake ta zukar jinin marar lafiyar ta hanyar catheter yayin da jini ke shiga cikin na'urar ta dialyasis, yau kwanan su huɗu kenan da aka yi referring nasu a wannan asibitin na abuja kuma shi ne karo na farko da aka wanke masa kodarsa tasa anan wanda dama tun kafin su zo abuja ake masa yayin da suke jiran sakamakon gwaje-gwaje da likitoci suka sake masa. Wasu irin hawaye ne masu dumin gaske suka sake zubowa daga idanunta a karo na ba adadi. Tunawa da tayi likita ya bukaci ganinsu ita da ƙanin mijinta yasa ta fitowa daga ɗakin ba dan ranta yaso ba, domin gani take yi ko yaya ta gusa daga kusa dashi zata dawo ne ta tarar da ya rasu a duk sanda irin wannan tunani yazo mata sai taji wani irin tsoro ya lullube ta. Kai tsaye room 12 ta nufa ɗakin da aka kwatar da Abdallah kafin akai shi dialysis unit, cikin sanyi jiki haɗe da jaruntar da ta aro ta yafawa kanta, ta tura kofar ɗakin duk da haka fuskarta ta gaza boye halin damuwar da take ciki. Musamman idanuwanta da suka kode tare da yin luhu-luhu alamar dake nuna tasha kuka. Da sallama ta karasa shiga ɗakin Faruk dake zaune a ɗakin ya amsa mata tare da faɗin "Amina ya jikin nasa?"

Sai da taja dogon numfashi kafin cikin sarkewar harshe ta amsa masa a takaice "Da sauki likita yace yana san ganin mu a office ɗinsa sakamakon gwaji da sukai masa ya fito." Jiki macce ya miƙe suka sake fita, har suka isa office ɗin babban likita ba wanda ya sake iya magana, saida suka nemi izinin shiga aka musu iso, kana suka shiga likitan ya nuna musu kujerin dake gaban desk ɗinsa tare da furta "Please have a seat!"

Zama suka yi tare da zubawa likitan idanu likitan ya karkato da allon computer ɗinshi ta yadda zai nuna musu sakamakon CT scan ɗin da aka yi wa Abdallah (computed tomography) tare da cewa "Wannan shine CT scan da akayi masa ya kuma nuna kodarsa mai ɗauke da cuta ta lalace duka dole sai anyi masa unilateral Nephrectomy ma'ana za a cire kodar da ta kamu da cuta domin tana barazana da ɗayan mai lafiya."

"Innalillahi wa'inna illaihim raji'um!" Kusan atare suka furta tuni kukan da take ta ƙokarin ɓoyewa ya kubce mata "ki yi haƙuri Amina ki daina wannan kukan domin bashi da wani amfani kawai ki cigaba addu'a Allah ya ba Abdallah ikon cinye wannan jarabawa."

Faruk ya faɗa tare da sake maida hankalinshi kan likita yana faɗin "Yanzu doctor mene ne solution?"

"Solution ɗaya ne ayi gaggawar cire koda ɗin tun kafin ɗayar ta kamu, sai ku je ku biya kuɗin aikin gobe ko jibi sai ai masa."

Su miƙe kowanne su jikinsa a sanyayye har sun kai kofar fita Faruk ya dawo ya tambaye likita nawa ne kuɗin aikin makudan kudade da likita ya ambata masa yasa jiri ya ɗebe shi, har sai da ya dafa kujera idan Allah ya taimake shi yana kusa da kujerar da ya tashi,Amina dake kusa da kofa ta fashe da kuka mai matuƙar sautin gaske domin ta tabbata ko dukka abin da ƴan uwan mijinta su mallaka suka kaɗar basu isa  su biya wadannan kuɗaɗen ba, kai ko quarter ɗinsu ba zasu iya haɗawa ba. Cikin mayuwacin hali suka koma ɗakin da suke, yayin da Amina ke cigaba da shasshekar kukanta, dole Faruk ya hadiye tasa damuwa ya dawo yana rarrashinta da kalaman kwatar da hankali dakyar ya samu ta tsagaita da kukan nata. Amina ta dube faruk cikin dusashiyar muryata ta ce "Yanzu fissibillahi Faruk ina zamu samu waɗannan uban kuɗi da likita ya ambata?"

"Ba komai Amina Allah zai kawo mafita kawai ki cigaba da addu'a Allah yana sane da halin da muke ciki."

"Faruk kullum cikin addu'a nake babu ranar da zata fito ta koma ga Ubangiji ba tare da nayi wa Abdallah addu'a ba, amma a yau na fitar da rai da samuwa lafiyarsa kawai dai zan cigaba da masa addu'a samun saukin tafiya...

Ta kasa karasa maganar saboda kukan da yaci ƙarfin ta sai kawai ta kife kanta cikin cibiyoyin ta, tana cigaba da kuka dan a yanzu shi kadai ne abun da ya rage mata. Shi kanshi Faruk yasan abin da Amina ta faɗa gaskiya ne, su dukka babu wanda yake da wadannan kuɗaɗe. Hakazalika babu wanda keda kaddara da za a kadar dan ko a yanzu kafin su zo Abuja sai da aka yi karo-karo mai taro mai sisi, hatta da gonakin su na gado da suka rage musu sai da suka siyar, a cikin kwanakin huɗu da suka yi a wannan asibiti sun kashe kuɗin yakai kimanin dubu ɗari huɗu, wa suke dashi da zai biya musu miliyan tamanin dole su cire tsammanin daga kan Abdallah, kawai su cigaba da yimai addu'ar cikawa da imani. Haka suka ci-gaba da zama jigun-jigun bayan 4 hours aka dawo dashi daga dialysis unit, bayan Abdallah ya farfaɗo suka tayar dashi zaune suka jingina mai pillow shine ya buqaci hakan saboda duk gaunin ciwo da yake ciki  ba zai hana shi sallah ba, Amina ta taimaka mai ya yi alwala daga nan zaune ya yi sallah sai da ya rama dukka sallolin da suka wuce shi, kana Amina ta haɗa masa tea ya sha kaɗan. Ya ɗauki lokaci a zaune kafin ya buqaci su kwatar dashi, gani yayi bacci yasa su cigaba da tattauna idan za a sami waɗannan makudan kuɗi dan har sun kira waya can gida Katsina sun faɗa masu halin da ake ciki, suma acan hankalin su ne kawai ya tashi tare da cire rai akan Abdallah dan basu da mafitar wannan kuɗin.

Washegari

Amina ta kira ƙaninta Usman dake bautar ƙasa a kaduna ta sanar dashi halin da Abdallah yake

ciki suna gama waya ya, dau hanyar Abuja, zuwan Usman yasa taji sauki damuwar da take ciki, kamar daga sama Usman ya kawo wata shawara wadda sai da zuciyar Amina ta buga da ƙarfin gaske "Yaya Amina nace me zai hana anemi taimakon yaya Imam shi kaɗai ne a dangi wanda yake da wadannan kuɗaɗe da ake bukata, ki yi haƙuri ki danne duk wani abu da kike ji akansa domin samuwar lafiyar mijinki."

Tun sanda Usman ya fara magana har yakai aya Amina tana kallon sa zuciyarta na bugawa, kasa magana tayi sai famar kallon sa kawai take, Faruk ne ya sauke numfashi ya muskuta tare da gyara zamanshi, yana faɗin "Amina maganar Usman fa abar dubawa ce duk da bashi kaɗai ya fara kawo wannan shawarar ba. Dan ko Kabir da Sakina da nai waya dasu abun da suka ce kenan na ɓoye miki ne saboda sani da nai miki da matuƙar wahala ki amince, amma zance na gaskiya a halin yanzu Imam ne kaɗai hope ɗinmu."

Wani irin kuka Amina ta fasa tana girgiza kai "Dama ku daina kawo shawarar neman taimako a wurin  Imam domin nasani ba taimaka mana zai yi ba."

"A'a zai iya ko dan albarkacin ki Amina."

"Faruk dan Allah abar wannan magana dan kwata-kwata hankalina ba zai dauke ta ba."

"Saboda bakyaso na sami lafiya Amina ko bakyasan mu cigaba da rayuwa a tare?"

Kamar daga sama taji saukar muryar Abdallah a kunnenta.

Ta yada idanunta akanshi cikin firgici take kallansa, domin bata taɓa tsammanin fitar wannan maganar daga bakinsa ba hasali ma ta dauka yana bacci, dan tun jiya da likita ya fada musu halin da yake ciki, suke kunbiya-kunbiya dan kar yaji hankalinsa ya ƙara tashi dan a dalilin wannan ciwo har ya kamu da hawan jini wanda ada bashi dashi. Kallonsa kawai take idanunta na cicciko da hawayen tausayi da ƙaunarsa, duk abun da zai sa Abdallah ya amince da neman taimako a wurin Imam ba ƙaramin abu bane, sai kuma ta tuna magana ce ake ta tsakani rai da mutuwa, sai taji tausayin shi ya ƙara lullubeta, da wani irin rauni cikin muryata ta ce "Duk duniya bana tunani akwai wanda yakaini san gani samuwar lafiyarka Abban Jabeer saidai ina cike da fargabar yadda za mu tunkare Imam da wannan babbar buƙata, ka fi kowa sani idan da akwai abun da ya tsana ni da kai ne kayi haƙuri mu fallawa wa Allah ikonsa." Ta karasa magana tana jin wani irin kunci can kasan zuciyarta shima Abdallah daga wannan maganar da ya yi bai ƙara cewa komai ba sai kawai ya juya musu baya tare da lumshe idanunsa. Usman da Faruk ba suyi ƙasa da gwiwa ba suka cigaba da rarrashin Amina da tunatar da ita muhimmancin lafiyar mijinta har ta sauko ta amince, ba anan gizo ke saƙa ba ta yaya ta ina zasu fara neman taimako Imam "Faruk ku je tare da Usman tun da yasan gidanshi kuma suna shiri sosai dashi, ni ba sai naje ba."

"Haba Amina miyasa kike da taurin kai ne hmm?" Kamar kina mantawa da irin zazzafar kiyayyar dake tsakanin ƴan ɗakinmu da nasu Imam, tamkar ba mahaifi daya ne yai silar zuwanmu duniya ba. Idan har ni na tunkare Imam wallahi-azim ko kwadala ba zai bayar ba, amma ke ina da yakini akanki."

"Yaya Amina abun da yaya Faruk ya faɗa gaskiya ne kece yafi cancanta ki je ki sami shi ko babu komai cousin dinki ne uwa ɗaya ta tarbiyyatar daku ya kamata zuwa yanzu ku watsar da abun da ya faru acan baya, ku cigaba da zumuncinku Allah bayasan mai yanke zumunci."

"Banida laifi Usman duk abun da ya faru laifin Imam ne, amma ba komai dukawa wada baya hana tashi da tsawo." Da wannan kwarin gwiwa Amina da Usman suka nufi gidan Imam dake maitama, sai dai can kasan zuciyarta tana cike da zullumi da fargabar abun da zai faru, musamman kafin su fito da Abdallah ya riƙe hannayenta yana zubda hawaye yana rokonta Allah ma'aiki ta sauke duk abun da take ji akan Imam ta roke shi koda durkusa masa ne tayi shi dai a ceto rayuwarsa domin shi kaɗai yasan irin azabar da yake sha. Around 3 taxi ta sauke su a gate ɗin gidan Imam wanda hakan ya haifar wa Amina da matsanancin faduwar gaba har ƙwaƙwalwarta ta tuno mata da wani ɓangare na rabuwarsu yayin da muryarshi idan yake kuka ya dinga mata echo a kunnenta, da wani kalar sauri ta dafe kunnuwanta ga jiri dake dibar ta. Usman bai tanka mata ba duk da ya lura da halin da ta shiga, sai ma hannunta ɗaya da ya kama ya cire shi daga kunnenta, yaja sanyayyu kafafunsa ya isa ga gate ɗin gidan ya yi knocking jin kadan sai ga maigadi ya leko yana sanye da uniform kalar ruwan ƙasa, yana gani Usman yasaki fuskarsa, har ya miƙa masa hannu sukai musabaha "malam Usman kaine atafe kwana biyu ka daina leko mu ko duk bautar ƙasa ce ta boye ka?"

Da murmushi akan fuskar Usman ya bashi amsa kana suka wuto cikin gida, mai aiki kaɗai suka tarar a babban falo suka umarce ta da ta kira masu matar gidan ta amsa musu da to ta wuce ɗakin Jamila tai knocking tare da faɗa mata tayi baki,mamaki ne ya lullube ta su waye dan bata expecting din zuwan kowanne bako a gidanta amma duk da haka ta amsa da cewa su jira gata nan fitowa. Tana fitowa tai tsaye turus ta kasa karasawa saima murza idanunta ta dinga yi "Wa nake gani haka Usman kamar Amina anya ba idanuna gizau suke min ba?"

Ɗan ƙaramin murmushi Usman ya yi tare da fadin "Ita ce aunty Jamila ya gida da yara?"

Karaso wa Jamila tai fuskarta cike da fara'a ta amsa wa Usman kafin ta zauna kusa da Amina tana tambayarta ya jikin maigidanta Amina ta amsa da sauki bayan sun gama gaisawa Usman ya sako da makasudin zuwan su "Aunty Jamila Ya Imam yana gari kuwa?"

"Yana nan Usman ai ba ƙaramin sa'a kuka taka ba dan kuwa jiya-jiya nan ya dawo daga tafiya tsawon wata ɗaya bayanan yaje wani training a Ghana, sai dai ya fita amma ba nisa ya yi ba bara na kira muku shi a waya."

Ta kwallawa mai aikinta kira taje bedroom ta dauko mata wayanta, bayan ta kawo mata tai dialling lambar mijin nata, sai da ta kusan tsinke wa sannan ya daga cikin kakkausar muryar da yake mata amfani da ita ya furta "Ke ya aka yi ne?"

Yayin da ita kuma ta amsa mishi da wani irin sanyi "Daddy ka yi babbar bakuwa?"

Sai da ya gama shan ƙamshin sa kafin ya ce "Bakuwa daga ina?"

"Aminar Aayya ce suka zo tare da Usman ashe anyi referring ɗin Abdallah a national hospital."

Wani irin shock yaji jikinshi ya dau rawa tsohon miki dake can kasan zuciyarsa ya dawo masa sabo fil hatta da miyau bakinsa sai da suka canza teste, ya shiga kokawa da numfashin sa, take noise bleeding ya subuce masa sosai jini ke fita daga hancinsa idan Allah ya taimake shi idan yake shi kaɗai ne, jin shirun sa ya yi yawa yasa Jamila ta kashe wayarta dan tasan halin miskilanci mijin nata, ta ce dasu gashi nan zuwa da kanta ta shiga kitchen ta haɗo musu abinci da drinks, ta zauna suna fira da Usman jefi-jefi abinci ma shi kadai yaci iyakaci Amina tasha ruwa suma dan tana jin yadda maƙoshinta ya bushe ƙamass! Da ba dan haka ba, da ba abun da zai kaita shan ruwan gidan Imam Mamman Wali.

#Tareeq Imam

#soyayya

#Tausayi

#Nadama.

Aayya ta ce a gayamuku kada ku shagala da karanta Free page ku manta da na kuɗi ne😂

Ta ce ga masu buƙatar ci-gaba da karanta wannan littafi za su biya 700 kacal ta wannan asusun banki 7032566272 Hauwa Shehu opay. Aayya tayi arha ta hana bashi dan haka ku hanzarta ku nunawa shalelenku Tareeq ƙauna, duk da Tareeq yace a baku part one kyauta amma part two kun dai gane, kusan Tareeq ɗan albarka ne yana yin ku.

Jeeddah Aliyu

07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Hauwa Shehu Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewbook@jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

013.

Sun dau kusan mintina ashirin a zaune kafin sun ji sallamarshi cikin husky voice ɗin nan nasa, Usman da Jamila ne suka amsa masa yayin da gaban Amina ya cigaba da dukan tara-tara duk sai taji ta tsargu ta ma kasa kallonsa to da wane irin ido ma zata kalli Imam har ta iya rokarsa ya taimaki mijinta ya ceto rayuwarsa. Usman ne ya tashi ya miƙa masa hannu suka gaisa cike da wannan izzar tasa wacce tana cikin abubuwan da Amina ta tsana ko can baya,ya nemi kujera ya zauna tare da crossing legs ɗinsa. Duk yadda Amina taso ta dago ta kalle shi kasawa tayi tun ma kafin yasan makasudin abun da ya kawo ta gidansa har tafara jin nadama zuwanta, wani irin kallo ya aika wa Jamila kafin adakile ya furta "Jamila bamu wuri zan gana da ƴan uwana?"

Sosai Jamila taji zafin maganarsa tsawo shekaru goma da aurensu ta kasa sabawa da wulakancinshi, ta tashi rai ɓace ta wuce ɗakinta shiru ya biyo baya kowanne su ya kasa magana sai sake-sake suke, can Imam ya kalli Usman ya ce "Usman kun sa an kirani nazo kun yi banza dani alhali na baro tarin ayyuka masu muhimmanci, nazo nan."

Sai lokacin Amina tai ƙarfin halin dagowa ta kalle shi fuskarshi a hade kamar bai taɓa sani me ake nufi da fara'a a rayuwarsa ba, nan take wani irin mugun tsaro da shakkar sa suka sami matsuguni a zuciyarta, zata ma iya cewa tsawon rayuwar da suka yi acan baya bata taɓa jin tsoron sa irin yau ba, sai ma taga ya dawo mata wata irin halitta ta dabam. Shi kanshi Usman ya razana da yanayin fuskar Imam shiyasa ya rasa ta ina ma zai fara zancen.

"Usman idan ba zakuyi magana ba zan fa tashi nai tafiyata kasan ni ina bawa lokacina matuƙar muhimmanci domin abu ne shi idan ya wuce ba zai taɓa dawowa ba har abada."

Yadda ya yi magana yasa Amina ta kafe shi da jajjaye idanunta tana kallon farar fuskarshi mai zagaye da baƙin saje mai haɗe da gemu, can kuma ta ɗauke kanta, tana daɗa jin nadamar kawo kanta gidan Imam.

"Yaya dama mun zo ne dangane da rashin lafiyar yaya Abdallah?"

"Hmm! Jikin ya yi tsanani kenan?"

Ya tambaya cikin halin ko in kula sosai yanayi da yai tambayar dashi ya ɓatawa Amina rai, saidai ya ta iya tun da ita ta kawo kanta dole ta shanye duk wani wulakancinshi.

"Amina ya jikin mijin naki?"

Kamar daga sama taji ya jefo mata da wannan tambayar saida ta hadiye miyau, kafin cikin rawar murya ta amsa masa "Da sauki."

"Allah ya bashi lafiya."

Ya yi magana idanunsa na kan wayarshi dake hannunshi. Nan ma shiru sukayi na wani ɗan lokaci kafin Usman ya kawo karshen shiru nasu "Yaya Imam dama Amina ce tace na rakota wajen ka, ka taimaka masu saboda za a yiwa yaya Abdallah surgery to asibiti ne suka bukaci kimanin naira Miliyan tamanin,su kuma basu dashi sh...

Cike da izza ya katse Usman yana faɗin

"Anya kuwa Usman Amina ce tace ka rakota wajena? Kodai tursasata ku kayi dan nasan ko karen hauka ya cije Amina ba zata zo guna neman taimako ba?"

"Allah yaya ita ce ta nemi hakan da kanta."

Usman ya faɗa cikin rawar murya yana dan zungurar ƙafar Amina da ƙafarsa da nufi tai magana, wani malalacin kallo Imam yake aika mata kafin ya tabe baki yana faɗin "Ban ga alamar hakan a tattare da ita ba Usman."

"Dan Allah Imam ka tai...

Sai kuma ta kasa karasawa sakamakon wani irin kololo da yazo ya tokare mata kirji, sai kawai ta fashe masa da matsanancin kuka. Wani irin abu Imam yaji ya dakar mai zuciya kukan Amina shine babban makamin dake saurin raunata masa zuciya, ya rasa wane irin masifaffe so ne yake mata da tsawon shekaru nan ya kasa cireta daga zuciyarshi ya kasa goge babin ta a cikin rayuwarsa, tabbas ya ƙara yarda da so abin banza ne da yake kai zuciya idan za a wulakanta ta, gurin da ba a san daraja da kimarta ba, ba dan so ya kasance abin banza ba yaushe ne kukan Amina zai yi tasiri akansa?"

Kokari ya yi ya danne abun da yake ji yana taso mai ya kalli Usman ya ce "Usman bamu wuri zamuyi magana dan waƙa abakin mai ita yafi dadin sauraro."

"Tau yaya!"

Usman ya faɗa tare da tashi ya fita waje a zuciyarsa yana wa Amina addu'a fatar samun nasara.

Amina kasa magana tai sai kawai ta sami kanta da rera wani irin kuka mai matuƙar ban tausayi duk rashin imanin ka, idan kaga yadda take wannan uban kukan dole ka ji tausayinta ya ratsa ka, bare zuciya irin ta Imam dake adane da tsohuwar zazzafar soyayyar ta. Ya ajje wayarsa a hannun kujera ya tallabe kumatunsa yana kallonta ta dau lokaci tana kuka, kafin ya miƙa hannu ya dau tissue box ya taso ya miƙa mata, batai gardama ba ta amsa ta zaro guda biyu ta goge fuskarta cikin dusashewar sauti Amina ta ce "Dan Allah Imam ka taimaka ka ceto rayuwar ɗan uwanka, bamu da wadannan kuɗaɗe bamu da mafitar su kai kaɗai ne muke sa ran za ka taimaka mana, Abban Jabeer yana cikin mayuwacin hali na rai ko mutuwa."

"To ku barshi ya mutu mana dole ne sai ya rayu."

Kamar saukar aradu haka Amina taji saukar wannan maganar ta Imam dan sai da ta fado daga kan kujera, idanunta suka firfito ta watsa su akan murtukakkiyar fuskarshi da babu alamar rahama ko jinkai akanta, ya dawo mata wani irin mugun mutum marar imani.

Cikin sautin kuka Amina ta buɗe bakinta ta ce "me kake cewa Imam?"

Kansa tsaye yasake maimaita abun da yace kuma babu nadama a cikin furucin nasa "Cewa nayi

tun da bakuda kuɗi da za ku biya ai masa surgery ku barshi ya mutu ai wani lokaci mutuwa hutu ce ga musulmi musamman shi da yake shan wahala, infact waƴansu mutane sun cancanci mutuwa, ko ba ki taɓa jin wani karin magana da ake cewa faduwar wani tashin wani ba?"

"Innalillahi wa'inna illaihim raji'um!  Imam kai wane irin mutum ne wacce irin zuciya ce dashe a kirjinka?"

Ya dage girar ido yana kallonta yana murmushi mai nuna zallar muguntarsa a fili, ya ce "irin wadda take dashe a kirjinki Amina ai ni ɗan kwaikwayo ne duk abun da nayi daga gunki na koya."

Har zuciya ta dibe Amina da tashi tai tafiyar ta sai kuma ta tuna da halin da ta baro mijinta, kuma Imam shi kaɗai ne hope ɗinta shi kaɗai ne kaf zuri'ar marigayi Mamman Wali da yake da arziki taimaka musu "Ka yi haƙuri Imam ka tuna ba a rama gayya da mugunta Abdallah ɗan uwanka ne da ku ka haɗa uba ɗaya kada ka yi duba da alakar dake tsakanina dakai ka kasa taimakon ɗan uwanka yana halin rai ko mutuwa, nasani tun fil'azal akwai kwatacciyar gaba ta ƴan ubanci a tsakanin ku, amma bashi zai hana ka taimake shi ba domin jini ba wasa bane."

Wani shegen murmushin gefen baki ya sakar mata tare da mikewa ya dau wayarsa ya kare mata kallonta tass! Kana ya buɗe bakinsa cikin izza da baƙin wulakanci ya ce "Alhamdulillah! Na ji daɗi da ya kasance ni ina da abin da ke da mijinki kuke nema agareni kuma na mallake shi hakazalika ko wanda ban taɓa sani ba yazo min da buƙata irin waccan kika zo da ita sai inda karfina ya ƙare, sai dai kashh! Ke da mijinki ne Amina ba zan taɓa iya taimakon ku ba. To me zai sa na taimaki makiyina? Bayan Ubangiji ya kawo min hanyar da zai dawo min da abuna da ya rabani dashi ki je kawai ina jiranki idan kin gama takaba zan waiwaye ki, kinsan ni masoyi ne nagari bana taɓa gudun abun da nakeso koda yayi min halin butulci."

Yana karasa magana ya nufi kofar fita wata irin wutar kiyayyar shi Amina take ji tana ruruwa a kaftanin zuciyarta. A fusace ta dakatar dashi ta hanyar cewa "Ayau na kara jinjina wa jahilci ka Imam kana musulmi amma kake murna dan ɗan uwanka musulmi yana cikin lalura ta ciwo har kake mai fatan mutuwa, ka manta cewa daga kai har shi rayukan ku ba a tafin hannun ku suke ba, sau nawa ma aka yi mai lafiya ya mutu yabar mai jinya idan Ubangiji yaga dama sai ka riga Abdallah mutuwa dan haka ka daina murnar karenka ya kama zaki domin wannan zaki bana wasa bane, har abada na haramta gare ka koda kuwa ta Allah ta kasance da Abdallah yadda Annabi ya haramta da wuta haka na haramta gare ka Imam Mamman Wali."

Batare ya juyo ya kalleta ba ya make kafadunsa ya fice abinsa, ta share fuskarta ko sallama bata yiwa Jamila ba ta fice sai da suka dau hanyar komawa asibiti take fadawa Usman yadda suka yi da Imam, jikin Usman duk ya yi sanyi a haka suka dawo asibiti kuma bata ɓoyewa Faruk da Abdallah komai ba dan bata ga amfani ɓoyewar ba tun da dama sune suka tursasa ta.

Bayan kwana shidda!

Jikin Abdallah ya ƙara tsanani hankalin Amina dana ƴan uwansa yai bala'in tashi sai fafutukar

neman kuɗi suke yi hatta acan Katsina ƴan uwan Abdallah sun shiga neman taimako a wurin dangi mai taro mai sisi har masallatai suke neman taimako, tare da bin gidajen ƴan siyasa, dakyar aka haɗa miliyan uku, wanda aka turowa da Faruk, sai dai tun ba a je ko'ina ba kudaden dake hannunsu da suka zo dasu suka kare tass! A wajen siyen magani ga kuma dialysis din ake masa, dole suka fara taɓa miliyan uku ɗin a wata safiya wanda ya yi daidai da cikar Abdallah kwana goma sha uku a asibiti, Amina tana cikin goge mai jiki kamar yadda take mai duk safiyar Allah, Abdallah ya riƙo  hannunta mai ɗauke da ƙaramin towel ɗin take goge mai jiki, cikin gaunin ciwo da rauni na wanda ya gama fidda rai ga rayuwa ya ce "Amina!"

"Na'am! Ta amsa masa cike da kulawa har tana haɗawa da shafa fuskarsa da ɗayan hannunta "Amina ki yi haquri ki sake komawa wajen Imam wallahi ni kaɗai nasan irin kalar azabar da nake ji cikin jikina mutuwa dole ce akan kowanne ɗan adam amma wahala ce bata da daɗi, Imam yana sanki zai iya yin komai akanki."

Sosai Amina ta ji ranta ya yi mugun ɓaci amma sai tai ƙoƙarin danne wa saboda tasan halin da Abdallah yake ciki abin a tausaya masa ne ai masa uzuri dan haka ta nemi kusa dashi ta zauna tana mai ƙara damƙe hannun shi dake cikin nata, cikin kwatar da murya ta ce "Abban Jabeer ban ƙi ta taka ba, ba kuma wai ba zan iya komawa wajen Ya Imam bane kawai dai komawar ce bata da wani amfani, dan ko sau dubu zan je wajensa ba zai taimaka mana ba, dan haka dan Allah ka cire shi a lissafi mutane da zasu iya taimaka mana."

"Nikam Amina kina kuwa san na sami lafiya?"

"Haba Abban Jabeer wannan wacce irin magana ce?"

"Idan har da gaske kinasan lafiya ta, ki danne duk abun da kike ji akan Imam kamar yadda na danne idan kuma kinasan na mutu ya sami damar aurenki shikenan."

Sosai Amina taji zafin waɗannan kalaman na Abdallah tamkar an yayafa mata tafasasshen ruwan zafi a zuciyarta, sosai ta sha kuka har yaya Kabir ya shigo ya tarar da ita tana kuka abin mamaki shima da ya ji abun da ya faru sai ya goyi bayan ɗan uwansa ba dan zuciyarta taso ba, haka ta kira Imam tanasan ganinsa dan tayi alkawari ba zata ƙara zuwa gidansa ba. Da kanshi yazo asibiti dan wulakanci sai ya tsaya a wajen gate ya kirata, tana ƙoƙarin buɗe kofa ta fita Abdallah ya kira ta "Amina dan Allah kada ki bari wannan zafin kan naki ya hana Imam ya taimaka min, ki kwatar da kai ki roke shi idan ya kama ki durkusa akan gwiwarki ki dafa kafafunsa kin ji Amina?"

Amina ta juyo ta kalle shi tana jin wani abu yana tsagar mata a zuciya, sai kawai ta gyada kai ta fice. Imam yana tsaye jingine da jikin motarsa yana waya ganinta yasa shi katse wayar as usual fuskarsa a murtuke.

Sallama tayi ya amsa kamar bayaso kafin ta daidaita tsayuwarta, cikin sanyi murya ta ce dashi "Ya gida da iyali?"

"Lafiya!"

Ya amsa a takaice shiru Amina tayi kamar ba zatai magana ba sai taja numfashi tare da saukewa "Na kira ne akan waccan taimako da muke nema a gareka Imam, dan Allah ka tausaya wa rayuwar Abdallah wallahi yana cikin tsananin zafin ciwo, da za ka ganshi na tabbata sai ka tausaya masa."

Ta ɗan dakata domin taji ta bakinsa sai dai shiru bai ce komai ba. Da ta gaji da shiru nasa tasake cewa "Imam baka ce komai ba sai waya kake latsa anya kuwa kana ma saurarena?"

Ya ɗago da girar ido dage ya kalleta sai kuma ya kauda fuskarsa yana faɗin "Na ji ki sarai Amina ba abun da ban ji ba ko kinasan na maimaita miki abun da kike ce?"

Ta girgiza kai tana ji sanda hawaye suka zubo mata tai sauri kai tafin hannunta ta goge.

"Amina!"

Ya kira sunanta cikin ƙaramin sauti ta amsa da "na'am!"

"Amina ni fa kaifi ɗaya ne kema kin san da wannan bana amai kuma na bishi na lashe, wallahi-azim ko duk duniya ce zata taro akaina ba zan taimakawa Abdallah da single kobo from my pocket gwada ki daina wahalar da kanki ku nema a wani wuri ba zan iya ba."

Da sauri ta zube gabanshi ta kama kafafunsa tana wani irin gunji kuka "Dan Allah Imam...

Bai bari ta karasa ba ya yi sauri janye kafafunsa ya kalleta da rauni a zuciyarsa yana ji da zai iya da ya taimaka ko dan albarkacin ta, sai dai wani bangare na zuciyarsa yake haska mai irin wulakanci da tai mai a baya, ya juya da sauri ya shiga motarsa ya barta anan wuri har ya yi nisa yana kallonta ta jikin mirror mota. Wani tukuki Amina take ji a zuciyarta a haka ta koma cikin asibiti tana kuka tana gayawa Abdallah abun da ya faru hakan ya tunzira shi ya kamo hannunta ya riƙe, yayin da hawaye ke bin rammamiyar fuskarshi cikin murya ta wadda ciwo ya gama cinye wa yake magana "Ki min alkawari Amina ko bayan babu ni ba za ki haɗa hanya da Imam ba balle har aure ya shiga tsakanin ku domin nasani duk wannan abin da yake yi har yanzu da sonki a zuciyarsa yana ji asarar ya taimake ni dan kar na rayu idan na mutu ya aure ki...

Da sauri Amina ta rufe mai baki da tafin hannunta tana kuka ta ce "Ko ba ka faɗa ba Abban Jabeer na haramta wa kaina kowacce irin alaƙa da Imam kai hatta da zumunci dake tsakanin mu ayau na yanke shi, saboda ban ga amfanin sa ba. Wallahi Abban Jabeer a halin babu komai a zuciyarta sai tarin tsana da kiyayyar Imam."

Tun daga wannan ranar kullum sai Abdallah yasaka Amina tai mai alkawari ko bayan ransa ba zata aure Imam ba. A haka ta cigaba da jinyarsa har sukai sati uku a Abuja kafin shi da kanshi ya nemi su maida shi Katsina yana so ya mutu cikin danginsa, a ranar suka nemi sallama dama likitoci da ke duba shi sun gano ɗayar kodar ta kamu da cutar sosai, shiyasa ba suyi gardama ba suka sallame su a washegari suka koma Katsina. Ga baki ɗaya ƴan dakinsu Abdallah da suka ji ƙi taimakon Abdallah da Imam ya yi sai suka ƙara rura wutar gabar dake tsakanin su dan tun sanda Abdallah ya kwanta jinya idan ka cire Maimunatu babu wanda yazo cikin diyan Aayya ya

duba shi ita ma Maimunatu bai fi sau biyu ko uku ba tazo da Aayya ta sami labari taje ta zauna ta ƙare mata tanadi daga sannan bata koma ba, sai dai tana kokarin aika ma Amina da kuɗi a boye saboda suna shiri sosai. Tun dawowarsu jikin ya ƙara rikicewa sau biyu ake mai dialysis a sati amma yanzu sau uku ake yi, gashi babu wasu kudin kirki a hannunsu. Gani halin da Abdallah yake ciki yasa Baaba Karime ta dau ƙafa ta je gidan Aayya ta zube gabanta tana kuka tana mata magiya da taimaka ta wa Imam magana, amma haka Aayya ta rufe ido ta gaggaya mata magana iya san ranta da ta gama ta shige ɗakinta ta bar Baaba Karime a zube tsakiyar falo gwanin ban tausayi. Wannan abu da Aayya tayi wa Baaba karime yasa ta kulace ta kuma shi ne silar ƙara hassassa mummunar gaba a tsakanin yaransu, dan kuwa Baaba Karime tana komawa gida ta tara yaranta ta gayamusu ko bayan ranta bata yarda zumunci ya sake shiga tsakaninsu da ɗiyan Aayya ba. Ita da ƴaƴanta suka saka Amina gaba suna mata gargadin ko Abdallah ya mutu wallahi ba zata aure Imam ba. Ita Amina bin su kawai take da kallo dan tuni ta daɗe da dasawa zuciyarta hakan.

#Amina

#Abdallah

#Imam.

#TeamTareeqImam.

WANNAN LITTAFI NA KUƊI NE FREE PAGE NA GAF DA KAREWA, GA MAI BUKATAR CIGABAN WANNAN LABARI ZAI IYA TURA NAIRA 700 KACAL TA WANNAN ASUSUN BANKI 7032566172 HAUWA SHEHU OPAY SHAIDAR BIYA TA WANNAN LAMBA 07032566172. NA GODE.

[7/6, 7:24 AM] Hauwa Shehu Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

From the writer of NI DA YAYA HABEEB.

014.

Tun bayan rabuwar Imam da Amina ya kasa samun natsuwa ko bacci ya kwanta sai ya yi

mafarkin Amina tana kuka tana rokonshi ya taimaki mijinta kada ya mutu, duk yadda yaso ya kwata ya yi bacci sai ya kasa gashi ko cin abincin kirki baya iya ci sai dai ya tsakura, damuwa da tunani sukai mai yawa watarana juma'a ana saukowa daga masallaci ko iyalinsa bai faɗa mata ba, ya dau hanyar Katsina tun kafin ya iso ya kira Maimunatu ta binciko mai asibitin da Abdallah yake. Tun kafin ya sanar da ƴan uwan shi dalilin zuwanshi suka kore shi tare da yi mai mummunan wulakanci, duk da haka Imam bai yi ƙasa da gwiwa ba ya nemi Maimunatu da ta yi magana da Amina a shirye yake da ya kashe ko nawa ne Abdallah ya sami lafiya yasan ya yi kuskure yana nema afuwarta tayi hakuri ta yafe masa sharrin zuciya ne.

Da yake Amina babu abin da takeso sama da lafiyar mijinta, ta amince har suka hadu da Imam ɗin suka tattauna daga nan ta dawo asibiti bata ɓoyewa musu ba ta gayamusu bukatar da Imam yazo da ita, ai kuwa suka rufeta da fada da zagi hatta da Abdallah nuna ya yi baya bukatar taimakon Imam a kyale shi ya mutu shi yama gama cire rai da samun waraka saboda dukka kodujinsa sun lalace, Imam bai taimake shi ba sanda ya nema ba har sai da yaga babu tabbacin zai rayu dan haka bayaso kuma kar ta sake yi mai maganarsa.

Imam bai hakuri ba yasake dawowa Katsina ya koma asibiti, duk da a lokacin Abdallah yana ciki mayuwaci hali hakan bai hana shi fatattakar Imam ba. Tare da yi masa gargadi ya fita sabgar matarsa don yasan har yanzu yana sonta. Kwana Imam uku a Katsina ba irin rarrashi da bai yiwa Abdallah da Ƴan uwansa ba kai har ma da Baaba Karime amma suka kafe lallai basa buƙata har Abdallah yana cewa idan har Imam ne kaɗai zai taimake shi ya gwammace ya mutu.

Yayin da Amina ta nemi Imam da biya kuɗi ba tare da sani Abdallah ba. Shi kuma Imam ya ce ba zai yi haka ba muddin ba da amincewar Abdallah ba, babu wani taimako da zai iya mata. Amma ya mata alkawari duk sanda Abdallah ya amince a shirye yake da ya taimaka. Daga haka ya juya ya bar cikin asibiti. A lokaci babu kalar roko da magiya da Amina bata yi masa ba har sake durku masa tayi. Amma a haka ya tafi ya barta durƙushe a ƙasa tana kuka duk da har can ciki zuciyarsa bai ji daɗi hakan ba.

Bayan sati biyu da faruwar haka Allah ya karbi ran Abdallah, ba wanda zai iya kwatanta irin tashin hankali da Amina ta shiga ga baki ɗaya ta dawo abar tausayi. Rasuwar Abdallah ya kawo daidaito tsakaninta da Aayya, dan gidanta Aayya ta dawo tana tayata zama tun kafin Amina ta gama takaba ta fahimci take-taken Imam yayin da ta saka aranta koda mazan duniya sun ƙare ba za taɓa aurensa ba. Domin kuwa tana jin haushi yadda yaki amincewa ya taimaki rayuwar mijinta a cewarta dama can burinsa kenan Abdallah ya mutu kamar yadda ya taba gayamata. Imam ya fito da maitarsa fili kanta don haka ita kuma tasha alwashi haramta masa kanta. Tana kammala takaba da watanni ukku Imam ya bayyana mata buƙatar shi naso aurenta, bata yi ƙasa da gwiwa ba ta faɗa masa zahirin gaskiya ba za ta iya aurensa ba koda kuwa shi kadai ne namijin da ya rage a duniya. A wannan karo Imam Wali ya shirya tsaf dan gani ya aure Amina ko tana sonsa ko bata so hakan bai damuwarshi ba ce. A bisa shawarar Aayya suka dunguma zuwa Baurawa wurin malam Yusufu mahaifin Amina ba tare da malam Yusufu yaji ra'ayin Amina ba ya ɗaura mata aure da Imam Wali. Kusan rabin hauka Amina da ƴan uwan Abdallah suka yi dan har gida suka zo suka kare musu zagin ƙare dangi ita da Aayya, al'amarin da ya janyo Imam

ya nuna musu ƙarfin arziki dan kuwa sa wa ya yi police suka kwashe su akai kai mai su cell, sai da Baaba Karime ta je har kusada ta gayawa wani kawunsu wanda shi kaɗai ya rage musu yazo ya yiwa Imam magana sannan fa yasa aka sake su, da nufin shi ya maka su kotu amma sai da yasa akai musu iyaka da Amina, su kuma daga wannan lokaci suka yi fushi mai tsanani tare da karɓe Jabeer.

Amina tayi duk bore da zata iya ba wanda ya kulata daga ƙarshe sai kakkausar kashedi mahaifinta yai mata wanda yasa dole ta zauna da Imam Wali a matsayin mijin aurenta. Babu kalar ƙaunar da Imam Wali bai nuna mata ba amma a banza, domin duk lokaci da zai yi tarayyar aure da ita sai sun yi artabo sai dai ya nuna mata ƙarfi a haka ta haifi yara uku Fadila Khadijah mai sunan Aayya shiyasa suke kiranta da Baby sai Tareeq wanda tun daga haihuwarsa Imam ya tattara ya daina nuna bukatar shi akanta dama burin shi ya sami ɗa namiji kuma ya samu,tsawon shekaru 14 kenan rabo da su haɗa shimfida dan kuwa Imam ya yi alkawari sai dai ita ta kawo kanta gareshi yayin da ta bangaren Amina hakan gaba yakaita a cikin shekaru da suka gabata Imam ya sami daukaka sosai wanda yanzu haka yana riƙe da muƙamin special adviser to the president on political matters(mai ba shugaban ƙasa shawara kan harkokin siyasa) inda matarsa Jamila ke da yara uku dukka mata Zahra, Bilkisu sai kuma Zainab wacce take sa'ar Baby. Kuma suna zaman lafiya da Amina saboda Jamila mace ce mai hakuri da kauda kai shiyasa zaman su ya yi daɗi. Kasancewar Tareeq shi kaɗai ne ɗa namiji a wurin Imam Wali shiyasa yake nuna masa wata kalar soyayya Imam wali irin mutanen ne masu fiffita ƴaƴa maza akan ƴaƴa mata dan haka Tareeq ya taso ba faɗa ba kwaɓa tsanani gatan da yake nuna masa yasa kangare ya zama fitinannen yaro da baya ji maganar kowa baya kuma tsoron kowa tsageranci ba kalar wanda ba ya yi. Kuma ba uban da ya isa ya ɗaga mai ko ɗan yatsa saboda yana da goyon bayan mahaifinsa former general controller wanda bayan ya yi retirement ne ya tsunduma harkokin siyasa. Kiri-kiri Alhaji Imam Wali ke nuna bambanci tsakani yaransa mata da Tareeq ko kaɗan baya iya ɓoye zallar soyayya da yake mai. Ita kam Hajiya Jamila ko kaɗan hakan bai dame ta ba domin ita ma tana ƙaunar Tareeq tamkar ɗan da ta haifa da cikinta a dalilin sunan mahaifinta da Imam Wali ya saka masa. Yayin da a bangaren Ummi da yaranta suke nuna masa wata kalar tsana, tamkar ba ita ta haife shi ba su kuma ba ƴan uwanshi na jini ba.

{END OF FLASH BACK)

A lokaci guda Ummi da Fadila suka sauke naunnayar numfashi kafin Fadila tai ƙasa da muryarta ta ce "Ummi ba ki faɗa min ya aka yi, Ya Jay ya dawo hannun Daddynmu domin tun sanda nayi wayau nake gani Ya Jay a gidanan da farko na zaci ubanmu ɗaya dashi sai daga baya na fahimci uwa kaɗai muka haɗa shima a dalili yadda Daddy ke kiran Tareeq da suna magajinsa?

Sai da ummi ta sake furzar da iska daga bakinta kafin ta ce "Duk da kasancewar Imam yana da murɗaɗɗen hali amma a wani ɓangare yana da kirki, tun sanda ƴan uwan Abdallah suka karɓe shi na shiga damu dakyar nake iya bacci gashi ko na je Baaba Karime ba zata barni na gashi ba, in kuma a tarar dashi tsakar gida za ta ɗauke shi ta shige daki ta rufe Jabeer yana kuka ina har in karashe magiya ta, ba zata ba zata saurare ni ba. Rashin Jabeer ya haifar min da

matsananciyar damuwa sannan na sami labarin irin riƙon sakaniyar kashi da Baaba Karime take mai gashi banida yarda zan yi domin a lokaci nayi zato yarda Imam ya tsani Abdallah ba zai riƙe masa ɗa ba sai ga Imam ya shayar dani mamaki, dan kuwa da ya fahimtar dalilin shigata damuwa ba tare da sanina ba yaje Katsina sai gashi ya dawo da Jabeer bansan ya akayi har Baaba Karime ta amince ta badashi ba wanda har yau ɗinan bai gayamin dalili da yasa ta bashi Jabeer ɗin ba, duk wani abu da uba yake wa ɗansa domin inganta masa rayuwa Imam ya yiwa Jabeer. Wanda a dalili hakan sai da Hajiya Jamila ta dauko ƙaramin ƙaninta Hamza ya dawo gidanan. Kasancewar Jabeer sa'an Hamza ne sai ya zamana komai tare Imam yake musu hatta da ƙasar waje tare ya tura su karatu wanda ahali yanzu su ke kula mai da kasuwanci sa anan Kano. Lokacin da Imam ya ajje aiki shine ya dawo nan Kano ya gina katafare gidan da muke ciki, saboda harkokin kasuwancinsa sun fi yawa anan.

"Ummi saura ki faɗa min yadda Uncle Usman ya aure mahaifiyar Gifty?

"Bayan Usman ya kammala karatun shi sai ya sami aiki a National agency for food and drug Administration and control (NAFDAC) a garin Kaduna can Allah ya haɗa shi da A'ishah iyayen A'ishah asalin su buzaye ne mahaifin A'ishah yana aikin gadi a kusa da gidan da Usman yake haya, cikin hukunci Ubangiji soyayya mai ƙarfin gaske ta shiga tsakani Usman da A'ishah lokaci da Usman ya zo Katsina da zance neman aure A'ishah, Aayya ta daka tsalle ta dire ta ce batasan da zance ba. Maimunatu take so ya aura shi ma Usman ya kafe shi fa A'ishah yake so tun farko tasan tana so haɗa shi da maimunatu miyasa bata taɓa faɗa masa ba sai yanzu da ya kamu da ƙaunar A'ishah. Duk yadda Aayya taso haɗa aure Usman da maimunatu burin ta bai cika ba. An yi aure Usman da A'ishah sai dai Aayya bata ƙaunarta ko kaɗan a wurin haihuwa Tahreem ta rasu ba tare da ko fuskar 'yarta ta gani ba. Ranar suna yarinya ta ci sunanta A'ishah Ummi na mata lakabi da Tahreem yayin da ummi na nemi iyayen A'ishah dasu bani Tahreem wannan shi ne dalili zaman Gifty a gidan Imam Wali kusada.

#Jeeddah Aliyu

#Imam Wali

#Ummi

#Aayya

#Abdallah.

WANNAN LITTAFI NA KUƊI NE FREE PAGE NA GAF DA KAREWA, GA MAI BUKATAR CIGABAN WANNAN LABARI ZAI IYA TURA NAIRA 700 KACAL TA WANNAN ASUSUN BANKI 7032566172 HAUWA SHEHU OPAY SHAIDAR BIYA TA WANNAN LAMBA 07032566172. NA GODE.

[7/6, 7:24 AM] Hauwa Shehu Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

015.

Tareeq yana gani irin aika-aikar da ya wa Baby ya zame jikinsa ya shige part ɗinshi ya shirya cikin kayan ƙwallo red colour ƙafarsa sanye da red and black color football shoe, a bayan jersey ɗinsa an rubuta slugger 10 ba ƙaramin kyau footballwear ɗin suka yi masa, ya fito tamkar wani shahararrren ɗan wasan ƙwallon ƙafa wanda tauraronsa ke haskawa a faɗin duniya. Filin kwallo zai tafi amma sai da ya bi jikinsa da tsadaddun turarunkan Daddy da yake ɗebo wa.

Ya taje tulin sumar kansa wacce kullum cikin gyarata yake yana masifar ji da wannan sumar ta kanshi.

Yana fitowa daga part ɗinshi tun kafin ya kai gate ya hango direban ummi ya yi parking mota a daidai entrance ɗin shiga flat ɗin Ummi, Jabeer ya fito ta backseat kyakkyawan matashin saurayi mai jini a jiki shekarun sa na haihuwa ba zai su wuce 26 zuwa 27 Jikinsa sanye da blue long sleeve shirt tare da black cino trouser akwai suma akanshi sai dai ba mai yawa sosai ba da alama yana rage ta time to time. Fatar jikinsa chocolate color ce bashi da tsayi sosai. Yana tsaka-tsakiya shi ba dogo ba kuma ba gajere ba.

Direban Ummi ya buɗe car booth ya ciro luggage ɗin Jay yayin da direban sai doka murmushi yake Allah ya zuba wa ma'aikatan gidan ƙaunar Jabeer saboda tsanani kyauta da yake musu Jabeer mutum ne mai matuƙar kyautar gaske abinsa na kowa ne. Shiyasa yake da azababben farin jini bashi da haniya kuma ba miskili bane yana da wasa da dariya sai dai kuma ba kodayaushe ba. Akwai shi da masifar son girma musamman yanzu da yake gani shi ke shi ke jagorantar wasu daga business ɗin Imam Wali.

Jabeer da Uncle Hamza ko kaɗan basa shiri da juna a dalili kowanne su yana adawar da ɗan uwansa. Sai dai wannan ƙiyayyar da suke wa junansu ɓoyayyiyar ƙiyayya ce kowanne su yana ɓoye ki da yake wa ɗan uwanshi idan suka haɗu a wurin guda za su yi hira har da dariya, amma a can ƙasan zuciyoyin su Allah ne kaɗai yasan me suke ɓoyewa.

"Mtss!

Tareeq ya ja guntun tsaki tare da kauda fuskarsa da barin kallon side ɗin da Jabeer yake, daga Jabeer har Uncle Hamza bala'in haushin su Tareeq ke ji a cewarsa dukkan su suna ƙarkashin

daular ubansa amma suna mai wani gani-gani bayan sun kwana da sani shine magajin wannan dukiyar da suke hura hanci akanta.

"Kai Tareeq zo mana!"

Ya Jabeer ya ƙwalla wa Tareeq kira wanda ke kokarin gitta su ya wuce. Tareeq bai so tsayawa ba sai kuma wata zuciya ta ce ya tsaya mana ya ji uban me zai masa da yake kiransa dama fa ya kwana biyu bai yi rigima da namiji ɗan uwansa ba kullum faɗansa yana ƙarewa ne kan mata.

Cikin wannan tafiyar tasa ta izza da taƙama ya tunƙari wurin Ya Jabeer gashi ya wani ɗaure fuska tamau!

"Lafiya Jay ka ke ƙwalla min kira?"

Tareeq ya faɗa cikin dakakkiyar murya sa'ili da ya iso dab da Jabeer.

Jabeer bai yi mamaki da Tareeq ya kirawo shi da sunansa ba, saboda tun kafin Tareeq ya kai shekaru balaga baya kiransa da yaya kamar yadda su Fadila ke kiransa dashi.

"Malam musa ba shi jakkar ya shiga min da ita kai kuma ka gyara parking."

Jabeer ya yi magana yana murtuƙe fuska.

"To ranka ya dade.

Malam musa ya faɗa tare da sauke luggage ɗin Jabeer gaban Tareeq.

"Buhun b****uba nan jay ni ka ke cewa na ɗauka maka luggage??

Tareeq ya yi magana with angry voice har yana pointing ƙirjinsa.

"Kai ɗin ko ba za ka iya bane huh?

Shima Jabeer ya yi magana a hasale.

"Da dai ace nan gidan ubanka ne jay da ba abinda zai hana ni amma tun da ba gidan uban....

"Paaaaaaa!

Kafin Tareeq ya ƙarashe magana ya ji saukar five cuties fingers ɗin Jabeer akan kumatunshi.

"Idan iskaci da rashin tarbiyyar ka ya motsa kada ka sake ƙazamin bakinka ya ambaci sunan ubana, domin ubana ba abokin wasanka bane."

Tun sanda Jabeer ya ɗauke Tareeq da mugun mari yake dafe da kunce shi sai wani uban huci yake fitar wa, wata kalar muguwar zuciya ta taso mishi ji yake yi zai iya raba Jabeer da rayuwarsa.

"Dan Allah ka yi haƙuri ranka ya daɗe ka daina biye mai kaine babba ya kamata ka dinga haƙuri

da ƙañin ka. Bari na shigar maka da jakkar."

Malam musa bai tsaya jiran ji ta bakin Jabeer ba ya dau luggage ɗin ya nufi cikin gida. Jabeer ya yiwa Tareeq mugun kallo ya juya yana ci-gaba da zaginsa har zuwa lokaci Tareeq bai gama tunani kalar hukunci da zai ɗauka akan Jabeer ba. Ɗagowa da zai yi ya hango jack(ƙarfe da ake saka wa a kwance tayar mota) ciki booth da wani irin sauri ya dauƙo shi, Jabeer ya ri ga ya sa kai ko kaɗan bai yi tunani Tareeq zai iya ɗaukar mataki  marinsa a yanzu ba. Shiyasa tun da ya tunƙari ciki gida bai waiga bayansa ba. Tareeq yana zuwa ya sauke wa Jabeer ƙarfen a ƙeya, wata irin rikitacciyar ƙara Jabeer ya ƙwalla mai sauti gaske ya yi tangal-tangal kamar zai faɗi sai kuma ya tsaya da ƙafafunsa dafe da ƙeyarsa ya juya da nufi yaga wanda yai masa irin wannan ta'asa, a zuciye Tareeq ya sake buga masa ƙarfe daidai gefen fuskarsa zuwa abinda ya yi kanshi jinin Jabeer ya yi tsartuwa, tsanani azaba yasa shi faɗuwa ƙasa. Duk da haka Tareeq bar barshi ba ya jefar da ƙarfen gefe ɗaya, ya haye ruwan cikin Jabeer yana nushin sa a fuska duk da Jabeer ya shiga kare dukan da tafukan hannayensa sai dai hakan bai yi wani tasiri ba, a dalili jininsa dake zuba ya fara bugar dashi. Ihunsa da ya karaɗe gidan ya jawo hankali mutanen gidan ummi da tawagar ƴan matanta haɗe da malam musa direba suna rige-rige fitowa daga can gate kuma maigadi da securities suka rugu, kafin Ummi ta iso securities biyu ke kokari cire Tareeq daga jikin Jabeer daidai tana ƙaraso wa suka yi nasarar yakice shi daga kan Jabeer zuwa lokaci fuskar Jabeer ta rine da jini don har ya fara fita hayyacinshi a dalili jini da yake zubar wa bana wasa bane.

Ummi bata tsaya neman ba'asi ba ta ɗauke Tareeq da tagwayen maruka cikin tsanani fushi ta cukume wuyan jersey ɗinshi ta girgiza shi da dukkan ƙarfinta "Kashe ni ka ke so yi Tareeq ko? me miyasa kwata-kwata a rayuwarka ba ka da buri da ya wuce ka ganni cikin ɓacin rai? Na rantse da girman ALLAH idan wani mummunan abu ya sami Jabeer ba zan kyaleka ba. ka zame min fitina Tareeq kullum sai ɗanɗani baƙin ciki da ɓacin ranka miyasa ka fita daban a cikin ƴaƴan da na haifa? Wane kalar zunubi na aikata da Allah ya jarabce ni da haifar taƙadari yaro irinka?"

A fusace Tareeq ya fincike daga riƙe masa wuyan riga da Ummi tayi ya kalleta da wani irin fushi da zafin zuciya sai kuma ya yi ƙwafa ya juya da nufi yabar musu gida, da wani kalar fushi ummi ta sake riko wuyan rigarsa ta dawo dashi ta dinga dukansa da hannuwanta shi kuma yana tsaye kamar an dasa shi. Wani bugu da Ummi ta kai wa Tareeq sai ga hancinsa nan take noise bleeding ya goce masa Aayya da ke ɗakinta ta ji hayaniya tayi yawa ta fito, ta gane wa idonta me ke faruwa sai kawai ta ci karo da Tareeq tsaye Ummi tana dukansa gami da surfa mai zagi, da sauri Aayya ta zo ta shiga janye Tareeq ta rushe da kukan da babu hawaye tana faɗin "Innalillahi wa'inna illahim raji'um! Me nake shirin gani ni Hadizatu me yai miki ki ke masa wannan la'ananne duka shin ba magana nake miki ba Amina kashe shi ki ke so ki yi ko me??"

Sai lokaci Ummi ta sake shi ta koma gefe dafe da ƙirjinta ta shiga sauke numfashi bi da bi.

Securities ne suka kama Jabeer suka shigar dashi mota malam musa ya ja mota suka nufi asibiti da Jabeer Fadila da Zainab suka bi su a baya a tasu mota, Baby dake tsaye tana fama da

nononta dan har zuwa yanzu bai fasa mata zogi ba. Ta nufo wurin Ummi ta dafa ta tana mata sannu ta fahimci Asthma Ummi ke so tashi don yadda take fizgar numfashi nan ba na lafiya bane.

Sai da numfashi Ummi ya daidaita kana ta kalle side ɗin da Aayya take ta duƙar da kan Tareeq ƙasa jini dake fita a hancinshi yana diga kan interlock. A kufule ta ce "Nagaji, nagaji, Allah ya sani nagaji da ƙunsar bakin cikinka Tareeq fitinarka tayi yawa na tabbata baƙin cikinka ne zai kar ni...

Kasa ci-gaba da magana Ummi tayi a dalili barazanar da numfashinta ke mata "ki yi haƙuri Ummi ki daina magana kin ga yadda numfashinki ke sarƙewa alamar Asthma ki zai iya tashi.

Baby ta faɗa tare da kama damtse hannun ummi, da kyar ta cire ƙafarta da taimako Baby suna dab da isa entrance, Tareeq ya ɗago idanuwanshi sun canza colour a zuciye ya ce "Nima nagaji Ummi, nima nagaji da rashin ƙaunar da ki ke nuna min. Miyasa tun farko kinsan bakyasona ki ka haife ni? Miyasa lokaci da ki ka san kina ɗauke da cikina ba ki yi abortion ɗina ba?

Cakk! Ummi ta tsaya tare da waigowa ta kalli Tareeq da yai wani tsareta da idanuwansa yayin da jini ke zuba daga hancinsa da sauri Aayya ta kama hannunsa "Ya isa Tareeq zomuje na saka ma ƙanƙara ko habo (noise bleeding) ɗinan zai tsaya tsabar an tsane ka yau sai da aka tayar maka da masifaffen habo nan naka."

A fusace ya ture hannu Aayya "Ba inda za ni Aayya har sai Ummi ta faɗa min dalili wannan ƙiyayyar da take min hujjar da ake kafa min kwata-kwata ban gamsu da ita ba. Dalili nake so ji daga bakinta idan kuma ba ita ne ta haife ni ba ta faɗa min na daina kallonta a matsayin mahaifiyata."

Ya ƙarashe magana ciki fushi da fusata, cike da takaici Ummi ta girgiza kai ta juya tai tafiyarta.

Shi ma Tareeq juyawa ya yi ranshi yana mai tuƙuki ya nufi flat ɗin Hajiya Jamila.

Direct ummi ta haura upstairs bedroom ɗinta wanda ba kasafai take zama cikinsa ba ta fi so zama downstairs, ta maida ƙofar ɗaki ta rufe ta nemi gefen gado ta zauna har zuwa lokaci tana dafe da ƙirjinta da yai mata mugun nauyi. Ita kanta tana so sani miyasa take ji ƙiyayya ɗa da ta haifa da cikinta da ace tsanar da tai wa Imam Wali ce hujjar miyasa bata ji irin wannan yanayi akan Fadila da Baby suma ai jini imam Wali ne?"

Rashin sani amsar tambayarta yasa ta miƙewa ta ɗauki hijabinta da car key ta fice zuwa asibiti da Jabeer yake domin taga hali da yake ciki.

Aayya tana zuwa ɗakinta ta dauko wayarta ta dinga scrolling through contact ɗin da ke wayarta har ta kai da hoton Imam Wali dama hotonsa shine alamar da ke sa wa ta gane numbersa tun ba karatun boka tayi ba tai dialling number ta kara a kunnenta tana ji ya yi picking ta rushe da kuka "Subhanalillah! Aayya me ya faru ki ke kuka Dan Allah ki natsu ki yi min bayani abinda ya faru??

Imam Wali ya yi magana cike da son kwatar wa da Aayya hankali.

"Mene ne bai faru ba Imamu ga baki ɗaya gidan ka ya dawo tamkar sassani yaƙi na rasa irin wannan masifar? Kullum matsalolin gidanka ƙara habbaka suke kamar wutar kara anya Imamu ba ka sabawa Allah a ɓoye?

"Innalillahi wa'inna illahim raji'um! Haba Aayya Dan Allah ki dinga kyautata min zato. Allah shi ne shaidata ina ƙoƙarin ƙare hakkokin ubangiji."

"Dole tasani faɗar haka al'amarin gidanka ya ƙazanta matuƙa gaya, kullum Amina ciki dukan Tareeq take ga zagi da alkaba'i iri-irin tamkar batasan daga inda ya fito ba. Akan wannan shegen agolan ɗanta yau saura kaɗan ta kashe ma Tareeq ba ka ga yadda tai masa jina-jina ba. Shiyasa tun farko na nuna maka ban amince da zaman Jabeeru a gidanka ba amma da yake shegen taurin kai ne da kai ka kafe sai da ka haɗa shi da ƴaƴanka to gashi nan tana ƙoƙarin rabaka da magajinka."

Sosai ran Imam ya ɓaci yai shiru kawai yana sauraren maganganun Aayya. Can ya ja numfashi tare da sauke wa ƙoƙari danne ɓacin ransa yake yi kafin ya ce "Aayya In-shaa-Allah gobe ko jibi zan dawo zan magance matsalar amma kafin sannan ki rarrashi mutumin naki."

"Ai kuwa gara ka dawo kaima ai Imamu kana da naka laifi kullum kana gantali a hanya kamar wani marar mafadi ba dole gidanka ya rikice ba."

Murmushi kawai ya yi don yasan halin Aayya yanzu nan sai ta juye faɗa kansa. Shiyasa yai sauri yi mata sallama ya kashe wayarsa.

Tareeq a falon sama ya tarar da Hajiya Jamila tare da Ya Zahra wacce bata daɗe da zuwa gidan ba, kusan a tare suka miƙe tsaye kowanne su da kalar tashin hankali dake shimfiɗe akan fuskokinsu. Salati suka hau yi tun kafin ya ƙaraso Ya Zahra taje ta riƙo shi jikinta har wani kalar rawa yake ita ma Allah ya saka mata ƙaunar Tareeq duk gidan da ita kaɗai yake shiri don ko Ya Bilkisu basa shan inuwa ɗaya, saboda faɗan gyara kayanka da take masa. Shi kuma duk mutumin da zai faɗa masa gaskiya ba za mu shirya ba.

"Ya Allah! Wai har yanzu noise bleeding ɗinan bai bar ka ba Auta? zo ka zauna mommy kira sahura ta dauko min ice bag a fridge, sannu Auta hope babu headache?"

Dukka waɗannan maganganu kusan a tare Ya Zahra ta furta wa Tareeq.

Daga ita har mommy ba su sami natsuwa ba har sai da suka ga jini ya tsaya. Tareeq yana gani yadda mommy ta nuna zallan kulawarta akansa sai kawai ya ji wani irin rauni a zuciyarshi, bai san sanda ya kwata jikinta ya rungume ta, yana fadin "ina ma ace ke ce ki ka haife ni Mommy ba Ummi ba?"

#Jeeddah Aliyu

#Tareeq

#Zahra.

#Aayya

#Mommy

#Jabeer

#Imam Wali

WANNAN LITTAFI NA KUƊI NE KU BIYA 700 KACAL KU SHA KARATU CIKIN NATSUWA DA KWANCIYAR HANKALI ZA KU BIYA TA WANNAN ASUSUN BANKI

7032566172 HAUWA SHEHU OPAY

SHAIDAR BIYA TA WANNAN NUMBER 07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Hauwa Shehu Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

016.

Jin abunda ya faɗa yasaka mommy sakin murmushi gami da shafa tarin sumar kanshi "Ban taɓa kallonka ba a matsayin ɗa da na haifa ba Babana kaima ka ɗauke ni a matsayin mahaifiyarka ni da Amina ba mu da bambanci kuma ka yi haƙuri da duk abinda Amina take ma. Ba yi kanta bane ƙiyayya da take wa mahaifin ka ce ta shafe ka. Babu wata uwa a faɗin duniya ta za ta haife ɗa ta ce bata sanshi sai dai a bisa wani kwakwara dalili."

Girgiza kai Tareeq ya shiga yi "Mommy ki daina depending ummi I know she doesn't love me at all abubuwa da take min bai yi kama da na wacce ta haife ni ba."

"Babana sarkin rigima in na ƙara ji kace Ummi bata sanka sai na cire ma kunne."

Mommy tayi magana tana ɗan murɗe mai kunne.

"Ouuchhh! Mommy zafi.

Ya yi magana ciki shagwaɓaɓbiyar murya, mommy bari na je na canza kaya wannan duk ya ɓaci da jini su Roonie na jirana za mu tafi training kinsan next week muna da match."

Tareeq ya faɗa tare da barin jikin mommy.

"Allah ya tsare yasa ku yi nasara kuma Dan Allah Babana idan ka dawo daga training ɗin ka ba wa Ummi da Jabeer haƙuri nima zan shiga gunta na bata magana ka ji yaron kirki magajin Daddy."

Sosai fuskarshi ta cika da murmushi yana matuƙar jin daɗi ya ji an kira shi da magajin Daddy. Ba tare da ya amsa wa mommy zai ba da haƙuri ko ba zai bayar ba ya juya yana faɗin "Ina sonki sosai mommyna."

"Auta dan Allah idan ka fita banda tsokanar magana ka tsaya iya abinda ka je yi."

Ya Zahra ta faɗa ciki ɗaga murya.

"I love you Ya Zahra.

Ya faɗa daidai yana ƙarasa fita.

Mommy da Ya Zahra suka yi dariya.

"Wallahi mommy Ummi tana bani mamaki na rasa dalili da yasa take tsangwamar Tareeq idan don ƙiriniyarsa ce da zarar ya ƙara girma zai daina."

Taɓe baki Mommy tayi tare da ɗaukar remote ɗin Ac ta ƙara masa gudu, tana cewa "Miye abin mamaki Zahra tunda tun farko mahaifinku yasan bata sonshi ya kafe sai da ya aureta tsawon shekaru 23 kenan yana shanye baƙin cikinta. Akwai abin mamaki da ya wuce wannan. Amina bata da laifi ko kaɗan laifi na ubanku ne da ya nace mata."

Murmushi kawai Zahra tayi saboda ta hango zallar takaici da kishi a ƙwayar idon mommy gudun kada maganar tayi nisa sai ta sauya akalar firar tasu zuwa wani zance na daban.

Tareeq yana zuwa ɓangare shi ya yi wanka kana ya shirya cikin brown chino trouser haɗe da red t-shirt dukka daga kamfanin levi's ƙafarsa sanye da trainers shima red colour ya yi kyau na ban mamaki sai dai fuskarshi babu walwala a haka ya rufe ɓangare nashi ya fito. Yana fitowa ya haɗu da El-yaqub ya zo ya kawo mishi waya da Daddy ya ce aka kawo mai, wannan yasa ya saki fuska har walwala shi ta dawo, cike da zumudi yake kallon iphone ɗin da Daddy ya ce akawo masa. Ransa ya yi farin tass.

Horn aka yi maigadi ya buɗe gate kusan a tare motoci su Ummi suka shigo dawowarsu daga asibiti kenan Jabeer ya sha ɗinki a goshinsa da kuma ƙeyarsa kansa ya sha naɗi bandaging 🤕 da malalaci kallo ya bisu dashi da wani murmushi maƙale akan fuskarshi ya wani ɗage girar ido

Ummi tana ganinsa tare da El-yaqub ranta ya ƙara ɓaci saboda tasan waya ce ya kawo masa baya ta ce ba za a canza masa ba. Wannan kaɗai ya ƙara tabbatar mata da rashin muhimmancinta acikin rayuwar Tareeq tun da bata isa ta faɗa ya ji ba. A da yana shakkarta saɓani yanzu da duk abinda za ta faɗa sai da ya bi ta bayan kunnensa. A zuciye Ummi ta ɗaga ƙafarta da zimmar ta je ta hana El-yaqub ya bashi waya, Fadila ta riƙe mata hannu "Ummi please ki kyale shi dan Allah karki tanka masa ko kin yi magana ba dauka yake ba asalima sai dai ya ƙara miki ɓacin rai."

Ba haka Ummi taso ba duk da haka ta bi maganar Fadila. Jabeer ya kai dubansa gun da Tareeq yake still yana kallonsu kamar yaga kashi irin mai shege doyi nan, da sauri Jabeer ya kauda fuskarsa can ƙasan zuciyarsa yake ji tsanani tsanar Tareeq ya kasa yarda Tareeq ne yai masa mummunan rauni irin wannan ya fitar masa da jini mai yawa, yaro da aka haifa a tafin hannunsa This is a shame for him da wani kalar fushi ya nufi entrance Fadila ta bishi a baya kaitsaye corridor da zai kai shi da ɗakinshi ya nufa wanda ke kusa da na Tareeq. Shima Jabeer ba dai zuciya ba don har wani huci yake yi zuciyarsa tana toya ya zauna gefen gado Fadila ta zauna kusa dashi tare da kama hannunsa ta haɗe da nata "ka yi haƙuri Ya jay you're mature enough to know that anger won't solve anything sai ma ya ƙara rura wani wuta na daban. we are all brothers and sisters, we should not fight among ourselves mu dinga haƙuri da Tareeq ruɗin kuruciya ke damun shi da kuma gata da Daddy yake nuna masa, a matsayinka na babba kuma namiji kaine ya dace ka ja shi a jikinka ka dinga lurar dashi ina ji a jikina wata rana Tareeq zai gyaru za mu yi alfahari dashi."

Har Fadila ta dasa aya a zancenta Jabeer bai furta uffan ba duk abubuwan da take faɗa ba wanda ya shige sa balle ya yi tunani amfani dasu, ba abinda zuciyarsa take so da muradi irin yai ma Tareeq rauni da yafi wanda yai masa, baya ji da akwai wata kalma a duniya nan da za ta saukar mishi da haushin Tareeq da yake ji, don haka sai ya miƙe yana faɗin "Feedy bari nayi wanka kafin na fito ki kawo min abinci."

Fadila ta tashi tare da ficewa ita kanta haushin Tareeq take ji abubuwan da yake yi sun yi yawa kuma ba wanda ya isa ya faɗa ya ji kowa kallo bai isa ba yake masa.

Tareeq ya karɓi wayarshi gami da nufar ɗaya daga cikin motoci Daddy ya hau wacce ransa ke so ya fice gantali abinsa, kasancewar ranshi a dagule yake shiyasa ya fasa fita ball mestry training ɗin. Sai dab da magariba ya dawo yau Allah ya taimaka bai fita gantalinsa na dare ba.

Washegari.

Da wuri Tareeq ya yi shirin tafiya school saboda yau suna da test ɗin Chemistry kuma teacher da yake ɗaukar su Chemistry mugu ne na ƙarshe lissafi. Tun jiya rabonsa da shiga flat ɗin Ummi shiyasa yanzu da ya hango ta tsaye riƙe da hannu Gifty kallo ɗaya yai mata ya kauda fuska, hannayensa zube ciki aljihun wando uniform ɗinshi sai kawai ya canza hanya baya so duk wani abu da zai sake haɗa shi da Ummi.

Ummi taga lokaci da ya canza hanya hakan ba ƙaramin ciwo yai mata ba saboda haka ranta a

ɓace ta ƙwalla mai kira "Kai Tareeq zo nan!

Ta ƙarashe magana gami da ya fito shi da hannunta, jim ya yi kamar ba zai je ba sai da ya gama harare-hararenshi yana cuno baki gami da gunguni kafin ya je yai tsaye nesa kaɗan da ita ya sadda kanshi ƙasa.

"Yanzu Tareeq har ka yi girman da za ka yi gaba dani anya kuwa kasan hakkin uwa kasan kuwa abinda kalma uwa take nufi?"

Shiru ya yi bashi da alama amsa mata sai kawai Ummi ta girgiza kai ta ce "Je ka Allah ya shirye ka ya ganar da kai."

Nan ma bai tanka ba ya juya abinsa daidai direbanshi yana ƙarasowa ya buɗe masa murfin mota ya shiga har suka fice daga gidan bai sake ko kallo side ɗin da Ummi take ba.

Wasu zafafan hawaye Ummi ta ji suna bin kumatunta, a haka direbanta Malam Iliya ya zo ya same ta da sauri tasa gefen hijab ɗinta ta goge fuskarta. Malam Iliya ya karɓi lunch pack ɗin Gifty ya wuce da ita parking lot, Ummi kuma ta juya ciki gida.

Ɗakin Baby ta wuce ta duba ta kwance ta tarar da ita tana bacci dan haka ta fito ta shiga na Fadila ita kuma tana tsaye gaban dressing mirror da perfume bottle a hannunta.

"Ina kwana Ummi.

"Lafiya ƙalau Fadila kin tashi lafiya?

"Al-hamdullilah Ummi.

"ma-shaa-Allah! Halan yau lectures ɗin safe ki ke da?

"A'ah sai eleven o'clock kawai dai akwai assignment ɗin da zan yi submitting lecturer ya ce kowa ya yi submitting assignment ɗin da kanshi kuma idan 9:00am ya yi ba zai karɓa ba. Gashi assingnment ɗin shi ne matsayin test Shiyasa na shirya da wuri bana so na rasa C/A ɗinshi saboda yana da matsala."

Fadila ta ƙarashe magana tare da mayar da perfume bottle ɗin inda ta dauko Ummi tayi murmushi tare da faɗin "koma mene ne ki tabbata ki yi breakfast kafin ki fita."

"Tohm Ummi!

Daga haka Ummi ta fice bata koma ɗakinta ba sai ta bi ta corridor da zai kai ta ɗakin Jabeer, tana shiga yana fitowa daga wanka ƙungusa ɗaure da brown towel.

"Ya jikin naka?

Ummu ta faɗa with love and care.

A maimakon jabeer ya amsa sai kawai ya ɗan runsuna cike da girmamawa ya gaidata, ta amsa

masa da yalwattace murmushi akan fuskarta.

"Idan ka shirya ka fito ka yi breakfast.

Ummi tayi magana gami da juyawa ta fice. Jabeer ya bi ta da kallo yana jin tsanani ƙaunarta, domin Ummi mace ce da bata wasa da duk wani abu da ya shafi iyalinta.

Yau tun misali 7:15am Nana ta zo school a ƴan kwanaki nan ta rasa gane kanta bata da aiki da ya wuce tunani abun da Tareeq yai mata tana ji kamar tana kewar shi, ita kanta tasan tarayyar ta dashi ba abu mai yiwuwa bane amma ta kasa yarda da hakan. Tun sanda ta zo school take zaune a gefen baranda class ɗinsu ta jingina bayanta da pillar hannuwanta rungume da backpack ɗinta dake kan cinyoyinta. Lokaci da ta hango motar gidansu Tareeq sai da tai wani kalar sauke dogon numfashi, har direban ya yi parking ya fito ya buɗe wa Tareeq ƙofa bata iya ɗauke idanuwanta ba, tana gani Tareeq ya fito jikinta ya yi wani irin tsammmm!" Tsigar jikinta ya mimmiƙe,cikin tafiyarshi ta ƙasaita ya nufi hanya da za ta sada shi da class ɗinsu, tun da ya tunkaro class ya ga yadda Nana ke mishi mayatatcen kallo kamar, za ta cinye shi, mugun kallo da yai mata yasa tai sauri ɗauke idanuwanta daga kanshi ba wai don ta gaji da kallo nasa ba. Ya wuce ta ya haura stairs ɗin da za kai shi class. Nana ta sauke ajiyar zuciya bayan ta dawo daga bin sa da kallo, jikinta a mace ta ɗauki backpack ɗinta ta rataya a shoulder ta. Tareeq yana zama a seat ɗinshi tana shigowa kanta tsaye ta nufo wurinsa "Good morning slugger!

ta faɗa da ɗan tsoro akan fuskarta.

A zuciye ya taso mata tamkar zai kifa mata mari "me matsalar ki dani? Na ga mamanki ta ce na fita sabgar ki na kuma fita to akan me za ki nemi ki dinga taƙura min? Ba a min haka you better stay away from me Nana."

Ya ƙarashe magana yana wani furzar da iska mai zafi daga bakinshi.

Dukkan jikin Nana ya ɗau rawa Allah ya yi ta da wani irin mugun tsoro, ga ta kuma da saurin kuka, tsanani takaicinta yasa Tareeq ya bar mata class dama su biyu ne kaɗai a ciki raguwar students suna wurin assembly.

A natse Jabeer ya gama shirin sa ciki white colour three quarter haɗe da green armless shirt, yana kama da Tareeq sosai da yake dukkan su biyu suna ɗibar kama da Ummi. A dining room ya tarar da Baby da Aayya suna ci abinci kowanne fuskarsa a murtuƙe ya ja kujerar da ke kusa da Aayya ya zauna tare da faɗin"ina kwana Aayya?"

"Yana bisa gado ka je ɗakina za ka ganshi."

"Uhm! Aayya kenan daga gaisuwa sai ki sakar min baƙa."

"Ba dole na sakar ma baka ba jiya daga dawowarka ka haddasa fitina a gidanan na tabbata kaine ka fara tsokanar Tareeq domin kowa ya shaide shi a gidanan duk ƙiriniyarsa baya shiga sabgar mutum idan ba a shiga tasa ba. Don haka Jabeeru ka ji tsoron Allah ka daina haddasa

fitina domin Allah da kansa ya la'anci mai tadda fitina."

"Wannan kuma Aayya kanki za ki gayawa domin nima kowa ya shedeni zuciyata cike take da tsaron Allah."

Jabeer ya faɗa tare da tsare Aayya da fusatattun idanuwanshi saboda maganarta, ba ƙaramin fusata shi tayi ba.

"Dan Allah Ya jay daina kula wannan tsohuwar mai mugun so zuciya yanzu nan sai tai spoile mood ɗinka."

Baby ta faɗa ta zari plate ta yiwa Jabeer serving.

"La'illaha illallahu muhammadu Rasulullah Sallallahu alaihi Wasallam!

Baby da Jabeer suka haɗa baki suka taya Aayya ƙarasa kalmar shahada da take yi tana tafa hannuwa.

"Za ka aikata fiye da haka Jabeeru ai tun da Amina ce ta haife ka ɗibar albarka fiye da wannan za ka iya."

Kafin Jabeer ya mayar wa da Aayya magana suka ji tsikayi muryar Ummi a bayansu ta nufo cikin dining room ɗin "Ni kam har sai yaushe Aayya za ki fara faɗar alkhairi akaina?"

"Har sai ranar da ki ka daina nuna wa Tareeq tsana da tsangwama."

"Wallahi Aayya muguwar ƴar son zuciya ce ke ban da tsabage so zuciya shi Tareeq ba ki ga irin rashin Kunyar da yake wa Ummi ba? Babu wata girmamawa da yake mata a matsayinta na mahaifiyarshi."

"Ya isa Jabeer ko kaɗan bana ji daɗi yadda ku ke mayar wa da Aayya magana, ita ɗin mahaifiyata ce dole ku girmama ta tamkar yadda ku ke girmama ni zance Tareeq kuma bana so ka ci abincin ka kawai."

Rai ɓace Aayya ta tashi cikin bala'i da masifa da ya gama zama mata jiki don har wani ƙanƙance idanuwa take yi "Ni ba mahaifiyarki bace Amina sai dai uwar goyonki da kin ɗauke ni a matsayin mahaifiya da ba ki tsane jinina har haka ba. Da ba ki zurfafa ƙiyayyar da ki ke wa Imamu ba har ta kai ga shafar gudan jininsa, don haka ki daina kirana da mahaifiyarki."

Kafin Ummi ta yi magana Aayya ta wuce fuuu cikin ɗakinta ta bugu ƙofa da ƙarfi, jikin Ummi yai bala'in sanyi ta ji wani irin abu mai nauyin gaske ya tokare mata kirji. Kanta yai bala'in sarawa breakfast ɗin ba tayi ba kenan ta koma ɗaki ta kwanta ranta na mata soya.

#Jeeddah Aliyu

#Tareeq

#Nana

#ummi

#Aayya

#Jabeer

WANNAN LITTAFI NA KUƊI NE KU BIYA 700 KACAL KU SHA KARATU CIKIN NATSUWA DA KWANCIYAR HANKALI ZA KU BIYA TA WANNAN ASUSUN BANKI

7032566172 HAUWA SHEHU OPAY

SHAIDAR BIYA TA WANNAN NUMBER 07032566172.

[7/6, 7:24 AM] Hauwa Shehu Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

017.

Yadda Ummi ta taƙure jikinta wuri ɗaya tun anan za ka fahimci kwanciyar bana jin daɗi tayi ba. Damuwa ce tai mata yawa a duk lokaci da taso ta tsananta tunani haɗe da lallaɓo mafita dalili da yasa take ji tsanar Alhaji Imam Wali da ɗanta Tareeq sai ta ji kanta ya dau zafi. Wani irin jiri ya dinga ɗibar ta kaman zai yada ta. Duk wanda ya kalli Ummi zai ga rashin natsuwar zuci a tare da ita kullum cikin ƙunci take duk da tana ƙoƙari ɓoye hakan wa yaranta, saboda bata so damuwarta ya shafe walwalarsu.

Haka jiya da dare mommy ta shigo flat ɗinta ta gayamata son ranta sai abunda bakinta ya manta, duk akan Tareeq ta rasa miyasa tsakani Aayya, Alhaji Imam Wali da mommy duk wanda ya tashi buɗe bakinsa sai ce bata ƙaunar Tareeq? Wannan kalmar yana hurting ɗinta amma batasan me yasa ba za ta iya ƙaryata furuncin su ba. A wasu lokuta ji take kamar ƙwaƙwalwarta zai buga.

Tareeq yana fitowa daga class ya ci karo da Roofy Sodangi ta sakar masa murmushi tana hango Nana a bayanshi wacce yana nufar ƙofar fita ta biyo shi nan take murmushin kan fuskarta ya washe, a fusace ta gallawa Nana harara tare da shan gabanta tana faɗin "hey!why are you following my boyfriend?"

Da mamaki Tareeq ya kalli Roofy sai kuma ya taɓe baki ya sauka ƙasa kallo sama da ƙasa Nana take wa Roofy kafin tayi murmushi "your boyfriend??

"Yes! Do you have problem with that?

Roofy ta faɗa tana tsare gida ya mutsa fuska Nana tayi tare da faɗin

I don't think Tareeq is your boyfriend because you're not suitable with him."

Nana tayi magana tare da ture ta ta wuce da gudu Roofy ta bi ta tana faɗin "Nana Bashir  I'm not done talking to you get back here and tell me who is suitable for him?"

Nana ita ma ta juya a fusace daidai tana sauka ƙasa Roofy ita ma tana kawowa second to the last stairs rai ɓace suke kallon juna kowacce zuciyata ta zo wuya Roofy ta ce

"Ina fatan ba ƙoƙari ki ke ki ce ke ce ki ka dace dashi ba?"

"Ki je ki tambaye shi mana amsar ai tana bakinshi."

Zuwa Rooney ne ya shiga tsakaninsu domin har abin yana so ya zama musu dambe.

*LATE ALHAJI ABDALLAH SARAKI MANSION*

Wata mota ce kirar Mercedes C300 4Matic ta nufi katafaren gate ɗin gidan da ƙarfi mamallaki mota ke danna horn maigadi ya rugu ya buɗe masa gate sai da ya isa daidai entrance ɗin gidan ya yi parking bai ma gama daidaita parking ɗin motar da kyau ba. Saboda yadda tayoyin motar suka juye kowacce ta kalli gun da take so.

ya ɓalle murfin mota ya fito jikinsa sanye da shadda royal blue in color

cikin zafin nama irin na wanda ke cike da koshin lafiya yake, taka ƙasa tafiyarsa kaɗai ya isa ya faɗarwa da ƙaramin jarumi gaba. Fuskarshi na ɗauke da wani irin kwarjini da cikar haiba.

Kaitsaye ya haura bene zuwa ɗakin shalelen ƴarsa wacce ita ce silar da ya baro wurin aikinshi ba shiri yana tura ƙofar ɗakin nata da aka ƙawata shi da deco komai na ɗakin white and baby pink color ya hango ta kwance akan cinyoyin ummarsa tana bacci abinta sai da ya saki ƙarfaffiyar ajiyar zuciya kafin ya maida ƙofa ya rufe, da wani kalar sauri ya isa wajenta. Hannunta da ke lulluɓe da pop ya fara yada ganinsa akai.

"Allah ya shirye ka Mahmoud ya rage maka wannan masifar son ƴaƴa kalli yadda ka shigo min ba ko sallama kamar wanda aka jefo daga sama. Maza koma ka yi sallama sannan ka shigo."

Hajiya Salma ta faɗa tana mai maka mai harara.

Ba yadda ya iya dole ya koma ya sake buɗe ƙofar tare da sallama. Sannan fa

Umma ta amsa tana ƙara jefa masa harara.

Sai da ya zauna kusa da Taheerah kana ya ɗora hannunsa akan ƙanana kalabar twisting dake kanta yana shafa wa a hankali. Taheerah yarinya ce sosai wacce shekarunta na haihuwa ba za su wuce 8yrs ba fatar jikinta chocolate color ce kamar ta Mahmoud.

"Umma gari ya ta ji mummuna rauni irin wannan?"

"Ba ka ji abinda na faɗa maka a waya bane?"

"Ni fa umma abu ɗaya na ji kin faɗa Baby heerah ta karye a hannu iya abun da na ji kenan."

"Ai kuwa ba yadda za a ka ji tun da ka riga ka zama magge uban so ƴaƴa, to lilo ta hau a school garin ƙiriniyarta ta faɗo, shine fa ta sami karaya a hannu.

Sai kawai ya shiga surfa faɗa wai laifi school ɗin ne basa ba wa yara kula da kyau ba dole su faɗo ba, dnn haka cire ta zai yi ya sauya mata school.

Ko kaɗan Umma bata yi mamaki furuncinsa ba haka ta dinga fama dashi akan Aabid kafin ya kammala primary school ya sauya mishi makaranta yafi goma, shi ba wanda ya isa ya dakar mai ƴaƴa wani irin mahaukacin so yake gwada musu. Tun lokaci da mahaifiyarsu Layla ta rasu ta hanyar hatsarin mota akan hanyar ta na zuwa bikin ƙanwarta daga Kano zuwa Katsina, a lokaci tana shayar da Taheerah cikin hukunci Ubangiji da ƙudirarsa Taheerah ko kwarzane bata yi ba dama shi Aabid yana zuwa school ta barshi a wurin Umma, tun anan wuri ita da direba da ya ɗauko ta suka rasu. Shekara bakwai da rasuwarta ko zance aure Mahmoud bai so ayi masa.

Shiyasa yaransa ke hannun mahaifiyarsa.

Aabid shi ke da 15 yrs a halin yanzu yana SS2 a secondary school sai ita Taheerah me 8yrs tana primary 2.

Mahaifin Mahmoud Alhaji Abdallah Saraki ya rasu kusan shekaru 15 da suka gabata. Alhaji Abdallah Saraki ɗan kasuwa ne yana da rufin asiri daidai gwargwado matarsa ta aure guda ɗaya ita ce Hajiya Salma ta haifa masa ƴaƴa uku Nafisa ita ce babba tayi aure a garin Zaria ta haifi ƴaƴa bakwai sai Mahmoud sai kuma Sameer shi ma ya yi aure da yaransa uku. Mahmoud yana aiki a NNPC(Nigerian National Petroleum Commission) rashen Kaduna.

Tun bayan rasuwar mahaifinsu Sameer ke kula da kasuwancin da mahaifinsa ya bari suna da shaguna har guda biyar a kasuwar kwari suna siyar da atamfofi, laces, shadda da dai sauransu yanzu haka sun bude wani rashe a Kaduna da Abuja.

Yini ranar sallah ce kaɗai ke fitar da Mahmoud Saraki daga ɗakin Taheerah.

***************

Gaba ɗaya class ɗin ya yi tsit kowanne dalibi kanshi na duke yana rubuta iya abinda ya sani tun lokaci da Tareeq ya fara rubutu yake ji kamar ana kallonshi ya ciro kai ya dube gun da yake tunani mai kallon nasa yake, kamar dai yadda ya zargi ita ce mai kallon nashi zarginsa kuwa ya tabbata ga baki ɗaya hankali da idanuwanta suna kanshi. Bata rubuta uwar kome akan answer sheet ɗinta ba, biro ɗinta ma a bakinta yake tana taunarsa a hankali. Da alama bata ma san me take yi ba.

"Nana Bashir!

Tareeq ya furta can ƙasan maƙoshinsa tare da girgiza kai ya ci-gaba da rubutunshi duk ya bi ya tsargu da irin  mayatatcen kallo da take mai.

Tareeq ya tsinci kanshi da rubuta wa Nana test da yake Allah ya bashi fasaha da baiwar iya different handwriting.

"Get ready to submit.

Teacher ɗin ya faɗa idan Allah ya taimake Tareeq sai aka kira teacher ɗin a waya sai ya umarci ɗaya daga cikin student da ke zaune a front seat ya ce ta karba mishi answer sheet ɗin shi kuma ya fita waje yana waya. Hakan yasa Tareeq ya taso daga wurin zamansa da test ɗin da ya yiwa Nana ba tare da ya yi mata magana ba ya ajiye takardar akan desk ɗinta ya juya da sauri ya koma seat ɗinshi.

Da wani irin shock Nana ta bishi da kallo kafin ta dawo da ganinta kan takardar ta bi kyakkyawan handwriting ɗinsa da ido hatta da number ɗinta ya rubuta saboda suna amfani da number ne maimakon suna, duk abinda ke faruwa a tsakaninsu akan idon Roofy Sodangi hakan yasa ta cika tayi fan. Sai during breakfast period ta sami damar amayar da abinda ke ranta. As usual suna zaune gun da suka saba zama Roofy ta kalli Tareeq da fushi akan fuskarta "slugger me ka aikata ɗazu a class?"

Ba tare da ya kalleta ba ya ce "me kenan?"

"Please slugger stop pretending like  ba kasan me nake nufi ba kawai ka bani amsar tambayana ka cire min ƙwaƙwato da ke raina akanku kai da ita."

"Ki daina yi min ihu aka banaso."

"Ba zan daina ba har sai ka bani amsar tambayana Tareeq Imam Wali for how long muke tare da kai duk cikinmu ba wanda ka taɓa rubuta wa test sai wannan mummuna yarinya Nana Bashir, ka faɗa min wacce alaƙa ka ke yunkuri kulawa da ita after all abinda tai maka but you're still care about her?"

Wani kalar kallo ya watsa mata ta fara hasala shi "Wai me damuwar ki ne Roofy?

"I'm just protecting what's is mine, any problem with that??"

Da mamaki shimfiɗe akan fuskarshi ya ke kallonta kafin ya ja guntun tsaki gami da faɗin " I don't understand, what is yours?"

"You Tareeq kai ɗin nawa ne ni kaɗai i can't sharing you with any girl in this school is better to stay away from her ko wallahi-tallahi ka jawo mata masifa da bala'i don ba zan zuba ido ina kallo wata kucakar yarinya ta zo ta raba ni da kai ba."

"You're mentally ill it's obvious you didn't take your medications today, you should go back home and to do that before you run into street."

Tareeq  ya faɗa yana mata wani irin kallo yana dasa aya Ronnie da Lil-prince suka sheƙe da dariyar ƙeta hakan ya ƙara linkawa Roofy Sodangi takaici a fusace ta ɗauki backpack ɗinta. Ta wuce zuwa class zuciyarta tana mata ƙuna. Nana Bashir dake tsaye nesa dasu duk abinda ke faruwa akan idanuwanta duk da bata ji me suke faɗa amma jikinta ya bata suna magana ne akan ta. Sai kawai ta saki shu'umin murmushi ta nufi wurin Tareeq tun kafin ta ƙaraso Lil-prince yasa kafaɗarsa ya zuguri kafaɗar Tareeq gami da faɗin "Slugger ga fa new crush

ɗinka nan tafe ita ce mace ta farko da ta taɓa ture gwamnatin Roofy ɗin mu."

Guntun tsaki Tareeq ya ja tare da gallawa Lil-prince baƙar harara Lil da Ronnie suka sheƙe da dariya daidai Nana Bashir tana ƙaraso wa.

"Sannun ku BBT (Bad boys team)

Nana ta faɗa sa'ili da ta iso gaf dasu Ronnie ne ya fara haɗiye dariyarshi ya amsa mata cikin ƙaryar da murya Nana Bashir ta kalli Tareeq tana murmushi ta sake cewa "Please Tareeq two minutes zan yi magana da kai."

"Kina bini bashi ne?"

Tareeq ya faɗa ba tare da ya kalli gun da take tsaye ba.

"At least let me say the words."

Nana ta faɗa tana sake karya murya.

"Uhm!

Tareeq ya faɗa yana ya mutsa fuska.

"Thank you so much for the test you did to me thank so very much for helping me out."

"Keep your thanks I don't need it. because nayi ra'ayi ne ban kuma yi don ki gode min ba you can leave."

"Uhm.slugger..

"Please Nana just go.

Yadda Nana Bashir taga Tareeq ya katse ta a fusace sai kawai ta juya can kasan zuciyarta take ji wani irin farin ciki marar misaltuwa.

Bayan an tashi daga school Tareeq and his teammates suna zaune a gun da suke zama kafin a zo ɗaukar su, ya hango Gifty wacce fitowarsu daga lesson kenan "Ke red hair zo nan."

ya yi magana tare da ya fito ta da hannu, Gifty  ta ɓata rai saboda ya kirata da suna da bata so tayi tsaye tana kallon gun da Tareeq yake zaune nan take idanuwanta suka yi rau-rau kamar za ta sa kuka ta ƙi jini ta ji Tareeq ya kira ta da wannan suna.

"Gifty zo nace don ubanki in ki ka bari na taho wurinki da kaina sai na kifa miki mari."

Tareeq ya sake faɗa, Ronnie ya ce "Please slugger ka kyale min matana bana ji daɗin yadda ka ke hantararta."

"Mtss! Uban matarka idan ka kure min maneji zan haɗe kai da ita naci ƙaniyarku."

"Allah ya ba ka haƙuri my in law amma dan Allah karka sa min ita kuka wallahi ina mugun san Gifty."

Kafin Tareeq ya bashi amsa Gifty ta ƙaraso cikin ƴar muryarta na yara ƙanana ta ce "Gani Ya Tashh."

Haka take kiranshi dashi, kuma ita kadai ke kiran shi da sunan bai kuma taɓa ki amsa mata ba.

Sai da Tareeq ya maka mata harara mugun haushinta yake ji a dalili ita ɗin diyar umminshi ce.

"Ya sunanki?"

Duk da Gifty yarinya ce ƙarama amma tana da wayau sosai tuni ta fahimci tambayar reni wayau ce Tareeq yake mata.

"Suna na Tahreem Imam Wali.

"A gidan uban wa Imam Wali ya zama Babanki?

Shiru Gifty tayi don batasan me za ta ce dashi ba.

"Idan kin je gida ki faɗawa ummi na ce daga yau karki sake yi min amfani da sunan ubana tun da ke ma ai kina da uba ba shegiya bace ke, ko ke shegiya ce?"

Ya tambaya yana kallonta ta girgiza kai "good girl wuce ki je ga direbanki can ya zo karki manta da saƙona ki gayawa ummi, na ma san ba za ki manta ba tun da ke talktive ce.

Gifty da ta juya ta nufi wurin malam Iliya direba da ke jiranta.

Ronnie da Lil-prince suka sa dariya yayin da Lil ke cewa "Gaskiya slugger ba ka da mutumci hatta da umminmu ba ka bari ba, to a duniya nan wa za ka ragawa?"

Ya ƙarashe magana tare da ɗora yatsansa a haɓarsa alamar tunani.

Kafin Tareeq ya bashi amsa Roofy Sodangi ta taso daga wurin zamanta ta taho wurinsu da har tayi fushi ta ware kanta daban a cikinsu, fahimtar tayi dukka team din rashin ji nasu halinsu ɗaya ba za su taɓa rarrashinta ba balle su bata haƙuri, sani halin su yasa ta rarrashi kanta. Yau motar Tareeq su Ronnie suka biyo shi sai da malam musa ya sauke kowanne su kofar gidansu kafin ya sauke Tareeq sani ya yi Ummi tana dakonsa shiyasa bai bi ta cikin main parlor ba.

Gifty tana dawowa gida ko uniform bata cire ba ta wuce ɗakin Ummi ta faɗa mata saƙon Tareeq, shiru Ummi tayi zuciyarta na mata wani irin raɗaɗi, sai kawai ta ce da Gifty ta je ta cire uniform tayi wanka ta zo taci abinci. Gifty bata daɗe da fita ba Baby ta shigo wacce har yanzu nononta yana mata zafi ta ce "Ummi Daddy ya dawo yanzu nan."

Kamar saukar aradu haka Ummi ta ji saukar albishir ɗin da Baby tai mata ko kaɗan bataso a ambata mata koda sunan mijin nata ne balle tayi arba dashi yanzu farin cikinta yana juye wa zuwa baƙin ciki.

Alhaji Imam Wali yana fitowa daga mota direct flat ɗin Ummi ya nufo duk da ba ita ke dashi ba part ɗin Hajiya Jamila ya dace ya sauka, amma tsabar fitina da yake ji akan Ummi yasa shi ya nufo ɓangaren ta. Tun jiya da Aayya ta kira shi a waya ta faɗa masa  irin duka da Ummi tayi wa Tareeq yake ji kansa ciki ɓacin rai, a yadda yake ji ransa yana masa ƙuna komai zai iya faruwa a yau ɗinan idan ya ce komai yana nufi har rabuwa da Ummi zai iya domin ta ri ga ta kai shi maƙura ya gaji da munana halaye ta. Zai iya haƙuri idan shi take wa amma ko kaɗan haƙurinsa baya tasiri akan kowa idan aka taɓa masa shalelen ɗansa.

Duk gaisuwar da housemaid ke mai ba wanda ya amsa yana shigowa main parlor ya nufi upstairs daidai staircase ya tsaya ya shiga kwallawa Ummi kira "Amina! Amina! Ke Amina kina ina maza sauko ki faɗa min dalili da yasa ke da ɗanki ku ka dakar min yaro??"

Ummi ta kalli Baby wacce tun sanda tai mata albishir ɗin dawowar Daddy nasu bata baro ɗakin ba. Saboda haka Ummi ta kalli Baby, Baby ta kalleta yayin da idanuwan Baby suka bayyanar da tsoronta a fili tasan yadda iyayen nasu ke musanya yawu a tsakaninsu abin ba kyau gani balle saurare batasan sai yaushe iyayensu za su daina faɗa a tsakaninsu ba? Batasan har sai zuwa yaushe gidansu zai zama gidan farin ciki da walwala ba? Tun sanda ta fara girma hankali ya fara zuwa mata take gani iyayenta a halin rashin jituwa har kawo yau ɗinan da ta balaga tasan me zaman aure yake nufi bata canza zani a tsakaninsu ba.

Kafin Baby ta gama tunani Ummi ta sakko daga gado a fusace ta nufi ƙofar fita, da sauri Baby ta biyo ta a baya tana faɗin "Dan girman Allah Ummi karki fita ki biye wa Daddy ki fita batun sa kawai idan ya gaji da masifarsa yai tafiyarsa, Ummi please ki yi min wannan alfarma wallahi banaso ina ganinku kuna faɗa da junanku."

Duk magiya da Baby take yiwa Ummi bai sa ta fasa tunkarar wurin Daddy ba.

Daddy yana hango ta bai jira ta ƙarasa saukowa ba ya soma zuba ruwan tijara "Akan me za ki mayar min da yaro kamar wani jaki duka ma ya tashi daga gareki ke kaɗai hadda gami da yaranki to wallahi wannan ya zama na farko kuma na ƙarshe da Jabeer zai sake ɗora hannunshi akan Tareeq. Zan iya jure duk wani wulaƙancinki Amina kuma na shanye sa amma bani da haƙuri ko miskala-zarrati idan aka taɓa Tareeq."

"Tabbas yau na ƙara fahimtar son zuciyarka Imam Wali shi Tareeq yafi kowanne ɗa zane ne, da idan ya yi laifi ba za a hukunta shi ba ko kuwa shi kaɗai aka haifa sauran yara da yake duka su sassako su aka yi ko me??

Ummi ta faɗa ciki ɗaga murya da fusata.

"Wannan kuma matsalar ki ce Amina duk ɗa da ki ka ga Tareeq ya daka gonarsa ya shiga, ai ba mahaukaci bane shi da zai dinga duka mutane haka siddam. Don haka ki kiyaye ni ba zan lamunci wannan mugun hali naki akan yarona ba, ni nai miki laifi da na aure ki ba tare da kina sona ba, saboda haka ƙiyayyarki ta kare kaina. Idan har kike sake ɗora hannunki akan Tareeq wallahi sai nayi mugun ba ki mamaki."

"Muddin ba ka hana masa duka yarana ba nima ba zan fasa dukan nasa ba. Yaro ya bi ya lalace ba a tsawata masa tarbiyyar sa gaba ɗaya ta gurɓace."

Aayya dake ɗakinta ta ji haniya ta kaure a gidan nasu ta fito tana ta-ta kasancewar ƙafafuwanta sun fara gazawa.

Tun kafin ta ƙaraso ta shiga faɗin "Kaiconki Amina ke kam ki yi asara ina mamaki ke ɗin tarbiyya ta ce, da ana dawowa duniya daga lahira na tabbata da Fatima ta dawo ko don tayi Allah ya wadai da halinki. Duk faɗin duniya nan da take ciki da jinsin maza da mata ki rasa makiya da za ki zabawa Kanki sai mijinki da ɗanki na cikinki. Wannan mugun hali ko a tarihin jahilan farko ba a taɓa yi irinsa ba."

Wannan furuncin na Aayya yasa ka idanuwan Ummi cicciko da hawaye sai kawai ta juya saboda bata so Imam Wali yaga zubar hawayenta ya zaci cewa yaci galaba akanta.

Imam Wali shi da Aayya haka sun ɗauki lokaci a tsaye suna faɗar maganganu marasa daɗi akan Ummi kafin ya fice zuwa ɗakin shalelen nasa, tun kafin ya buɗe ƙofa yake ji wani irin loud music yana tashi Daddy ya saki ƙayatattace murmushi gami da girgiza kai.

#Jeeddah Aliyu

#Tareeq

#Gifty

#Nana

#Roofysodangi

#ImamWali

#Ummi.

REMAIN TWO-THREE FREE PAGES  SU KARE GA MAI SHA'AWAR CIGABAN WANNAN LITTAFI ZA KU BIYA ₦700 TA WANNAN ASUSUN BANKI 7032566172 HAUWA SHEHU OPAY SHAIDAR BIYA TA WANNAN LAMBA 7032566172.

[7/6, 7:24 AM] Hauwa Shehu Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

018.

Daddy ya murɗa handle ya shiga Tareeq baya ciki parlor ɗin sai da Daddy ya rage volume kafin ya wuce ɗakinshi daidai yana fitowa daga wanka a maimakon ya ɗaura towel sai kawai yai amfani dashi yana goge sumar kanshi. Dama wannan yana ɗaya daga cikin ɗabi'unsa bai wani damu da suturta tsiraicin shi ba. Gaba gadi ya fito abinsa yana ji an turo ƙofa yai sauri kallan kofar ya gani Daddynshi ne ya buga wani uban ihu gami da jefar da towel ɗin hannunshi a naked ya nufi Daddy ya rungume shi da kyar Daddy ya ciro shi daga cikin babbar rigarsa, da ya cukuikuye shi.

"Haba my heir har sai yaushe za ka daina irin wannan sakalci huh?" Ya kamata kasan ka girma ka wuce wannan shirme."

Cikin turo baki Tareeq ya ce "me nayi Daddy?"

"Kalli yadda ka fito a tunanina ka yi girman da za ka daina fitowa daga wanka haka."

Daddy ya yi magana tare da nufar gun da Tareeq ya jefar da towel ɗin ya duƙa ya dauko masa kana ya jefa masa Tareeq ya cabe towel ɗin Daddy ya ce "Maza ka suturta jikinka kar na sake gani ka fito a haka. Ka saka kayanka ka zo part ɗina ina jiranka za mu yi magana."

Dariya Tareeq ya yi tare da faɗin "tohm Daddyna."

Yau kusan two days da dawowar Daddy ga baki ɗaya Tareeq ya daina fitar dare iyakanci ya je ball mestry training, kafin magarib ya dawo kuma shikenan ba zai sake fita ba yana tare da Daddy shiyasa ko Ummi ta yiwa Daddy ƙorafi akan fitar dare da yake yi sai ya ƙaryata domin idan, yana gari wata kalar natsuwa Tareeq ke yi har wani ladabin kare yake ƙiƙƙira duk abunda za ka faɗa akanshi Daddy ba zai taɓa yarda ba.

***********

*LATE ALHAJI ABDALLAH SARAKI MANSION*

Tun lokaci da Mahmood ya baro wurin aikinsa ya tare kacokan ɗakin Taheerah sallah kaɗai ke fitar dashi gidan. Taheerah garin ƙiriniyarta ta buge ciwo ta fara kuka wani lokaci har tayata yake yi, wannan so ƴaƴa na Mahmood Saraki yana tsorota Umma ko a tarihi bata taɓa gani uba dake da masifar son ƴaƴa irin Mahmood ba.  Ba yadda bata yi dashi ba akan ya koma gun aikinsa yaƙi wai jira yake sai an cire ɗori yaga yadda hannu Taheerah ya yi kafin ya koma. Ko yanzu lallaɓa ta yake yi akan za su je asibiti a duba hannun nata sai uwar shagwaɓa take zuba masa.

"Baby ki yi haƙuri mu je asibiti a duba ki kin ji??

Cuno ɗan ƙaramin bakinta tayi mai kama da gidan tsutsu "Abba daga asibiti za ka kaini wurin Ya Aabid na

ganshi??

"Aabid yana school Baby a dokar school ɗinsu ba a bari a gansu sai lokaci visiting, ki yi haƙuri idan lokaci zuwa ya yi koda ina Kaduna ne zan taho mu je tare."

Da kyar ta amince ya ɗauke ta suka fice kaitsaye get well woman and children health care suka nufa.

***********

Aayya ta fito cikin shirin tafiya asibiti gani likita kwana biyu tana fama da jiri da ciwon kai a main parlor ta, tarar da Fadila da ke zaune tana jiran fitowar ta, ta rakata wannan umarni ne daga Daddy ba don haka ba, da ba idan za ta je bala'in haushin Aayya take ji shiyasa tun sanda saƙon ya riske ta ta raka Aayya asibiti take ci rai. A compound suka ci karo da Tareeq ya fito daga ɓangaren Daddy da car key a hannunshi "memory lost ina zuwa haka naga Feedy Baby sai kumbura fuska take yi da alama bataso raka ki."

Tareeq ya faɗa da salon haddasa husuma tsakani Aayya da Fadila.

Wata uwar harara Fadila ta maka masa cike da jin haushin suna da ya kira ta dashi sai kace wata sa'arshi, ta rasa wane kalar raini ne ya gama shiga tsakanin ta da yaranan.

"Wallahi bana so iskanci Tareeq sa'arka ce ni da za ki kira ni da wannan suna? Amma ba abin

mamaki bane don ka kira ni da gatsali idan aka yi duba da halinka na rashin girmama na gaba da kai." Aayya ta kalli Fadila ta taɓe baki kafin kuma ta ce

"Bari kawai Tareeq nima tun farko baso fita nake da Fadila ba ubanka ne ya haɗa ni da ita. Ai ni da nasan kana gida ba ka je makaranta ba da kai zan nema ka rakani."

"Ai ko yanzu za ki iya cewa ya raka ki, kin hutar dani da masifarki ta rashin dalili."

"Da kuwa na raka ki Aayya dan ni banida kamar ki a duk faɗin garinan. Zan iya sadaukarwa da komai nawa akanki."

Jin wannan magana ta Tareeq ya sanya Aayya ta sakar masa da murmushi ga baki ɗaya haƙora ta suka fito waje, kafin ta ce "Da kyau ɗan albarka amma me ya hanaka zuwa makaranta??"

"Aayya yau children day rana ce ta hutu."

"To madallah, ɗan albarka ke kuma wuce mu tafi ki kasa kin tsare tare da kashe kunne kina saurare abunda muke faɗa, Allah yasa magana ce da ta shafe mu ballantana mutum ya kwashe ya je ya kai wa uwarsa."

Fadila bata tanka ta ba, ta nufi wurin motarta tayi unlock ɗinta da key ɗin dake hannunta, don kawai Tareeq ya ƙara tulawa Fadila haushi yasa shi biyo Aayya ya buɗe backseat ita dashi suka kame "direba ja mota mu tafi."

Wannan kalma ta direba da Tareeq ya kira Fadila da ita yafi komai ƙona mata rai, saboda gudun fitina sai kawai ta danne ɓacin ranta, tasan halinshi ba abinda yafi so da ƙauna irin a ɗinga rigima dashi.

Duk kalar tsokanarta da yake bai sa ta kula shi ba har suka iso wurin da aka tanada saboda parking a asibitin Get well woman and children health care, kasancewar likita da ke duba Aayya yasan da zuwanta tun kafin su fito daga gida Imam Wali ya kira shi shiyasa kaitsaye suka shiga ofishin sa ba tare da jira ba. Suna shiga wayar Tareeq tai ringing sai da ya zaunar da Aayya akan kujerar gani likita kana ya fice daga office ɗin domin ya amsa kira da ake masa a waya.

Baƙuwar lamba ce ke kiransa sai da ya ja ɗan guntun tsaki yana ƙoƙari kiran number ɗin aka sake kira ya yi picking tare da ƙarawa a kunnensa na dama cikin zazzaƙar muryata tai mishi sallama bai amsa ba sai kawai ya zarce da tambayar "wacece?

"Nana Bashir ce.

"Nana Bashir?"

Ya faɗa fuskarsa cike da mamaki sai kuma ya yi ɗan guntun murmushi wanda bai wuce fatar bakinshi ba.

"Nana ya aka yi ne?"

"Lafiya ƙalau na kira ka ne just to say hi!

"Da gaske??

Tareeq ya tambaya saboda wannan sabon salon na Nana Bashir yana ɗaure masa kai tare da bashi mamaki.

"Eh! Amma ka yi haƙuri idan na tukura ma."

"Nevermind na gode da kulawa ki gaida gida."

Kafin ta sake magana ya yi hanging up.

Juyawa da zai yi da nufi ya koma office ɗin likita sai kawai ya ji an cukuikuye mishi wando jeans ɗin dake jikinshi cikin ƴar siririyar muryarta ta yara take faɗin "Yaya ka ɓoye ni banaso Abbana ya kaini wurin doctor allura zai min."

Kafin Tareeq ya juya yaga mai magana sai hango wani mutum yana sanye da brown shadda yana tafe da sauri tare da dube-dube hakan ya tabbatar mishi shi ne Abban wannan little brat ɗin mai neman mafaka a bayanshi, murmushi ya yi sa'ili da yaga mutumin ya zo ya gitta ta gabashi ba tare da ya kalle shi ba, bare yaga gun da yarinyarsa ta ɓoya. Farfajiyar asibiti ya nufa, ba tare da Tareeq ya juya ba ya saka hannunsa ya jawo yarinya sai kawai ya ji ta tsandara mishi mahaukaci ihu, da sauri ya sakar mata hannu ya juya gaba ɗayansa, pop da ya gani tun daga damtse hannunta har izuwa tsintsiyar hannunta ya gano hannun ta mai ciwo ne ya kama. Da sauri ya rage tsayin shi daidai da ita "Oh! Sorry kiddo ban san cewa hannunki yana da ciwo ba stop crying ko kina so Abbanki ya dawo yaga kina kuka yai min duka?"

Girgiza kai tayi tare da share hawayenta da ɗayan hannunta mai lafiya.

"Thats my kiddo.

"Hey! Don't call me with that name."

Yadda tayi magana cikin tsiwa har tana zare idanuwa kaman wata babba yai masifar ba Tareeq dariya, he is not friendly with kids amma wannan yarinya tai bala'in burge shi hannunta mai lafiya ya kama gami da faɗin "okay tell me your name.

"My name is Taheerah Mahmood Saraki.

"Wow nice name.

"Kai fa ya sunanka??

"Ni sunana T.....

"Taheerah!.

Muryar Mahmood Saraki da Tareeq ya tsikayi a bayanshi ya hana shi ƙarasa magana, da

sassarfa Mahmood Saraki ya ƙaraso bai bi ta kan Tareeq da ke tsaye riƙe da hannun ƴarsa ba sai kawai ya cire masa hannu daga riƙo da yai mata ya maye gurbin da nasa hannu "Baby heerah kin daga min hankali miyasa za ki gudu daga ofishin likita?"

"Abba na gayamaka banaso allura."

"Baby ba allura za a yi miki ba hannunki kawai za a duba."

"Banaso Abba ni ka kyale ni."

Tsintar kansa Tareeq ya yi da saka musu baki "Kiddo ki ji magana Abbanki mana ko ba kyau so ki zama yarinyar kirki?"

"Hey! Bana ce kadaina kirana da wannan sunan ba.

"Oh! Sorry my little princess."

Tareeq ya yi magana yana kama kunne hakan da ya yi ya ba wa Taheerah dariya, ta kama hannun Abbanta tana faɗi "Mu je Abba amma saboda wannan new friend ɗin nawa zan bi ka."

Sai lokacin Mahmoud Saraki ya ƙarewa Tareeq kallo wanda bai zai wuce sa'an Aabid ɗinsa hatta da tsayin su zai iya zuwa ɗaya nan da nan ya ji Tareeq ya burge shi saboda haka ya sakar masa murmushi "Thank you young man."

"You're welcome sir!

Tareeq ya yi magana tare da murmushi Taheerah ta kalle shi ta ce "See you later my new friend."

Dariya kawai Tareeq ya yi sai da suka bacewa ganinshi kamin ya koma ofishin likitan dake duba Aayya, bayan an kammala dubata aka rubuta musu magunguna da za su siya, akan hanyar su na komawa gida Fadila ta tsaya a wani katafaren medicine store Tareeq ya fita ya je ya siyo magunguna gaf da entrence Fadila tai parking Tareeq ya taimakawa Aayya ta fito suka shiga gida.

AFTER ONE WEEK

Tareeq ya fito daure da towel a ƙugunsa fitowar sa daga wanka kenan, yunwa yake ji sai ya ji ba zai iya tsayawa dress up ba ta corridor ya saɓa bi dan shiga part ɗin ummi anan ya biyo, a babban falo ya tarar da su Fadila suna kallo movie a television, ko kallon ba su ishe shi ba ya wuce zai shiga kitchen Zainab ta kalle shi tare da galla mai harara "Wai kai Tareeq miyasa kwata -kwata a rayuwarka ba ka da kunya? Na sha jin ummi tana ma warning ka daina shigo mata falo da towel da yake kunnen ƙashi ne da kai maganar fatar baki bata shigar ka ko?"

Kur Tareeq ya yi mata da idanuwa yana kallanta irin kallon nan na raini kamin ya ja guntun tsaki ya wuce  kitchen abinsa.

"Dan Allah Zainab ki fita sabgar wannan tsageran ko kin manta gargadin da Daddy yai mana

akansa kafin ya koma Abj?"

Baby tayi magana tana yatsine fuska.

"To shikenan sai a zuba masa ido ya dinga shukawa mutane rashin mutunci?"

A wannan karon Fadila ce tai magana cikin yanayi na takaici.

Tareeq ya debi abinci ya fito rike da plate dai-dai sanda Zainab tana cewa "Dallah! Kalli yadda yake wa mutane yawo a gida da guntun towel kuma idan kika bincika ko boxer babu a jikinshi marar kunya kawai."

Sai da Tareeq ya kawo gaf dasu ya tsaya anan tsaye ɗin ya fara cin abincinshi  yana sauraren duk abun da kowacce su take faɗa.

"Ai ɗan iska ne bashida kunya ko tsirara zai iya yawo."

Cewar Fadila tana wulga mai mugun kallo.

"Ko yanzu ya Fadila miye bambancin shi da wanda ke tsirara?"

Ita dai baby tun sanda tai magana sau ɗaya bata sake tsoma musu baki ba hakikanin gaskiya ta tsorata dashi tun sanda ya sakata jinyar nonota take taka tsantsan dashi.

Murmushi mugunta Tareeq ya yi yana faɗin "Zee kika ce ni da wanda ke tsirara duk ɗaya ne ko? kuma kika ce idan aka bincika banida boxer?"

"En! Na faɗa ɗin ko kana da bambanci ne da wanda ke tsirara?"

"Muna da tun da ni ina daure da towel amma bari na cire towel ɗin tun dama a tsirara kuke kallona, dan haka banga amfani towel ɗin ba."

Ko kaɗan basu taɓa kawo tsageranci Tareeq ya kai ya yi complete naked a gabansu ga mamakinsu sai kawai ganin suka yi ya janye towel ɗin jikinsa ya rataya a wuyansa, a lokaci guda sun ka kurma ihu tare da mikewa da gudu suka fice waje suna cigaba da ihu da kururuwa Tareeq ya kece da dariyar keta ya juya da sauri ya nufi corridor kada ummi ta fito ta ganshi.

"Kanana 'yan iska kawai da ku tsaya na nuna muku ƙarya iskanci.

A tsorace ummi ta fito Gifty na biye da ita a baya.

"Ke Fadila lafiyarku kuwa kuke wa mutane ihu?"

Ummi tai magana sa'ilin da Fadila ta leƙo da kanta cikin falon ta gani ko Tareeq yana nan.

#JeeddahaAliyu

#Tareeq

#Daddy

#Ummi

#Fadila

#Zainab

#Baby

REMAIN ONE-TWO FREE PAGES SU KARE GA MAI SHA'AWAR CIGABAN WANNAN LITTAFI ZAI BIYA ₦700 TA WANNAN ASUSUN BANKI 7032566172 HAUWA SHEHU OPAY SHAIDAR BIYA TA WANNAN LAMBA 07032566172

[7/6, 7:24 AM] Hauwa Shehu Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

019.

Cikin haki Baby ta ce da ummi "Ummi Tareeq ne ya....

"Ya isa baby!"

Ummi tai saurin katse ta a tsawace kana ta cikin ɓacin rai ta cigaba da cewa "Sau nawa zan gargade ku da ku daina kawo min ƙarar Tareeq?" Miyasa ku ka kasa fahimtar hali da kuke jefa ni a duk sanda ku ka faɗi wani mummunan abu da ya aikata?"

"Ki yi haƙuri Ummi."

Kusan a tare suka haɗa baki waje bata haƙuri su ka bi ta kusa da ita sumui-sumui suka koma ciki falo, Ummi ta ja guntun tsaki ta koma falonta. Cike da tu'ajjabi suka sake maimaita zance a tsakanin su suna ƙara mamakin zallan rashin kunyar Tareeq.

Tareeq yana kammala ci abinci ya shirya cikin ƙanana kaya blue jeans da white shirt ƙafarsa sanye da white trainers ya ɗora farar p-cap akansa, shigar ba ƙaramin kyau tai masa ba, sai zuba ƙamshin tsadadddun turaruka Daddy yake yi. Ya fito dauke da plate ɗin da ya ci abinci yana shigowa babban falo duk wacce tai masa kallo ɗaya sai ta kauda fuska tana tuna yadda

suka gansa ɗazu, shi kan ko a jikinshi ya wuce su ya shiga kitchen ya ajje plate ɗin ya fito, yana tafiyar ƙasaita ya yi ficewarsa da kallo suka bi shi kamin Zainab ta ja tsaki tana faɗin "wallahi ban taɓa zaton iskanci Tareeq ya kai har haka ba."

"Nima haka."

Baby ta faɗa tana girgiza kai.

Fadila ta karɓe zance da faɗin

"Ni kam ban yi mamaki ba domin daga kallon idanuwanshi zai aikata fiye ma da hakan. Bakwa gani idanuwanshi a tsatsaye kamar nonon maza ai alama ce ta rashin kunya."

Kai tsaye parking lot Tareeq ya nufa sai da ya zaɓi ɗaya daga cikin tsadadddun motocin Imam ya hau ya fice daga gidan,yana fitowa ya ga Nana tsaye rakube a jikin bango jikinta sanye da uniform ɗin islamiyya kamar a tsorace take dan sai kalle-kalle take yi kwata-kwata babu natsuwa a tattare da ita, kallo ɗaya yai mata ya ɗauke fuska ya wuce ta kamar wanda aka yiwa dole ya kalleta ta jikin front mirror ya hango tana ɗaga masa hannu alama ya tsaya. Mamaki ne ya kama shi har yana tambyar kanshi me Nana ke nema gunshi da take tsayar dashi, ya taka birki da gudu ta zo ta buɗe front seat ta shiga jikinta sai rawa yake buɗe da baki yake kallonta yana jira ƙarin bayani dalilinta na tsayar dashi har ta shiga mai mota.

"Tareeq please ka ja mota mu bar unguwar nan banaso a gan mu tare aje a faɗawa mamana."

Bai ce komai ba ya ja mota ɗin sai da suka bar unguwa kafin ya kalle ta yaga sai murza zoben hannunta take yi ya maida ganinsa akan driving cikin daurarriyar murya ya ce da ita "Wai ke me kike nema a wurina? ko so kike mamanki ta sake zuwa gidanmu tai mana tijara?"

"A'ah! Ba haka bane slugger kawai....

"Dallah ya isa Nana idan ba haka bane to uban me kike nema a guna?"

"sonka nake yi Tareeq!

"What!

Ya faɗa da ɗan ƙarfi tare da gangarawa gefen titi ya yi parking cike da masifa ya daka mata tsawa "Kin yi hauka ne? ko kuma dai wani tarko kike so ki ɗanna min?"

"Ba ko ɗaya Tareeq ni kaina bansan yaushe zuciyata ta kamu da mugun sonka ba dan Allah ka amince da soyayya ta."

Ta karasa magana tana rausayar dakai irin ya ji tausayinta ɗinan, mamaki sosai ya cika Tareeq sai famar kallanta yake da baki buɗe, batare da yace da ita komai ba ya fita daga mota ya buɗe bangaren da take "Get out of my car."

"Please slugger don't do this to me I love you I mean it."

"Get down of my car Nana Bashir kamin hakurina ya ƙare nai mugun wulakanta ki anan wuri."

"Slugger...

Kafin ta karasa fadar abun da taje faɗa yai bala'i fizgota daga cikin motar ya watsar da ita tai mummunar faduwa har sai da goshinta ya bugi gefen kwalta, ya shiga mota yaja ta da wani irin gudu yabar wuri.

SARAKI MANSION

Taheerah ce a falon ke wasa sai hawa kujeri take tana tsalle idan ta hau wannan sai ta dira akan wannan mai aikin Hajiya Salma sai magana take mata akan ta daina kada ta fama ciwo ta, amma kamar tana zuga ta ne. Taheerah yarinya ce mai yawan kiriniyar gaske kwata-kwata bata iya zama batare da tai tsalle-tsalle ba shiyasa kullum cikin ji wa kanta rauni take. Hajiya Salma dake ɗakinta tana sallar magariba tana ji yadda, Rabi mai aiki ke fama da ita. Dan haka tana sallame sallah ko addu'a bata tsaya yi ba ta dau casbinta ta fito tana zuwa ta dubi Taheerah ta lafta mata casbin, a duwawu wani irin ihu Taheerah ta fasa saboda casbin ya shige ta ba kaɗan ba Hajiya Salma ta fizgota, ta dankwarar da ita ƙasan rugs cikin faɗa take magana "Zaune nan dan ubanka yarinya kin bi ki fitine mutane da kiriniya ke ba halin ki zauna ki natsu wuri ɗaya."

Taheerah ta buɗe baki tana kuka sai sosa bayanta take idan Hajiya ta buga Mahmood yana dunfaro cikin gida ya fara jin sautin kukanta da gudu ya karaso jikinsa na rawa "Subhanalillah! Hajiya me take wa kuka ko hannunta tasake bugewa?"

Malalacin kallo Hajiya tai masa kafin taja guntun tsaki ta nufi kujera ta zauna ta cigaba ta jan casbinta. Mahmood ya durkusa gaban Taheerah ya jawo ta jikinshi yana shafa bayanta "ya isa baby heerah daina kuka ki gayamin menene ko hannun ne mu koma asibiti?"

Cikin muryar kuka take cewa "Abba Hajiya ce ta doke ni da casbinta."

Daga ji yadda take magana kasan yarinyar a sangarce take nan take Mahmood ya ɓata rai yana kallon Hajiya, wacce ta galla mai muguwar harara tana faɗin "Da ka juyo kana kallona za ka rama mata ne?" Sha-sha-sha wofi mai masifar son ƴaƴa yarinya ta bi ta sangarce sai rashin ji tsiya ka yiwa kanka faɗa Mahmood Taheerah mace ce duk dare dadewa gidan wani tayi dole sai ana tsawata, wannan riritawa da kake mata ya yi yawa hakan kuma zai iya taɓa tarbiyyar ta."

Tun sanda Hajiya Salma ta fara magana Mahmood ya dauke kanshi ya mayar kan ƴarshi yana shafar ta ita kuma ta lafe a jikinshi tana kanana kukanta mai cike da zallar shagwaba, wannan dukan da Hajiya tai wa Taheerah ba ƙaramin zafin shi Mahmood ya ji ba, dan shi ko kaɗan bai san abun da ya taɓa mishi ƴa duk duniya hajiyarsa ita kadai ce keda wannan zarar ta dukan yaranshi yanzu haka ya hana akai Taheerah gidansu Layla tun sanda ta taɓa zuwa gidan ana gobe za a fara azumi an kawo wa mahaifiyar Layla Hajiya Turai cefanen azumi,Taheerah ta shiga store ta fasa musu kiret uku na kwai, ai kuwa Hajiya Turai ta zane ta, Taheerah ta dinga kuka har zazzaɓi ya kamata sai taki bacci sai sunan Abbanta take kira, dole Turai tasa aka maidata, Taheerah ta kwashe tsaf ta gayawa Abbanta Hajiya Turai ta doke ta akan ta fasa kwai,

bawan Allah nan ya dinga faɗa har sai da zage-zage tun daga sannan ya soke zuwanta gidan sai dai Aabid ya je idan ya zo hutun makaranta. Hajiya Salma tayi faɗa har tagaji ta zuba mai ido, dan ta fahimci idan akan ƴaƴanshi ne ba sauya wa zai yi ba.

Hajiya Salma ta cigaba yi wa Mahmood faɗa daga ƙarshe ta dawo nasiha tana ankarar dashi illar da ke tattare da wannan gata da yake nunawa Taheerah domin a gaba zai iya yiwa rayuwarta gibi,shi dai Mahmood yana jinta ne kawai dan bai ga dalili da zai sa ya daina ba dan kuwa soyayyar yaranshi a cikin jininshi take. Sai da Taheerah tai bacci sannan ya sami natsuwa ya dauke ta kaita ɗakinta ya kwatar da ita ya tofe ta da addu'a kana ya rage mata gudun Ac sannan ya dawo falo ya sami Hajiya yasa mai aiki ta kawo mai abinci yana cikin ci Hajiya ta dube shi fuskarta haɗe ta kira sunanshi "Mahmood!"

"Na'am Umma."

"Na gaji da maka maganar aure kana kawo min kabli da ba'adi shiyasa na yanke hukunci da nake gani shine daidai da rayuwarka. Ina so gobe kafin ka wuce Kaduna ka je gidan Alhaji surooj ka gana da Farha mun gama magana da hajiya Turai gara ta maye gurbin ƴar uwata, na tabbata ita kaɗai ce zata iya haƙuri zama da ƴaƴanka kasancewar ta ƙanwar mamarsu."

Mahmood ya ture plate ɗin abincinsa gefe ya tattaro hankalinsa kacokan kan Hajiya, yayin da fuskarshi take haɗe "Umma dan Allah ki yi hakuri da zance Farha kar fa ki manta ko bayan rasuwar Layla mahaifinsu da kanshi yai min tayin aurenta ban karba ba, saboda ina hango rashin dacewar Farha a gareni kwata-kwata bata cikin jerin mata dani Mahmood zan iya aura yanayin tsarin da take gudanar da rayuwarta basu yimin ba. Farha ta cika wayewa idanunta a buɗe suke kullum pictures ɗinta na kan social media, haka kwanakin baya naga ta yi posting wayansu hotunanta da shigar da bata dace ba wallahi kamar ba ƴar musulmi ba."

Murmushi Hajiya Salma tayi ta gyara zamanta ta fuskance da kyau, wai yau Mahmood ne ke fadar bayasan wayayyiyar mace ya manta da yarda ya auro Layla kawai dai bambancin kaɗan ne dan ita bata shigar banza. Dama tun asali haka tarbiyyar gidansu yake daga uban har uwar ƴan boko ne masu akidar Turawa duk wanda yasan ahalin Alhaji Sa'id yasa cikakkun wayayyayun ne da boko ta gama ratsu su. To miye abin mamaki dan Farha tayi shigar banza dan haka a gani Hajiya Salma ba hujja bace kwakwara saboda tana da yakini duk wacce ta aure Mahmood zamansu ba zai yi lasting ba saboda ƴaƴanshi gwada ya aure Farha ɗin ko ba komai ƴar uwar marigayiya matarsa ce. Duk kauce-kauce da Mahmood yake yi dan ya kaucewa auren Farha abun ya gaggara domin kuwa Hajiya ta kafe ba gudu ba ja da baya sai dai in bata numfashi. Dole washegari ya je gidansu Farha wacce dama ta daɗe tana danko sonshi tun kafin ya aure Layla bayan aurensu ne ta haƙura ba wai dan ta daina son nashi ba. Sun taɓa haduwa a gurin Dinner party ɗin abokin shi a lokaci shi ne babban abokin ango ita kuma babbar ƙawa kwatsam! Ta ganshi ya zo gidansu wurin Layla a lokacin har rashin lafiya sai da yi daga baya ta cire shi a ranta saboda ita mace ce da bata cika ɗora kanta damuwa ba. Saboda haka ta karɓe shi da hannu bibbiyu bai wani daɗe a gidan yai mata sallama ya wuce Kaduna.

******

Kai tsaye Tareeq ya wuce joint idan suka saba haduwa da Friends ɗinshi ba shi ya dawo gida ba sai around 12 lokacin kusan kowa dake gidan ya yi bacci sai securities dake tsaron gidan, su kansu suna mamaki yarda Tareeq yake fita yawon dare tamkar ba ɗa babban mutum mai babban muƙamin a gwamnatin ƙasa ba, shi ko tsoron masu garkuwa da mutane baya yi hankalinshi kwace ya yi parking ya fito daga motar yana ƴan wake-wakenshi ya nufi part ɗinshi da uncle Hamza yaci karo tsaye kallon da yake mai yasa shi saurin kauda fuskarsa ya yi kamar bai ganshi ba, ya bi ta gefen shi zai wuce a mugun fusace uncle Hamza ya ce "Kai daga ina kake a wannan tsohon dare?"

Cak! Tareeq ya tsaya yana sosa gefen kuncen shi, tare da kallon uncle Hamza a dage "Ba da kai nake magana bane?"

"Mamaki nake uncle me hadin ka dani da za ka tsayar dani kana min wannan tambayar ko Daddy ne ya ba ka gadina in sani?"

"Wallahi Tareeq kai wa kanka faɗa ka gina rayuwarka ta gaba,ƙaramin yaro dakai kana neman ka ɓata rayuwarka a wofi, duka yaushe aka haife ka da za ka fara bin mata ko ni da Jay har yanzu babu mai budurwa a cikin mu. Ka ji tsoron Allah ka gyara gobenka tun kafin lokaci ya kure ma."

Dariya Tareeq ya kwashe da ita yana faɗin "cabbb! Lallai baƙin jinin ku ya yi yawa uncle Hamza ace duk wadannan shekaru naku ace baku da budurwa gaskiya na tausaya muku."

Ya karasa magana yana dariya girgiza kai kurum uncle Hamza ya yi batare da ya tanka mai ya wuce abin shi Tareeq ya ja guntun tsaki tare da faɗin "wawa kawai duk ranar da kasake tsayar dani kai min wa'azi sai na lafta maka rodi a keya."

Uncle Hamza yana jin shi ya yi banza dashi Tareeq ya juya ya shige part ɗinshi.

Washegari

Fadila ce ke shirya Gifty cikin school uniform ɗinta, tana cikin saka mata safa Gifty ta ce "Yaya Fadila ni waye Babana dan Ya Tashh yace ba Daddy bane Babana ba?

Fadila ta ɗago ta dube ta da mamaki akan fuskarta "shi Tareeq ɗin ne ya gayamiki ba Daddy bane Babanki ba?"

"Eh! Kuma yace na daina amfani da sunan Daddy a school, ni dai yaya Fadila idan ina da Baba a mayar min da sunanshi banasan na Daddy Ya Tashh."

Ajiyar zuciya Fadila tai bata tanka mata ba ta cigaba da shirya ta, bayan ta kammala ta riƙo hannunta suka fito dining room suka nufa ta zaunar da ita ta haɗa mata tea da chips, ummi ta fito daga kitchen hannunta riƙe da lunch pack ɗin Tahreem Fadila ta gayamata abun da Tahreem ɗin ta gayamata, yanayin fuskar ummi ce ta canza ta ajje lunch pack ɗin akan dining kafin ta ce "Ai tuntuni Tahreem ta gayamin."

"Amma ummi shine ba za ki dau mataki akan shi ba,tun da yafara da haka ba zai kyaleta ba, ya dinga bullying ɗinta a school kenan ya hana ta concentrating karatu, ko taji ta tsani school ɗin."

Cikin damuwa ummi ke faɗin "Fadila sai kace kin manta da waye Tareeq idan ma nayi magana ba abun da zai fasa ya riga ya gama raina ni duk abun da zan yi ba fasawa zai yi ba sai dai in canza mata school ɗin zan yi."

"A'a ummi ba sai kin canza mata school ba kawai idan yasake ki je school ɗin ki kai report wa school authorities kin ga su zasu kira Daddy su gayamai."

"Allah ya kyauta."

Ummi ta faɗa tana ji wani kunci a kasan zuciyarta.

Tareeq ya kammala shirin sa cikin uniform ɗinshi jiya da yunwa ya kwana dan haka yana gama shirya wa ya fito rataye da backpack ɗinshi a kafada ya shigo bangaren ummi, yana hango ummi da Fadila a dining room ya haɗe fuska ya nufi cikin falo ya ajje backpack ɗinshi ya dawo dining room ɗin sai lokacin ya gaida ummi tamkar bayaso Ummi bata amsa ba sai kawai tasakar mai muguwa harara,tea ya haɗa ya ɗebe chips kaɗan a plate ya ja kujera ya zauna zuciyar Ummi sai tafarfasa take tsabar haushin sa dake ji sai kawai ta bar dining room ɗin ta shiga kitchen. Fadila ta kalle shi a fusace tana faɗin "Nikam Tareeq uban me ka taka ne da ba za ka gaida mutane ba?" Tsakanin nida ummi waye sa'an ka?"

Bai tanka wa Fadila ba sai kurum ya shiga cikin abincinsa sosai Fadila ta harzuka "To bari ka ji daga yau mai kama da rana ta yau kar ka sake tare Gifty a school kai mata magana akan sunan Daddy da take amfani dashi idan hakan na damunka, ka je ka sami Daddy domin shine yasaka mata sunan shi ba dan batada uba ba."

Still bai ce da ita uffan ba Fadila ta ƙara hasala dan so tai ya tanka ta, ta sami damar wanke mai fuska da mari.

Fadila ta cigaba da fadar "Ɗan iska yaro marar mutunci ka zauna bakada aiki sai zaluntar marainiyar Allah har kana neman ka hana ta karatu saboda kai daƙiƙi ne ko?"

Kiranshi da suna daƙiƙi da tai ne ya bata mishi rai dan baya da niyar kulata "Wai duk saboda wannan mai jan gashi ne kike zagina yaya Fadila har da kirana daƙiƙi?" To wallahi kin siya mata masifa dan sai na nuna miki asali daƙiƙanci."

Ya karashe magana yana ƙwafa

Tahreem tana ji ya kirata da sunan da bataso tai rau-rau da idanu tanasan tai kuka da sauri Fadila ta jawo ta jikinta tana harara Tareeq Ummi dake kitchen tana ji duk abun da yake faɗa furucin shi yasata fitowa ranta ɓace ta ce "Kar ka fasa Tareeq ka cigaba dama kai ba wanda ya isa dakai ba a isa a faɗa ka ji ba amma kasani duk ranar da kasake tare Tahreem a school ta dawo ta gayamin wallahi-azim za ka sha mamaki irin abun da zan ma a gidanan ba dai takamar

ka tsageranci ba....

"Wai meke faruwa ne Ummi?"

Muryar Jabeer ce ta katse wa ummi faɗa da take Jabeer ya karaso cikin dining room ɗin sai lokacin yaga Tareeq tun kafin ummi ta bashi amsa ya gano dalilin faɗa nata.

Cikin fushi Ummi ta dube Jabeer tana faɗin "Jabeer kamar Tareeq ace yana neman ya gaggare ni yafi karfina na rasa yarda zan tankwara shi kullum da kalar baƙin ciki da zai kunsa min, haka jiya sai cikin dare ya dawo gidanan. Na gaji da baƙin ciki da yake kunsa min wallahi ina gaf da barin gidanan."

Ummi ta karasa magana hawaye na bin kumatunta, tana ji takaici wannan rayuwar da Tareeq ke yi.

Ummi ta juya rai ɓace ta bar cikin dining room ɗin ta nufi bedroom Jabeer da Fadila suka bi ta da kallo zuciyoyin su na musu zafi idan da akwai abun da suka tsana bai wuce su ga ummi cikin damuwa ba.

"Wai me ya faru ne feddy?"

Jabeer ya faɗa yana kallan Fadila da damuwa akan fuskar shi, sai da Fadila ta sauke numfashi kafin ta shiga bashi labarin abubuwan da suka faru sanda baya nan daga ciki har taɓa Nana Bashir da Tareeq ya yi Fadila tana zuwa gun Jabeer ya zazzaro idanuwa da baki buɗe yake kallan Fadila "Amma feddy miyasa ba ku gayawa Daddy ba? Wannan zuba ido da ake wa Tareeq bai kamata ba, tun da har yana tsoron Daddy gwada yasan abun da yake aikatawa sai ya dauki mataki icce fa tun yana danye ake tankwara shi idan ya bushe sai dai ya karye."

"Ya Jay kenan kamar ka manta da waye Daddy ko?" duk abun da Tareeq keyi ko an gayamai ƙaryatawa yake yi ya kuma rufe idonshi yaci wa mutum mutunci,nikam nagaji da kai mai ƙara dan rashe ne kawai ke juyewa da mujiya, yaje ya cigaba da iskancin shi duniya ce zata koya mai hankali. Ni dai abun da nakeso dashi ya fita sabgar Gifty ba ruwan shi da ita tun da ba zamanshi take a gidanan ba."

Sosai Tareeq ya fusata da maganganu da suke mai sai cika da batsewa yake ya ture kujerar da yake zaune ya tashi cikin fushi ya buga tea mug ɗin dake hannunshi a tiles tea ɗin ya fallasa wa Fadila da Jabeer a jiki tsabar fushi da yake ciki ya kasa magana sai kawai ya nuna su da yatsa tare da kiyasta yatsun sai kuma ya yi ƙwafa juya zai bar cikin dining din shi ma Jabeer cikin fushi ya taho ya fizgo collar rigar shi ya jawo shi da ƙarfi "dan ubanka ba inda za ka je dawo nan ɗan iska yaro ana magana za ka tafi wato kayi ƴan iska damu kai burinka kullum ka dinga musguna wa mahaifiyar mu ko?"

"Shi ai bai ɗauki Ummi a matsayi mahaifiya ba saboda baya gani girma da darajar ta hatta da ƴan aikin gidanan suna martaba ta, amma ban dashi da haihuwar irin Tareeq gwada barinsa marar amfani kawai."

Fadila ta faɗa tana ji kamar ta rufe Tareeq da duka. A hasale Tareeq ya dube Jabeer yace "Cika min collar riga Jay."

"Idan naƙi fa? Ko yau ma za ka buga min jack ne?"

"Fiye da hakan ma zan yima."

Tareeq yana rufe baki Jabeer yana sakar mai mari.

#Rigima

#Yan uba

#Nadama

#soyayya.

REMAIN ONE-TWO FREE PAGES  SU KARE GA MAI SHA'AWAR CIGABAN WANNAN LITTAFI ZA KU BIYA ₦700 TA WANNAN ASUSUN BANKI 7032566172 HAUWA SHEHU OPAY SHAIDAR BIYA TA WANNAN LAMBA 07032566172

[7/6, 7:24 AM] Hauwa Shehu Aliyu: TAREEQ IMAM

Na

Jeeddah Aliyu

Arewabook@jeeddah3256

020.

Sosai marin ya shige Tareeq ya ratsa mai ƙwaƙwalwa a rikice ya dafe kuncen shi, ya daɗe dafe da kumatu kafin ya ɗago idanuwanshi ya ware su akan fuskar Jabeer take mai kaskantaccen kallo wani irin tukuki takaici Tareeq ya ji a zuciyarshi cikin zafin rai ya furta "Ni za ka mara Jay?"

"An mare ka ɗin ko za ka rama marar kunya kangararren wofi?"

Hannu Tareeq ya ɗaga zai rama marin shi ya ji ta bayanshi an riƙe mai hannu ya juya a fusace, Zainab ce ta riƙe shi wacce shigowar ta kenan daidai ya ɗaga hannun zai mari Jay shine tai

saurin riƙe mai hannu, a fusace ya fincike hannunshi ya yi kanta zai kai mata duka Jay ya tare dukan ya sauka a ƙafadarshi ya daddage ya daki ƙirjin Tareeq da ƙarfi da dukkan hannayen shi, har sai da Tareeq ya yi baya kamar zai faɗi ƙugun shi ya buge dining table sosai ya ji zafin buguwar ya wawuro kwalbar ketchup ya jefa wa Jay ya tare da hannunshi, kwalbar ya fadi ya tararratse ketchup ɗin ya malale a tiles, cikin fushi Tareeq ya ke faɗin "wallahi yau sai ka yi danasani marina Jay sai na wulakanta ka angolan banza angolan wofi wadda ubanshi ya mutu bai bar mai komai ba sai gadon tsiya da talauci ba da....

Kafin ya karashe magana Jay ya kai mai naushi a hanci nan take nose bleeding ya ɓalle mishi, Fadila ta ce da Jay "Kar ka kyale shi Ya Jay cigaba da dukan dan iska har sai ya yi laushi."

"Yo dama karya iskanci yake yi."

Zainab ta faɗa tana ji farin ciki yarda Jay ya fasa wa Tareeq hanci ko ba komai yau ta huce takaici karya mata hannu da ya taɓa yi. Cikin baƙar zuciya Tareeq ya dau kujerar dining ya bugawa Jay shima ya dauko tashi kujera ya buga mai daga nan kazamin dambe ya kaure a tsakaninsu sai buge-buge da fashe-fashe suke yi duk abun da suka dauko su bugawa juna duk sun jiwa kansu rauni musamman Tareeq yafi bugawa saboda Jay yafi shi ƙarfi, ƙarar fashe-fashe da iface-ifacen su Fadila ne ya fito da ummi da Aayya sai kuma Baby da take bacci, gani abun da ke faruwa hankalin su ya tashi ga Tareeq sai zagin uban Jay yake yi abin da ke ƙara fusata Jay kenan "Na rantse yau sai ka bar gidanan tun da ba gidan ubanka bane,koda yake ubanka da ya mutu bai bar maka gadon gida ba shiyasa ka zo ka tare mana a gida kana angola wulankatacce you're trying to compare yourself with me."

Jay ya sake fusata saboda ya tsani ya ji Tareeq yana zaga mai mahaifi.

Aayya tana gani yadda Jay yai wa Tareeq rauni jikinshi duk jini ta ɗora hannu aka tana kurma ihu, a fusace Ummi ta daka musu tsawa tana faɗin su bari, sai dai ba wanda ya ji ta sai ƙara raunata junansu suke duk yarda ummi taso raba su ta kasa sai ma ƙoƙarin raunata ta,suke yi Fadila ta jawo ta gefe tana faɗin "Ummi dan Allah ki jaye kada su miki rauni ke Zainab kira securities."

Zainab ta ruga ta kira su suma sai da suka rirriƙe Tareeq saboda shi Jay Ummi tayi mai magana ya daina Tareeq ne ya kafe, dan sai auna wa Jay mummunan zagi yake Baby ce ta kama hannun Jay ta nufi ɗakin Ummi dashi wani zagi da Tareeq ya surfa wa Jay ya harzuka Ummi tayi kanshi ta rufe shi da duka da zagi

"Kai wani irin kangararren yaro ne Tareeq? A kodayaushe burinka ka kasani ɓacin rai kai jarabta ce babba acikin rayuwata haihuwar ka bata amfana min komai ba face baƙin ciki da takaici."

Ummi ta karashe magana tana rushewa da kuka baƙin ciki Tareeq ya ishe ta ji take tamkar ta buɗe ido ace ba ita bace ta haife shi. Cikin baƙar zuciya Tareeq ya dubi ummi ya ce "Tun da bani amfani Ummi ki kashe ni ki huta,da wannan tsanar da kike min gwada ki kashe ni. Ki kashe ni Ummi sai ki huta da baƙin ciki da nake sa ki, nace ki zo ki kashe ni Ummiiiiiii!"

Ya yi magana cikin ihu da karaji wanda hakan ya tunzira Ummi ta dauko flower vase tayi kanshi

da sauri ɗaya daga cikin securities ya riƙe vase din ya yi da daya ya dakawa Tareeq tsawa yana zare mai ido "Ka natsu Tareeq ka dawo hayyacinka kasan da wacce kake magana, kada rudin kuruciya ya rude ka, ka ɓata gobenka a wofi, uwa ba wasa bace ka ji ko?"

Ya yi magana yana kama collar rigar Tareeq ya girgiza shi da ƙarfi. Aayya ta zo da sassarfa tana kuka tana furta

"Innalillahi wa'inna illaihim raji'um! Da gaske dai Amina so kike ku ga bayan Tareeq ke da ɗanki to wallahi duk abun da ya same shi ki shirya shari'a da ubanshi saboda daga ke har ɗanki ba kyale ku zai yi ba, ki daina gani ke ce kika haife shi shari'a ba ruwanta da wannan."

Kuka sosai Ummi take yi wanda ya jawo Asthma ɗinta ya tashi numfashinta ya sarke Fadila da Zainab hankalin su ya tashi da gudu Fadila ta je ta dauko mata inhaler, ita kuma Zainab ta je ta kira mommy tun da Tareeq yana jin maganarta zuwanta yasa securities suka sake shi ta umarce su da su koma bakin aikinsu,

mommy ta rungume Tareeq a jikinta tana bubbuga gadon bayanshi, shi kuma sai hucci yake yi yana jan ajiyar zuciyar kamar wadda yaci kuka alhali ko digo hawaye bai zuba daga idonshi ba tsabar baƙar zuciya ce ke cin sa.

Numfashin Ummi yana dawowa daidai ta bar cikin falon mommy ta ja Tareeq zuwa ɓangaren ta Aayya ta bi su tana sharar hawaye, Mommy ta kira family doctor ɗinsu ya zo ya yiwa Tareeq treatment cuwuka jikinshi.

Aayya tai ƙoƙarin kiran Imam Wali ta gayamai mommy ta hana ta dan ita ta ba wa waya wai ta kira mata Imamu ya yi maza ya dawo tun kafin Ummi ta kashe mai magaji, sai kumfar baki take mommy ko sai famar rarrashinta take yi "Haba Aayya! Wannan bai dace ba, ba girman ki bane ace duk abun da ya faru a gidanan ki buga waya ki gayawa Alhaji, silar wannan abun da kike yi duk shi ne yake ɓata zaman su ya ƙara hassassa rashin jituwa a tsakanin Alhaji da Amina. Daga Alhaji har Amina naki ne idan aurensu ya yi daɗi za ki fi kowa farin ciki haka zalika in ya ɓace za ki fi kowa shiga baƙin ciki. Da tun farko ba ku cilaswa Amina auren shi ba, da duk wannan bata faruwa ba. Shi fa aure ibada ne kuma ana yin sa ne domin samun natsuwa da kwanciyar hankali. Idan aka rasa wadannan abubuwa guda biyu babu ta inda za a ji daɗin zamantakewar aure."

Jikin Aayya ya yi sanyi ta nemi wuri ta zauna tare da rafka tagumi ita kanta bata ji daɗin yanayin zaman Amina da Imam sai dai ta rasa ta ina zata fara magance wannan matsalar.

A wannan ranar daga Tareeq har Tahreem basu je school ba, har dare Tareeq yana ɓangaren mommy ta killa ce shi ta hana shi fita saboda tasan halinshi tun daga yarinta fadanshi baya mutuwa yana iya zuwa ya sake tada sabuwar fitina. Anan ƙaramin falonta ya yi bacci gani ya yi bacci yasa Aayya ta koma bangaren Ummi. Sai around 2 ya farka mommy ta zuba mai abinci yaci kadan ya sha magani sannan mommy ta tattaro hankali da natsuwarta wuri guda ta kalle shi tare da kiran sunan shi "Tareeq!"

"Na'am mommy!"

"Ina so ka bani aron hankalinka ka buɗe kunnuwanka dakyau ka saurare ni azahirin gaskiya abin da kake yi ba daidai bane, Ummi mahaifiyarka ce ita ce tai kayan cikinka har ka zo duniya to ashe kuwa ta cancanci girmamawa daga gareka.

Ubangiji da kanshi ya umarci a Kyautatawa Iyayaye (Musamman Uwa) ko acikin Al-Qur'ani, mai girma Allah (SWT) yana cewa

"Mu ce wa dan Adam ka gode wa Ubangijinka da iyayenka. Mahaifiyarka ta ɗauke ka cikin wahala har zuwa lokacin shayarwa."

(Suratul Luqman: 14)

Wannan yana nuna yadda Musulunci ke girmama uwa bisa wahalar da ta sha wajen daukar ciki, haihuwa da shayarwa. Haka zalika Annabi (SAW) Ya Faɗa sau uku a girmama Uwa

Wani sahabi ya tambayi Annabi (SAW) Wa ya fi cancanta da a kyautatawata?"

Sai Annabi ya ce

Uwa.

Sai sahabin ya ce

Sannan wa?

Annabi yasake ce mishi Uwa

Sahabi ya sake tambayar shi Sannan wa? a takaice sai da Annabi ya ambaci uwa sau uku kafin ya ce Uba.

(Hadisi ne a cikin Sahih Bukhari da Muslim)

Wannan hadisin yana nuna cewa uwa ta fi uba sau uku wajen cancantar kyautatawa. Ina kawo maka waɗannan misalai ne domin kasan irin girman da Allah subhanahu wata'ala ya yi wa uwa domin ka gyara alakar ka da mahaifiyarka. Kasani Tareeq Aljannarka tana Karkashin Sawun Amina.

Annabi Muhammad (SAW) ya ce

Aljanna na karkashin sawun uwa.

(Hadisi sahihi ne wanda ke nuna cewa kyautatawa uwa hanya ce ta zuwa Aljanna.)

Tareeq kula da uwa Ibada ce idan mutum ya kula da mahaifiyarsa, musamman a lokacin tsufanta, yana samun lada mai girma. Allah ya yi gargaɗi kan rashin kulawa da su, musamman lokacin da suka kai matakin tsufa

"Kada ka ce musu 'Uff!', kada ka yi musu ƙorafi, ka faɗi kalma mai kyau."

(Suratul Isra’i: 23)

Haka zalika uwa tana da matsayin da ba a iya kwatanta shi da komai a Musulunci. Ta cancanci girmamawa, soyayya, da kyautatawa fiye da kowa. Wannan daraja da Musulunci ya ba uwa na nuna girman rawar da take takawa a rayuwar ɗan adam da al’umma gaba ɗaya.

A addinin Musulunci, rashin girmama mahaifiya babban laifi ne kuma yana da matukar tsanani. Mahaifiya tana da matsayi mai girma sosai a Musulunci, kuma girmama ta wajibi ne. Rashin girmama mahaifiya yana daga cikin manyan kaba'ira (zunubai), kuma yana iya kai mutum ga fushin Allah. Kuma Allah zai iya hana wa mutum albarka ko nasara a rayuwa ina san kasani Tareeq rashin bin Iyayaye (musamman mahaifiya) yana haifar da fushin Allah. Yana iya kai mutum wuta idan bai tuba ba.

Idan mutum yana aikata hakan, wajibi ne ya tuba, ya nemi gafarar Allah, ya kuma gyara halayenshi da mahaifiyarsa tun kafin lokaci ya kure mai."

Mommy ta tsaya tana kallon reaction ɗin Tareeq sai taga jikinshi ya yi sanyi dan duk sanyi dake cikin falon gumi yake yi, which means nasihar ta ta shige shi saboda haka ta riƙo hannunshi cikin sigar rarrashi ta ce "zan je part ɗin Ummi dakai ka bata haƙuri kuma kada ka sake ka gayawa Daddy abun da ya faru ka ji Babana?"

Sai da Tareeq ya ja numfashi kafin ya gyada kai.

"Good bara na dauko mayafina mu tafi."

Mommy tayi magana tare da miƙewa ta wuce ɗakinta dake upstairs Tareeq kuma ya yi shiru duk jikinshi ya yi sanyi yana jin rashin kyautuwar abun da ya yi, haka mommy ta dawo ta sami shi duk ya yi wani iri ta kama hannunshi suka nufi ɓangaren Ummi.

A babban falo suka tarar da Ummi dasu Fadila Ummi tana gani Mommy ta shigo tare da Tareeq ta daure fuska har tai ƙoƙarin barin falon, cikin sauri mommy ta dakatar da ita "Dakata Amina! Magana nazo yi dake dan Allah ki dawo ki zauna."

Ambatar Allah da mommy tai yasa Ummi ta dawo ta zauna sai dai babu fara'a cikin fuskata, Fadila ta kalli Tareeq dake famar sunne kai ta tabe baki, Mommy ta zauna tare da zaunar da Tareeq kusa da ita cikin sanyi murya ta ce "Amina ga Babana yazo ya ba ki haƙuri sha'anin yara sai ana haɗawa da kai zuciya nesa kowanne yaro da nashi kalar kuruciya ki cigaba da yi mai addu'a watarana kamar ba a yi ba. Babana durkusa ka ba ummi haƙuri kai mata alkawari baza ka sake ba."

Tareeq bai yi musu ba ya sauko ya zube ƙasa ya buɗe bakinshi cikin ƙaramin sauti ba tare da ya kalli Ummi ba ya ce

"i am sorry Ummi ki yafe min."

Daga haka ya yi shiru yana ji wani daci a ƙasan zuciyarshi Ummi ta dube shi ta ɗauke fuska tana

ji wani sabon takaicin shi, mommy ta ce

"Amina ba ki ce komai ba?"

"Me kike so nace mommyn yara?"

"Ki ce kin yafewa Babana inshallah ba zai sake kwatanta laifi irin wannan ba."

"Faɗa kawai kike yi mommyn yara dan ki ji daɗin bakinki domin Tareeq ba zai taɓa canzawa ba. Dan ya bani haƙuri yanzu ba zai hana anjima ya sake aikata laifin da yafi wannan muni. Ai shi fitina a jininsa take idan kika ga bai yi ba mutuwa ya yi, Tareeq ya riga ya gama lalata tarbiyyarsa bana tunani zai gyaru."

"Subhanalillah! Amina idan fa hankali ya ɓata hankali ake sa wa ya nemo shi ire-iren waɗannan kalaman naki sam basu dace da uwa tagari ba, ai Allah keda shiriya ba mutum ba duk yarda kika kai ga san Tareeq ya gyaru idan Allah bai kawo lokaci ba duk tsana da tsangwamarki basu isa su canza komai ba. Ki dinga saita kalaman bakinki domin bakin uwa lalle ne."

Sosai Ummi ta ji ranta ya fara ɓaci har zuciyata tana kimtsa mata dan ba mommy bace ta haifi Tareeq shiyasa take kallon abun da yake a matsayin ba komai ba, cikin hasala ta kalli Tareeq ta daka mai tsawa "Kai! Tashi ka fice min daga falo banasan ganinka ko kaɗan tun daga lokacin da ka fara rarrafe na fara fuskantar kalubale akanka har kawo yau ɗinan da kake da shekaru goma sha biyar a duniya babu watarana da zata zo ta wuce ba tare da na kwana da bakin cikin ka me zai ayi da haihuwar yaro irin ka."

Tareeq ya ɗago idanuwanshi da suka yi wani irin bala'i ja yana kallon Ummi yana ji wani irin tukuki har yana ayyana anya kuwa Ummi ce asalin uwar da ta kawo shi duniya ahalin yanzu Ummi ta dasa mai kwankwato. Ya miƙe cikin wani irin yanayi ya fice Mommy ta bishi da kallan tausayi, tasani Tareeq baya ji magana taƙadari ne, na fitar hankali amma ba zai, zama hujjar da Ummi zata dinga nuna mai irin wannan matsananciyar tsana da tsangwama ba. Tareeq yana bukatar tallafin uwa wacce zata ja shi a jiki ta lurar dashi ta hanyar nasiha ba ta irin wannan hanyar da Ummi ta dauka ba. Cikin sanyi jiki Mommy ke magana "Ban yi mamaki da fitar irin wadannan maganganu daga bakinki ba Amina sai dai kisani kin yi kuskure mafi girma a rayuwarki, sai anan gaba za ki fahimci hakan. Uwa da kake gani Amina ginshiki ce muhimmi a tarbiyya da rayuwa yara, ko a cikin musulunci, uwa ita ce ginshikin gida, mai kula da tarbiyya, da samun lada mai yawa idan ta ciyar da iyalinta da niyya mai kyau. Zan iya cewa har da gudunmawarki a lalacewar tarbiyyar Tareeq saboda yawan jifar shi da kike yi da munanan kalamai."

"Dan girman Allah mommyn yara kada ki ƙara min ɓaci rai akan wadda nake ciki tun da har kina gani ni ce ban iya tarbiyya ba ki ɗauki Tareeq na ba ki, ki je ki tarbiyyantar dashi da taki kallar tarbiyya."

Ita ma Mommy cikin fusata ta miƙe tana cewa "Ke dai kina da baƙar zuciya Amina kuma wannan baƙar zuciya taki ita ce zata kai ki ga danasni kisani gyara kayan ka ba zai taɓa zama

sauke mu raba ba. Kuma kowa rai ya yiwa daɗi ba kamar mai shi idan Tareeq ya zama nagari sai kin fi kowa farin ciki haka zalika idan ya  lalace sai kin fi kowa baƙin ciki saboda jininki ne tsatsonki ne. Kuma daga yau ni Jamila ba zan sake yi miki magana akan ki gyara alakarki da ɗanki ba."

Ummi ta ƙara fusata ta miƙe suka shiga sa-in-sa dama Ummi bata iya fushi ba, ita kuma mommy bata ɗaukar raini nan take gida ya sake rikicewa su Fadila sai kuka suke yi sai da Aayya ta ja Mommy ta fitar da ita daga ɓangaren Ummi. Wannan abu da ya faru ya ƙara wa su Fadila tsanar Tareeq domin tun tasowar su basu taba gani hakan ta faru a tsakanin iyayen nasu ba. Duk da babu wata shakuwa a tsakaninsu amma suna zaman lafiya ba wacce ke shiga bangaren wata sai da babban dalili sai gashi yau a sanadin Tareeq kamar zasu doke juna.

*******

Sannu-sannu Nana ke rama a tsaye duk ta tsiyaya tamkar wacce ta kwanta jinya, tambayar duniya mama ta mata amma taƙi fadar abun da ke damunta sau biyu mama tana kaita asibiti iyakaci likita ya ce damuwa ce tai mata yawa da rashi bacci ga kuma ulcer. Da zarar Nana ta kwanta ba abun da ke mata shawagi a kwakwalwar sai abun da ya wakana tsakaninta da Tareeq, wannan abun ya kasa barin ta dan duk sanda ta tuna sai ta ji yanayin ta ya sauya ta ji tana kewar wannan abu ta rasa ina zata jefa kanta. Wata irin muguwar sha'awar ke damun ta wani lokaci har jiƙe wa take har sai ta canza underpants. Babbar damuwar ta bai wuce yarda Tareeq ya daina kulata ko a waya ta kira shi baya dagawa ji take kamar zatai hauka. Mama tayi faɗa har tagaji ta zuba mata ido.

A wani yammaci tana ɗakinta kwance akan madaidacin gadonta mai kalar light Pink ta lullube rabin jikinta da duvet mai taushin gaske, tun sanda ta dawo daga school take cikin damuwa saboda rashin gani Tareeq duk da baya kulata gani shi da take yi a class yana rage mata shauki da take ji akanshi.

Ta nisa a tunani har bata ji sanda mama ta shigo ba, tai tsaye gefen kanta tana kallonta tare da karantar yanayin ta, kafin taja gwaron numfashi ta zauna kan beside drawer cikin kakkausar murya ta kira sunanta

"Nana!

A birkice Nana ta kallo gefen da mama take sai kuma ta sauke ajiyar zuciya, cikin mutuwar jiki ta tashi zaune.

"Na'am Mama!"

"Matso nan zan yi magana dake kuma kisani this is the last time I'll ever speak to you after this, I won't talk to you again, sai ki je ki nemi wata uwa da tafi ni tun da ni ban isa dake ba."

Jikin Nana ya yi mugun sanyi ta matsa kusa da Mama cikin daurarriyar fuska Mama ta ce "Ɗago idanunki ki kalle ni."

Ba yadda Nana ta iya dole ta ɗago Mama ta ce "Me ke damunki?"

"Ba komai Mama."

Nana tayi magana cikin rawar murya

"Dan ubanki ki gayamin abun da yake damunki tun kafin na saɓa miki."

Yadda Mama ta bugawa Nana tsawa yasa ta ƙara rikicewa ta fara sakin siriran hawaye.

#Tareeq

#Nana

#Ummi

#Mommy

#love#hatred.

#07032566172.

ALHAMDULILLAH!! KARSHEN LITTAFI KASHI NA ƊAYA SAI MUN HADU DAKU A CIKIN KASHI NA BIYU. GA MAI MURADIN CIGABAN WANNAN LITTAFI ZAI BIYA 500 A MATSAYIN PROMO DAGA YAU 02 JULY HAR ZUWA 07 JULY TA WANNAN LAMBAR ASUSU 7032566172 HAUWA SHEHU OPAY SHAIDAR BIYA TA WANNAN LAMBA 07032566172.

1. Me ya sa Tareeq ke yin fusata da rashin ɗa ga mahaifiyarsa Ummi? Shin akwai wani boyayyen sirri wadda bai bayyana a gare su ba?

2. Ta yaya rikicin da ya faru tsakanin Tareeq da Jay da uncle Hamza zai kawo karshe?

3. Mene ne ra'ayin ka/ki game da yadda Ummi ta nuna tsana da tsangwama ga Tareeq? Shin wannan zai taimaka masa ko zai kara lalacewa?

4. Yaya kike ganin rawar da  Mommy (Jamila) take takawa a cikin wannan rikici? Shin maslaha take nema tsakanin uwa(Ummi) da ɗa,(Tareeq) mata (Amina) da miji(Imam) ko kuma wani abu daban?

5. Me zai iya faruwa idan Tareeq ya cigaba da nuna rashin ɗa ga mahaifiyarsa da kuma ƴan uwansa?

6. Me kuke tunani Nana ke ji game da rashin kulawar Tareeq gareta?

7. Shin Me kuke tunani zai iya jawo canji a halayen Tareeq? Shin zai kasance ne ta hanyar soyayya, ko kuwa wani abu daban?

8. Ga kuma labarin wasu iyalai a bangare ɗaya Mahmood Saraki da fitinanniyar ƴarsa, mai kamanceceniya da Tareeq, ita kuma me zai faru cikin rayuwarta?"

9. Shin Ummi zata yafewa Imam laifin da take ikrari ya mata?ya rayuwar aurensu zata cigaba da kasance? Ga kuma rikitacciyar tsohuwa Aayya a gefe tana jiran ko ta kwana.

10. Yaya kike jin wannan labari zai ci gaba a littafi na biyu? Me kike tsammani zai faru?

Duk amsoshi wadannan tambayoyi suna kunshe a cikin litaffi na biyu dan haka maza garzaya ki saka kuɗin ki, domin ji yadda zata kaya.

Jeeddah Aliyu

07032566172.